A Babban Gida Part 2 Complete Hausa Novel

By M Shakur

Language: English

Table of Contents

Soyayyanovels

PROLOGUE 3
PROLOGUE 7
PROLOGUE 10
PROLOGUE 13
PROLOGUE 16
ALMUNAUWARA ACADEMY 17
PROLOGUE 19
PROLOGUE 22
PROLOGUE 25
PROLOGUE 28
PROLOGUE 31
PROLOGUE 33
PROLOGUE 39
PROLOGUE 42
FLASH BACK ABATCHA ESTATE ABUJA 42
PROLOGUE 45
PROLOGUE 48
PROLOGUE 50
PROLOGUE 53
PROLOGUE 56
PROLOGUE 59

Soyayyanovels

[18/09, 6:55 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(It is a big house)_ ★TAKUN FARKO★ [Labari/Rubutawa] *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

_____°°°°°_____

__GABATARWA__ Bismillahir Rahmanir Raheem. Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah mamallakin Ranar sakamako, tsira da aminci su ƙara tabbata ga shugabanmu kuma masoyin mu Annabi Muhammad Sallallahu alaihi Wasallama, da iyalen shi da Sahabban shi, da duk wanda suka bi shi zuwa ranar sakamako. Ina ƙara gode wa Allah maɗaukakin sarki da ya bani ikon fara rubuta wannan littafi Mai suna “A BABBAN GIDA” ina roƙon shi da ya bani ikon gamawa lafiya ya kuma yafe min kuskuren da na tafka cikin labarin yasa yan uwa su amfana da shi. Ameeeen. Labari ne ƙirƙirarre, haka nan sunayen cikin shi ma ba a yi su dan cin mutuncin wasu ba, sai dai duk wanda wani ɓangare na littafin yayi daidai da rayuwar su sai su gyara kuskuren su da suka fahimta daga ciki. DIAMOND LADY

___SHIMFIƊA___ Littafi ne mai ɗauke da soyayya, cin amana, rashin tausayi, gwagwarmaya yan uwan taka, cakwakiya da kuma zanen ƙaddara.

___GARGAƊI___

Babban gida littafin mallaki na ne, ina da haƙƙi a kan shi saboda haka ban amince a karanta min shi zuwa audio ba sai da izini na, ban Amince wasu su haɗa min document ɗin shi ba. Takun farko garaɓasa ne, haka na biyu (ƙarshe) ya kasance na kyauta shima bisa sharaɗin samun comment, votes and shares har da reacting.. Comments ɗin ku kawai nake buƙata...domin shine ƙarfin guiwa tah.

___SADAUKARWA___

Dukka littafin Babban gida sadaukarwa ne gare ki Aishatu Usman (Baby UNA). Tabbas kin kasance ta musamman gare ni. Bazan taɓa mantawa da alkhairin ki gare Ni ba. Allah ya cika miki burukan ki baki ɗaya ya bar ƙauna

_____°°°°°_____

_____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ [Labari/Rubutawa] *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

*PAGE** 0 1

Wannan shafi naku ne masoya littafin _babban gida_. Ina ƙaunar ku loadi loadi. Ku ci gaba da kasancewa da alƙalamin DIAMOND LADY tare da comments. Barkan ku da Sallah.

SHARE AND COMMENT PLEASE _____★★★_____

Misalin ƙarfe goma sha ɗaya ne na safe (11:00am) yayin da hasken rana ya fito yayi ƙwal kasancewar yanayi ne irin na zafi da wuri rana take haskaka.

Ihun da naji yasa na nufi gidan domin ɗauko report.

Gida madaidaici ginin block, sai ƙofar ƙarfe me jan paint Wanda tsabagen dukan da ruwa ke mishi ya koma brown saboda tsatsa.

Mutane ne zaune a yar rumfar dake jikin gidan wacce aka kafa ta daidai bishiyar yandi dake wajen. Gabaɗaya kallo ɗaya zaka yi wa mutanen ka tabbatar ba na kirki bane don kuwa siffar su na ainihin bayyana ɗabi'ar su ta shaye_shaye ga kuma ihu da hayaniya da suke alamun wani musu ake bugawa.

Kai tsaye cikin gidan na nufa domin ganin su waye ke ihu, abun mamaki wata kyakkyawar mata ce wacce bazata wuce 32_34years ba tare da yarinyar ƴar kimanin shekaru 10years.

Jibgar su mutumin yake yi wanda kallo ɗaya zaka mishi ka tabbatar ba kan shi ɗaya ba kuma da gani mahaifin yarinyar ne wato mijin matar.

Ba ko ƙaƙkautawa kamar wanda aka bawa contract ɗin hakan yayin da Mamah babu abun da take sai hawaye.

Ita kuwa Zahrah bakin ta bai mutu ba yayin da shima yaƙi dakatar da dukan da yake mata.

“Wallahi ba zamu taɓa yafe maka ba, mugu kawai azzalumi”

Cike da mamakin ta mutumin wanda ba zai wuce shekaru 45years ba yake duban yarinyar baki buɗe. Ina da sabo ai ya saba da rashin kunyar Zahrah sai dai bai yi tsammanin ta kai har haka ba. Yanzu tsofai tsofai da shi ko kunyar shi ba zata ji ba take zazzaga mishi rashin kunya. (Ni Ko na ce ina tsufa a nan, bayan ko mutuncin kanka baka kama ba)

Ganin shirun nasa yayi yawa yasa ta goge hawayen da ke kan fuskar ta tana watsa wa mutumin kallon banza

“Wallahi Kawu ba zaka taɓa shiga aljanna ba in dai baka tuba ba, haka kawai bamu maka laifin komai ba ka kama jibgar mu, wallahi Allah sai ya saka mana...”

Bata kai ga ƙarasa abun da tayi niyyar faɗa ba taji an hanɓare mata baki, ba tayi mamaki ba saboda haka halin mamah yake sai kace damo, Gashi dai babu laifin da suka yi wa kawu yake dukan su, amma ta kasa yin komai, ita da take ƙoƙarin yi kuma an hanata.. wannan ai shi ne a dake ka a hana ka kuka.

“Ke Zahrah me yasa kam baki da hankali? Eyeh!! Ɗan uwan ubanki ne fa kike zagi” Ta faɗa tare da jan hannun Zahrah zuwa ɗakin ta.

Shi kuwa Kawu tsabagen mamakin Zahrah da ya cika shi bai iya taɓuka komai ba har sai da suka shige ciki sannan ya samu damar ficewa daga gidan yana mai nufar dabar su dake ƙofar gida ranshi a ɓace.

Hawaye na kawai ke zuba idon Zahrah yayin da Mamah ta ɗan murmusa tana jin takaicin irin halin da ta sanya kanta. A hankali ta fara magana cikin sassanyar murya wacce ke ɗauke da zallar sarewa..

“Haba Zahrah! Wai sai yaushe ne zaki sauya ɗabi'un ki?” Ta ƙarasa tare da bin ta da kallon tuhuma.

Tura ɗan ƙaramin bakin ta Zahrah tayi sannan ta kalli Mamah “Haba Mamah manah, wai sai yaushe ne zaki samu ƴanci a cikin gidan nan! Kin san dai Kawu ba ƙaunar mu yake yi ba kuma don meh zai ke dukan mu kamar wasu bayin sa, Ni wallahi Mamah ba zan ƙyale shi yayi ta zaluntar ki ba! Shine kawai. Ta ƙarasa tana gurmuɗa bakin ta tamkar tana gaban Kawu.

Jikin Mamah kuwa sanyi yayi da maganar Zahrah, Zahrah dai yarinya ce amma in ta zari magana ko wani babban iyakaci sai dai ba zata zuba mata ido ta lalata mata aure ba. Sam Zahrah bata da haƙuri ko na misƙala zarratin ammah ta ɗauki aniyar sauya ta da yardar Allah.

Bayan sun gama kukan su ne Mamah ta ƙara jan hankalin Zahrah kan rashin kirki da take tafkawa.

“zahrah'u ke har yanzu yarinya ce, ammah zan ci gaba da nuna Miki hanya saboda gaba, idan babu Ni zaki sha matuƙar wahala”

Zahrah da gabaɗaya ta ƙosa da zantukan Mamah yasa ta gyaɗa kai sannan ta miƙe ta nufi ƙofa.

“mamah nikam na tafi can gidan su Amira wasa na”

Mama dai da addu'a ta bi ɗiyar tata sannan ta tashi don ta kammala wankau ɗin da aka Kawo Mata zuwa yamma kuma zata wuce kasuwa.

★★★★★★

Ɓangaren kawu kuwa cikin fushi ya nufi dabar dake ƙofae gidan shi kamar an aika mishi da saƙon mutuwa. Mutanen da ke zaune a dabar kuwa da wata mahaukaciyar dariya suka kece suna tafa hannaye.....kallon banza da Kawu ya watsa musu yana muzurai kamar wani dodo yasa suka tsagaita.

“Haba Ale Idrisu, kar ka bamu kunya Manah! Kai da kace yanzu zaka fatattako su har waje ya naga kai ka dawo”

Fadin Baba Mola kenan wanda shima mazaunin dabar ne kuma ɗaya daga cikin tawagar Ale Idrisu.

Kallon shi Ale Idrisu yayi sannan ya sauƙe murya ƙasa saboda kada sauran tawagar su ji yace “wallahi wannan tsinanniyar yarinyar ce da ke hana ni rawar gaban hantsi, ammah zan ci ubanta ne shegiya”

Dariya Baba Mola yayi sannan ya dubi abokin shi Ale Kabir kafin yace “kada ka damu aboki na, shawara ɗaya kawai zaka bi domin samun muradin ka!”

Cike da ƙaruwar Ale Idrisu ke kallon Baba Mola Wanda ke wani lumshe idanuwa tamkar mai jin bacci yana washe bakin shi da ya koma baki tsabar zuƙar sigari da yayi mishi kanta.

“Na faɗa maka yarinyar nan kawai ka samu ka haɗa ta ka kai ta gidan mata, tun yanzu inda ta saba da can kaga shikenan, ko ka manta da alƙawarin da kayi wa shugaba ne?”

Zaro idon shi yayi nan da nan alamun rashin gaskiya suka bayyana akan fuskar shi. Hakan yayi daidai da fitowar Zahrah zuwa gidan su ƙawar ta. Kallon banza ta bi su da shi tana tofar da yawu irin taga kashi ɗin nan ta wuce. Shi kuwa Kawu ganin ta sai ya ɗaure fuska yana ƙara maida hankalin sa ga Baba Mola.

Ɗan baƙi ne ya juyo ya kalli uban gidan sa bayan wucewar Zahrah yana wani lashe baki tamkar maye.

“Yah oga nifah nayi kamun yarinyar nan, kyakkyawa ce son kowah, ah nidai zan jira nan da shekara biyu zuwa uku kawai ka wullo min ita”

Ya ƙarasa yana tanɗe baki. Kallon baka da hankali Kawu ya wulla wa ɗan baƙi. “Lallai ɗan baƙi baka da hankali, in kai ina yarinyar da ko shekaru goma bata wuce ba! Wai ma an ce maka duk rashin son ta da nake zan baka ita ne, Toh ita ɗin mallakin ɗan masu kuɗi ne kuma jari ce a gare ni! Saboda haka ka kauda idon ka a kanta tuntuni ka riga kasan da hakan koh?”

Ya faɗa yana cije leɓen shi sannan ya maida hankalin shi ga Baba Mola suka ci gaba da maganar su.

Ɓangaren Zahrah tunda ta wuce dabar su Kawu ta fara ɗan gudun ta tana tsalle tsalle irin na yara da ta saba yi har ta zo wajen wasu yara da suke wasa waɗanda su ma ba zasu wuce sa'annin ta ba. Wani daga cikin yaran ne ya watso mata ƙasa ai kuwa bata yi wata wata ba ta cakumo shi ta fara narka kamar ɗan ta. Wani tsoho ne yazo wucewa ya fara raba faɗan ammah Zahrah ta ƙi sakin Yaron nan. Duka kawai take kai mishi yayin da yayi la'asar har abun tausayi. Tsoho kuwa da yaga yarinyar ta fi ƙarfin shi yasa ya koma gefe yana jiran ko Allah zai kawo wani matashi..

Cikin motar shi yake ƙirar Mercedes Benz Mai tinted glass ya shawo corner ɗin. Ganin yarinya ƙarama ta kama yaro sai jibgar sa take gashi ya kasa tsinana komai alamun ya jima a hannunta ya sa shi yin parking.

Cikin takun sa na ƙasaita ya fito. Ba tare da ya ce komai ba ya nufi wajen da yarinyar take su kuma sauran yara sai kallon su suke saboda suma tsoron yarinyar suke kada su je garin rabiya ta dawokansu.

Hannun ta ya riƙe tare da jan ta gefe ammah ina Zahrah ta yi wani kukan kura zata ƙwace, jin ƙoƙarin ta na kwacewa yasa yayi murmushi sannan ya juyo da ita tana fuskantar shi.

“ke bari Manah!” abun da kawai ya faɗa sannan ya ɗago yaron da ke kwance a ƙasa jikin sa kaca kaca da ƙasa. Bata yi yunƙurin sake kamo yaron ba saboda irin kwarjini da yayi mata sai ta ja gefe tana saita numfashin ta.

Yaro kuwa ganin an ƙwallon e shi ai gidan su kawai ya nufa ba tare da yace komai ba. Ishaq kenan, ɗa ɗaya ga Cancellor wanda ya kammala karatun shi na mass communication yanzu haka next month zai wuce America for his masters.

Kallon ta yayi lokaci ɗaya yaji yarinyar ta burge shi, yana so yaga mace jaruma, wacce bata bari a gano raunin ta. Murmushi yayi mata sannan yace

“yan mata ya sunan ki” Zahrah kuwa tayi tunanin zai dake ta ne amma jim tambayar da yasa ta ce “Zahrah”

Yace “wow! Nice name" duk da cewa bata San meh yace ba da turanci kawai sai tayi murmushi har dimple ɗin ya ya lotsa.

Ishaq kuwa samun kan shi yayi da zuba mata ido sannan yace “which class are you now, yau Monday Mai ya hana ki zuwa makaranta?”

Lokaci ɗaya yanayin Zahrah ya sauya gashi yayi mata turanci kuma bata so ya gane cewa bata iya ba. Can tace

“ai ba a yin komai a makarantar ma, shi yasa bamu zuwa yanzu ma gidan su Amira zanje” “waye ce amirah?” “ƙawa ta ce” “toh muke na kai ki sai kike nuna min hanya”

Kafaɗa ta maƙe alamun ba zata je ba, ko kaɗan Mamah ta hana ta kwaɗayi balle har shiga motar yan gayu, inaaaa ba zata shiga ba.

“tsoro na kike ji Zahrah? Sunkuyar da kanta tayi sannan tace “a'ah” Cike da kulawa ya tsuguno daidai yadda tsayin su zai daidaita ya kamo hannun ta “kin ga cutie ki ɗauke Ni matsayin yayan ki, kada ki ji tsoro na bazan cutar da ke ba”

Cike da gamsuwa ta kaɗa kanta sannan yayi murmushi yace “good! Taho mu tafi"

Bin bayan shi tayi sannan ya buɗe mata seat ɗin mai zaman banza, bayan ta shiga ya rufe sannan suka fara tafiya tana nuna mishi hanya.

“cutie kika ce baa komai a makarantar, wa ce kike zuwa?” “bamu da nisa da makarantar, primaryn gwamnati ne"

Zaro ido Ishaq yayi sannan yace “kina so na sauya miki makaranta?"

Tuni ta ɗaga kai abun ka da yarinya babu hankali. Shi kuwa murmushi yayi sannan yace “alright zan saka ki wata makarantar ammah sai kin daina faɗa irin wannan da na tarar kina yi..."

Bata jira ya ƙarasa faɗin abun da ke ranshi ba tace “na yadda, na ma daina daga yau” “shikenan zaki raka Ni gurin baban ki ai?” “aah Baba na ya rasu, sai dai Kawu na da Mamah na, kuma Kawu ba so na yake yi ba kullum sai ya duka mu Ni da Mamah na”

Cike da mamaki Ishaq ke kallon Zahrah sannan yace “shikenan sai ki raka Ni wurin naman naki" a daidai nan suka iso gidan su amirah sannan yayi parking.

Kallon ta yayi sannan yace “cutie yaushe zaki koma gida?”

“sai da Yamamah zan wuce kasuwa taya Mamah aiki" “shikenan zan zo da yamma kin ji, sai muje wurin Mamah ɗin"

Daga haka ta fice da gudu ta nufi gidan su Amira ko godia bata mishi ba. Ya dade kafin ya ja motar shi ya tafi yana mamakin zantukan Zahrah, kuma yayi niyyar tallafawa rayuwar ta.

KO DAI ISHAQ SON ZAHRAH YAKE? TOH IN SON TA YAKE YA ZAA YI DA KAWU? KO MAMAH ZATA AMINCE? MENENE ALAƘAR KAWU DA MAMAH?

Duka amsoshin ku na cikin littafin *_Babban gida_* Yanzu ma aka fara!

Ku ci gaba da bibiyar alƙalami na don nishaɗantuwa, ilimantuwa da kuma samun faɗakarwa.

COMMENTS ƊIN KU NA DA MATUƘAR AMFANI DOMIN SHINE ƙWARIN GUIWA TA

DIAMOND LADY ce□□

[18/09, 7:00 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing   *A BABBAN GIDA*   _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 02

Wannan shafi naki ne masoyiya AISHA MB (Baby Isha) marubuyar littafin _aljanar ruwa ce_ Thanks a lot for ur selfless actions friend, loads of love Barka da Sallah

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Anyi sallar azahar kenan sai ga Yaya Ishaq ya zo kamar dai yadda ya faɗa, ya rasa ma ta yaya zai kira cutie ɗin tazo. Wani yaro ne yazo wulgawa ai kuwa da sauri ya dakatar da shi.

“kai yaro zo” ba tare da musu ba yaron ya je wurin yaya Ishaq Ɗan kallon yaron yayi sannan yace “ka ɗan shiga gidan nan kace Zahrah ta zo inji yaya ta”

Ba musu yaron ya buɗe ƙofar gidan sannan ya shiga ɗauke da sallama a bakin shi.

“Salamu Alekum” Maamahn Amira da ke shara ita ta amsa masa tana mai dakatawa da sharar don jin neh yaron yazo yi

“wai Zahrah tazo in ji yayan ta a waje” Bai jira amsar da maamah zata bashi ba ya fice abun da. Yayah Ishaq kuwa har kuɗi ya bawa yaro.

Maamah ce ta ƙwala kiran amirah da suka wuce can filin bayan gidan suna wasan su. Jin shiru basu amsa ba yasa ta wuce a fusace

“ke yar karuwai ki fito yana jiran ki a waje” Cike damamaki take kallon mamah. Shin meh yasa ake danganta ta da karuwanci?, Menene laifin ta da za'a ke mata hakan? tunawa da sabon yayan ta Ishaq da tayi, ai kuwa da gudu ta fita tana yi wa amirah sai da safe.

Tana ganin yaya Ishaq ta ɓare baki kamar gonar auduga yayin da shima yake jin ta ajikin shi. Babu abun da yake yi sai aika mata da saƙon murmushi.

“cutie, kin ce zaki kai Ni wurin Mamah koh?” Zaro ido Zahrah tayi kamar wata munafika. Shi kuwa yaya Ishaq jin. Shiru yasa ya ƙara kallon ta tare da faɗin “cutieeee...”

Ɗan tunani tayi da yar ƙaramar ƙwaƙwalwar ta sannan tace “toh yaya muje” “yauwah cutien yaya.”

A hankali yake driving ɗin yayin da hankalinsa kwacakwam ya dawo gare ta. “cutie mai Mamah take ji a kasuwa da yamma” Ɗagowa tayi da har zata yi shiru wata zuciyar tace ki faɗa masa wataƙila sanadiyyar haƙa sai ya samar muku sauƙi daga muguntar Kawu.

“mamah fah masa take soyawa a kasuwar kasan saboda meh?” Kai ya girgiza kamar wani yaro yayin da ta marakraice fuska

“idan taje tayi Masar ne take samun kuɗi, sauran Masar kuma muna ci da daddare saboda Kawu baya bata kuɗin abinci, sai dai shi ya shigo da ledar abubuwan sa da tsire da irin lemon jarkar man ammah baya taɓa ko sanmana..” can ta ɗan yi shiru

“kuma da kuɗin Masar Mamah take min kayan sallah, sannan tana wankin gidan Cancellor ma saboda ta samu kuɗi”

Jikin yaya Ishaq sanyi yayi jin irin wata rayuwa. Yana nanata wa a ranshi wai baya basu abinci. Kai anya wasu mazan ko

zasu shiga aljanna? Ka auro mata ka rabata da gidan su ammah ba zaka iya ciyar ta ba? Haba maza ai kuwa zan taimakawa waɗannan ahaki ko meh zai faru.

Zahrah kuwa da taji shirun yayi yawa sai ta ɗan taɓo fuskar shi “ka fasa zuwa ganin Mamah koh?” Jijjiga kai yayi sannan yace “aah cutie, zanje naga mamah”

Isar su kasuwa keda wuya suka fito, Zahrah ce gaba sai yaya Ishaq da ke bin bayan ta. Directly rumfar da Mamah ke ƙosai ta nufa.

“Mamah ga sabon yayah nah” Mamah da ta ke kwashe Masar da ta soyu ta ɗago ɗan bata fahimci meh Zahrah ke faɗi ba.

“ya Hajiya Balaaba ɗin”

Ɗan yamutsa fuska tayi da ta tuna wulaƙancin da maamah ɗin tayi mata sannan tace

“lafiyar ta ƙakau, tace a gaishe da ke”

murmushi Mamah tayi sannan ta zuba masa uku a plate ɗin roba sannan tace

“ga Masar nan kici,, nadan baki ci komai ba”

Amsa tayi ta ajiye sannan tace

“mamah ga sabon yaya nahiyar yazo gaishe ki”

sai a lokacin Mamah ta lura da yaya Ishaq dake tsaye harɗe da hannayen shi a ƙirji. Shi kam hankalin shi baya kan shi, in ba da kallon su Mamah babu abun da yake yi.

Gyaran murya Mamah tayi, sai lokacin ya ɗan miƙe da kyau sannan ya nufi rumfar Masar. Duƙawa yayi ya gaida Mamah cike da girmamawa.

“ina wuni Mamah, ya aikin” “lafiya ƙalau ” kawai Mamah tace fuskar ta na ainihin bayyana mamaki da kuma kuɗin da ta shiga, idan bata yi ƙarya ba ai wannnan yaron gidan Cancellor ne.

Ganin yanayin Mamah yasa yaya Ishaq ya murmusa..

“mamah nimah ki ɗauke Ni kamar ɗan ki, ki ɗauke Ni kamar yadda na ke jin ƙanwa ta Zahrah a jiki na, bani da niyyar cutarwa a gare ku sai dai ina don tallafa wa rayuwar ku.”

Murmushi mamah tayi “babu komai yaron nan ammah kai ɗin waye, kuma a ina kaga zahrah.” “mamah Ni ɗa ne a wajen Cancellor sannan kuma na haɗu da Zahrah ne hanyar tafiyar ta zuwa gidan su Amira ƙawar ta” Tun daga farko har kaita gidan su amirah da yayi ya labarta wa Mamah. Salallami ta fara “shikenan Ita dai Zahrah ba zata taɓa sauya halin ta ba kenan, toh Allah dai ya shirya”

Murmushi yaya Ishaq yayi sannan ya matso cikin rumfar, gefen matackn da take ajiye soyayyiyar masa yayi sannan ya kwashe ledodin,, duk wanda yazo siya da kan shi yake zuba musu har lokacin maghrib yayi. Masallacin da ke cikin kasuwar yaje yayi Sallah ya dawo. A lokacin Mamah har ta gama haɗa kayan suyar ta zasu dawo gida.

Ƙarasawa yayi ya ce “mamah a kwaso kayan sai mu tafi.” Ƙasa musu mamah tayi kawai ta umarci Lauwali almajirin dake taimaka mata da su wuce. Har wajen motar suka nufa sannan ya jera kayayyakin suka wuce ɗiiiiiiiiiii sai gidan Kawu.

Mamah kam lumshe ido tayi yayin da zuciyar ta ta karye, tunanin when last tashiga mota take yi tun ranar da aka kawo ta gidan masoyin ta Abdulkarim Kuru. Lokacin da ta cire tsammanin wahala a rayuwar ta sai gashi yanzu ɗan uwan masoyin ta na gasa mata aya a hannu.

Suna isowa Lauwali ya ciro kayan ya shigar da su gida, abun mamaki lokacin dabar su Kawu babu kowa sai Aminu Aljan.

Basu mishi magana ba suka kutsa cikin gidan. Bayan sun ajiye komai Mamah ta shimfiɗa wa yaya Ishaq sallaya ya zauna sannan ita ma taje tayi sallah. Mutuniyar kuwa kwantawa taje tayi.

Har Mamah ta idar da Sallah bata ga giftawar Zahrah ba yasa ta ƙwala mata kira “zahrah, Zahrah fito ki je ki siyo wa Ishaq ruwa gidan su Badi'ah.” Zahrah da bacci ya ɗan fara kwashe ta ta turo baki gaba sannan ta fito. Mamah sake baki tayi tana kallon ta ganin ko Sallah bata yi ba. Harara ta ɗan yi mata sannan tace “wuce kije kiyi sallah”

Juyawa Zahrah tayi tana ɓata fuska kamar wainar fulawa sannan taje tayi alwala don yin Sallah. Lauwali kuwa ya gama wanke kayayyakin kamar yadda ya saba yayi ma Mamah sai da safe. Yaya Ishaq ne ya ƙira shi bayan yazo ya zaro 5k a aljihun shi ya bashi. Godia sosai Lauwali yayi sannan ya wuce.

Zahrah na idar da Sallah ta fito, gefen yaya Ishaq ta zauna sai wani tura baki gaba take yi kamar wani pipe. Harara Mamah ta maka mata kafin ta ce “tashi kije gidan su Badi'a ki siyo masa ruwa da lemo.. ba musu ta miƙe duk da cewa bata don zuwa gidan.

Badi'a Sa'ar ta ce ammah basa shiri ko kaɗan saboda yadda suke treating nata. Gaba ɗaya unguwar babu wanda ke kyautata musu inda ka cire gidan Cancellor sai kuma Ammin Badi'a, ita dai bata tsangwamar su ammah bata shiga sabgar su.

Bayan ta siyo ta kawo gaban shi ta ajiye, Mamah ta zubo mishi Masar a plate sannan ya fara ci ba tare da jin ƙyamar su ba. Ita ma Mamah tace tare da Zahrah. Bayan sun gama ci yaya Ishaq ya sanar da Mamah ƙudurin shi na maida Zahrah private school da ke kusa da su. Mamah tayi farin ciki sosai har da kukan ta zai aikin godiya take rabza wa Ishaq, shi kuwa duk kunya ta cika shi.

Da haka yayi musu sallama ya wuce zuwa gida zuciyar shi wasai.

★★★★★ Sai wajen ƙarfe sha biyu na dare (12:00pm) Kawu ya dawo, su kuwa lokacin sun riga da sun rufe gidan. Bugawa yake ta yi babu ƙaƙƙautawa sai kututtuma ashar yake yi. Sama sama mamah ta jiyo ƙarar buga ƙofa,, a zabure ta miƙe zuwa hanyar waje.

“dan abu ta kazar ubanki ki kizo ki buɗe min ƙofar nan inda ba haka ba in na shigo sai na lahira ya fiki jin daɗi.

Jinjina kan ta tayi kafin taa nufi ƙofar. Tana buɗe ƙofar ko ya banko ta har sai da ta buge kan Mamah. Layi ya shigo yana yi alamun yayi mankas abun shi. Mamah kuwa cikin zuciyar ta tana Allah wadaran wannan miji nata.

Ƙunshi ledar hannun shi ya ya ƙara ƙanƙamewa kamar za'a ƙwace mishi daga hannun shi. A haka ya nufi ɗakin shi cikin tangaɗi har ya isa bakin ƙofa.. juyowa yayi ya kalli Mamah before ya shige ya na banko ƙofar.

Hawayen da ke zuba kan fuskar ta ta gode haɗi da wucewa nata ɗakin. Ba ita ta ta kwanta ba sai da ta yi alwala ta fara jera nafila tana roƙon Ubangiji ya kawo mata ɗauki.

_____**********_____

Ina kuke bayin Allah masu buƙata! Ina waɗanda ke cikin damuwa, ina waɗanda suke buƙatar neman wani zaɓi wurin Ubangiji.

Toh ga damah nan wacce take guarantee.

Manzon ALLAH صـلي الـلـه عليـه وسـلم yana cewa:- “idan dare ya wuce tsakiya ALLAH (Subhanahu wata'ala) yana sauƙowa zuwa saman duniya sai ya ringa cewa:- (shin akwai mai neman gafara a gafarta masa ?) yana ta fadar hakan har zuwa ketowar alfijir.

(saheeh musleem)

Saboda haka duk wata damuwa da kike da ita, don't hesitate to ask Allah, baya gajiya da amsa buƙatun bayin sa. Ki tashi kiyi sallah, koda raka'āt biyu ne sun wadatar ki roƙi Ubangiji kina mai yaƙini da shi, sai kiga ya amsa miki.

Kina cikin damuwa? Matsalar gidan aure ko kuma jarrabawar rayuwa, toh kada ki kuskura ki cire yaƙini a addu'a.

YA hayyu~ya~Qayyum!! Kayi gafara agaremu da iyayanmu da 'yan uwanmu da masoyan mu da sauran al'ummar musulmai.

KO YA ZATA KAYA? WANE NE KAWU?ME ALAKAR SHI DA ZAHRA?, MEH YASA YAKE CUTAR DA ITA? YA KUKE TUNANIN ZATA KAYA IDAN KAWU YA FAHIMCI CEWA WANI NA ƘOƘARIN TAIMAKAWA MAMAH?

AMSOSHIN KU NA NAN TAFe, BA A FARA LABARIN BA HAR SAI MUN JE BABBAN GIDA.

KU CI GABA DA KASANCE WA DA ALƘALAMIN DIAMOND LADY DOMIN NISHAƊANTUWA DA KUMA ILIMANTUWA.

COMMENTS ƊIN KU KAWAI NAKE SO DON SHINE ƙWARIN GUIWA TA ALƘALAMIN DIAMOND LADY Oum Zainab ce!

[19/09, 10:21 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 0 3

Shafin ku ne ƙawaye na ZAINAB SHEHU UMAR (ZEELY) SA'ADATU LAMARA ZULKHAIRAT (Matar mijinta) RABI'ATU ABDULLAHI HASSAN (matar Ɗan jagade) FATIMA AHMAD ABDULLAHI (Fatima anatomy)

Ina ƙaunar ku saboda Allah Barkan ku da Sallah

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Sassafiya Mamah ta tashi da aikace-aikacen gida. Sai around 8:00am Zahrah ta fito tana miƙa “ooooooooooh” Mamah ce ta kalle ta sannan ta kawar da kai. Wurin Mamah ta taho “ina kwana Mamah" “lafiya ƙalau Zahrah kije kiyi wanka sai ki siyo manah ƙosai da koko gidan Mati."

Da “toh Zahrah ta amsa tana wucewa bandaki. Bucket ta cika da ruwa sannan ta shiga toilet ɗin. Wanka tayi ta fito. Rigar ta yan kanti wacce ta ɗan ji jiki ta saka kafin ta shafa mai. Tana gamawa ta janyo hijabin ta da saman shi ya ɗan koɗe saboda dukan rana.

Fitowa tayi ta cewa Mamah “kawo kuɗin” miƙa mata 500Naira tayi sannan tace “ki siyo bread Babba guda ɗaya da canjin. “toh" Daga haka ta fita zuwa gidan Mati da ke kan kwanar layin su. Tana fita ƙofar gidan su nan a cike kamar wadda za'a yi taro sun cika rumfar wasu kuma har da kan dandamalin da ke jikin gidan sai ihu suke suna buga uban shewa da gani kaga tataccun yan iska. Kallo ɗaya tayi musu ta kau da kanta gefe haɗi da tsaki. Aljan ne ya hango ta sai wani fara washe baki “yar oga! Ina zaki haka da sassafe" Bata yi tunani da ita yake ba shi yasa ko kallo bai samu daga gare ta ba. Su kuwa sauran yan dabar suka saka ihu nan suka fara tsokalar Aljan.

Da ɗan gudu ta isa gidan sannan ta bada kuɗin ta haɗi da miƙa jug ɗin roba da ta zo da shi. Ana sallamar ta ta amsa bread wajen Bala Mai shayi daga nan ta wuce gida.

Kamar dai ɗazu wurin a cike yake ammah haka ta wuce abun ta saboda gargaɗin Mamah kan kada ta kuskura ta ce zata kula wani a dabar.

A ɗakin mamah suka karya, Bayan sun karya Mamah ta ɗauƙo wasu kuɗaɗe daga aljihun doguwar rigar da ke jikin ta. Kuɗin zasu kai 15k. Da mamaki Zahrah ke kallon kuɗin, duk da bata da wayo sosai ammah ta san wannan kuɗin da yawa suke

“mamah kuɗin menene wannan?” “yayan ki Ishaq na da kirki sosai, ya bamu ne mu ƙara a jarin masa”

Ko rufe baki Mamah bata yi ba taga ana shigowa da kayan abinci, shinkafa, taliya, macaroni, indomie da mai har da manja. Mamaki ne a fuskar su har lokacin da aka ce “a ina za'a ajiye su?”

Nuna musu ƙofar ɗakin ta tayi don kuwa nan ne wajen da zasu rabauta daga hannun Kawu. Suna gama shiga da su suka fita. Mamah bata bar mamaki ba ammah tayi shiru abun ta.

Sai wajen 11:00am Kawu ya banko ƙofar ɗakin shi fuskar nan duk yawun bacci alamun ko sallar asuba bai yi ba. Wata shegiyar miƙa da yayi abun takaici Mamah dai jinjina kai tayi tana roƙon Allah ya shirya Yunusa..

Wani kallon banza ya watsowa Mamah sannan yace

“ke ɗan ubanki shine jiya kina ji ina buga gida kika ƙi buɗe min? Gidan na ubanki ne? Nace na ubanki ne gidan?”

Mamah dai bata kula shi ba ta ci gaba da yi wa Zahrah bayanin yadda zasu sauya kasuwancin nasu. Sheƙa Kawu yayi hakan yasa ya kawo wa Mamah wani uban duka.

Caraf Zahrah ta tare ai kuwa sai a tsakiyar kanta wanda yayi sanadiyar faɗuwar ta ƙasa sumammiya. A firgice mamah ta yo kanta tana jijjiga ta ammah shiru. Hakan bai ishi Kawu ba sai da ya ƙara kawowa Mamah wani dukan. Bata damu ba saboda hankalin ta da ya matuƙar tashi kada taje ta rasa ɗiyar ta.

Ba tare da ya damu ba ya fice zuwa dabar tasu. Wani ihu suka sa suka fara yi mishi kirari

“Takawar ka lafiya Yunusa BabanMutuwa, kayi yadda kaso da uban kowa, ita kanta mutuwar tsoron ka take, kaga sarki mai cikakken iko”

Dariya yayi jin yadda ake fasa mishi kayi nan da nan majalisa ta fara, ana shan sigari ana gulma tare da kututgumo ashar. Authubillah!

★★★★★★★★

Ta ɗauki kimanin mintuna 20 kafin Zahrah ta ja dogon numfashi wanda lokaci ɗaya ta saki wani irin ihu. Mutanen da ke waje kan su sun tsorata bare kuma Mamah dake kusa da Zahrah, wasu faratu ne zaƙo zaƙo suka fara fitowa daga hannun ta sannan ƙwayar idon ta ta juya baka ganin komai sai farin idon da ya sauya zuwa blue colour ga wani girma da jikin ta ya ƙara tamkar wata aljana da ta fito filin daga.

Mamah ko rasa yadda zata yi da ita tayi, banda ɓari babu abun da jikin ta ke yi. Miƙewa tsaye Zahrah tayi tana nufar hanyar waje, Mamah bata yi ƙoƙarin riƙe ta ba saboda ita kanta a tsorace take.

Hakan yayi daidai da shigowar Kawu cikin gidan. Zaro idanuwa yayi cikin kiɗima ya fara ja da baya da niyyar guduwa..

Kirif!! Ƙofa ta rufe kanta yayin da halittar dake gaban shi ta sheƙe da wata dariya maras daɗin ji.

“Hahhhhhhhhh_hhhhhhhhh_hhhhhhhhhhh” dariyar da bata tsaya ba sai bayan minti 10. Kawu kuwa duk rashin tsoro irin nashi yau yaji, ai ance faɗa da aljani ba daɗi.... gabaɗaya zufa ce ke ketowa a jikin shi, bata yi mishi komai ba kawai hannun ta ta ɗaga sama lokaci ɗaya Kawu ma ya ɗago bisa iska.

Gefe ta wulla kawu kafin ta ƙara daga shi can sama a wannan karon, wani irin jujjuya shi take wanda hannun ta ne ke famar yin wannan aiki ɗin, bugawar da tayi mishi sai da ƙasa ta jijjiga, tuni ɣan majalisa suka watse duk da basu san daga ina bane hakan.

Ko motsi Kawu baya yi hakan yasa ta busa mishi iskar bakin ta daga wurin da take. A wahalce yaja wani dogon numfashi. Bai zata ba bai nufa ba sai ka cinnaku sun kewaye shi, cizo ta ko ina yi masa suke. Babu abinda yake banda susa da kururuwa.

Duk abinda ke faruwa Mamah ta kasa cewa komai. Sai can ta samu bakin magana

“zahrah don Allah kiyi haƙuri ki bar shi haka ai yaji jiki”

“hhhhhh_hhhhh" bayan wani lokaci tayi shiru sannan ta juyo tana fuskantar Mamah

Cikin haɗe fuska take magana “Madina! Wannan ba Zahrah bace nice!” ta faɗa cikin Muryar ta maras daɗin saurara..

Jikin Mamah ne ya fara tsuma hakan yasa Zahrah hura wa Kawu iska, nan da nan cinnakun suka ɓace ɓat! Jikin shi kuwa duk ya kumbura, ga uban ciwon da yake masa. Banzan kallo halittar ta watsa mishi sannan tace

“Idrisu BabanMutuwa!" A tsorace Kawu ya ɗaga sannan ya maida kan sa ƙasa

“ka saurare Ni da kyau! Ka gama naka mulkin yanzu lokaci na ne! Ka daɗe kana cutar da mahaifiya ta da bata taɓa zaluntar ka ba!”

A lokacin mamah ta zube a ƙasa sumammiya. Duk wannan na daga cikin shirin halittar.

“Idrisu Ni na san ka! Ka cutar da rayuwar mu, baka san cewa na san kai ne ka kashe mahaifi naba koh?, Kai ne ka hana Mamah komawa ga dangin ta ta hanyar sihiri koh? Toh wallahi ka kuskura ka ƙara wani kuskure kan hakan zan tona asiri har ƙwayoyin da kake siyarwa”

Kawu dai an rasa bakin magana,kai kawai yake jijjigawa.

“magana zaka yi ba jijjiga kai kamar gwaje ba”

“eh na daina wallahi na daina”

Daga haka ta ɗaga hannun ta lokaci ɗaya shima ya tashi bata direshi ko ina ba sai cikin ɗakin sa. Tana fitowa ta ɗaga Mamah ma ta kai ta kan katifar ta.

Daga nan ta hura mata iska ita kuma ta faɗi ƙasa kamar matacciya..

Numfashi Mamah ta sauƙe lokaci ɗaya kuma ta tuna meh yake faruwa. Tana juyo wa taga Zahrah kwance kamar gawa..

A hankali ta nufo ganin kamar bata motsi yasa Mamah saurin ɗebo ruwa a cup, addu'ah ta tofa ciki sannan ta shafa mata a fuska.

Numfashin da Zahrah ta ja yasa Mamah jin sanyi cikin ranta. A hankali ta fara buɗe idanuwan ta tana mai tuna abun da ya faru.

“Sannu Zahrah, ina ne yake miki ciwo?” ta faɗa a kiɗimce

“mamah kai na”

“sannu yi haƙuri bari na je na siyo miki magani, ki jira Ni kada ki fita kinji..”

Hijabin ta ta janyo ta fito, karo suka ci da ya Ishaq ƙofar gida ba tare da yan shi bane ta gota zata wuce. Cike da mamaki yace

“mamah meh ke faruwa?” sai a lokacin Mamah ta ɗago

“zan siyo paracetamol me a nan chemist zahrah ce ba lafiya.”

“subhanallah, toh ki koma ciki bari na shigo Mu kai ta asibiti.”

Da kan shi ya ɗauko Zahrah ya saka ta a mota. Babu ƙaƙƙautawa suka isa asibiti. A&E (Accident and Emergency) aka nufa da Zahrah. Taimakon da ta samu daga wurin likitoci yasa ta ɗan ware.

Sai wajen 5:00pm aka sallame su ammah kafin nan Doctor ya nemi magana da namijin saboda matar kam duk a ruɗe take.

Soyayyanovels

Bayan sun shiga office ɗin doctor, a hankali doctor ɗin ya kalli yaya Ishaq

“bawan Allah garin ya kuka bar ƙanwar taka damuwa ta mata yawa, yarinya ƙarama a ce BP nata na elevating haka tun yazo, gaskiya da matsala ko ma meh take so ya kamata Ku bata”

A sanyaye yaya Ishaq yace “in sha Allah doctor za'a kiyaye”

Daga haka ya fito. Da kanshi ya ƙara ɗaukan Zahrah suka nufi mota har suka isa babu wanda yayi magana. Bayan sun isa Mamah da kanta ta wanki Zahrah da ruwa mai zafi sannan ta haɗa mata tea Mai kauri da sauran kayayyakin da Ishaq ya siyo musu.

Bayan sallar maghrib yaya Ishaq ya fita sallah sannan Mamah ma tayi. Kallon Zahrah tayi tace “zaki iya sallar?" Kai ta gyada a hankali Mamah ta taimaka mata tayi alwala a zaune sannan tayi sallar ma a zaune. Bayan yaya Ishaq ya dawo Mamah ta shiga kitchen don girka abinci, ya rage iya yaya Ishaq ne da Zahrah. Kallon ta yayi yace

“cutie, meh ke damun ki haka kike sa damuwa a ranki” “babu komai yaya Ishaq, meh ka gani?” Wani kallo ya watsa mata “baki yadda Ni ɗan uwan ki baneh da ba zaki iya sharing damuwar ki da Ni ba ko?” Jijjiga kai tayi tace “aah yaya babu komai fah, Ni mah ban San meh ya same Ni ba kawai dai Kawu ya zo dukan Mamah shine na tare, daga nan ban san ina nake ba”.

Shiru yayi yana nazarin wannan kawun da take faɗa, yana don ganin shi gaskiya. “shikenan cutie, ki huta kafin Mamah ta gama girki”

Bayan sun ci dinner tukun na Yaya Ishaq ya tafi.

TOH FAH, YA RAI ZA'A KAYA, YAU KAWU ANJI JIKI WURIN ALJANU KO kAWU ZAI SAUYA HALI?

Duk cikin babban gida. BA'A FARA WASAN BA, JUST FOLLOW MY INK

[19/09, 10:21 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 0 4

Ina matuƙar godiya masoya na! Wannan PAGE ɗin naku ne. Allah ya bar ƙauna. Much love

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Har zuwa lokacin nan Kawu bai fito ba, ganin haka yasa Mamah zuwa ƙofar ɗakin ta leƙa. Suna haɗa ido ya galla mata harara hakan yasa ta fito waje babu shiri.

Sai bayan sun shiga ɗaki Kawu ya fito. Jikin sa yayi ruɗu ruɗu kamar wadda aka yi ma bulala. A hankali ya lallaɓa ya fice. Kai tsaye gidan Aminiyar shi jummai Rubber ya nufa.

Masu gadi sanin shi da suka yi da irin yadda yake alaƙa da uwarɗakin su yasa suka buɗe mishi. Ba tare da ya kula su ba ya wuce zuwa cikin gidan.

Zaune take daga ita sai wani matsiyacin shiru wanda da shi Gara babu, sai kuma bra.

Fara ce sol, jibgegiya. Can ƙarshen parlourn wasu ɣan mata ne da ba zasu wuce 23years ba tsirara haihuwar uwar su sai masha'ar su suke yi (authubillah). Ko kunya babu haka suke ta abun su basu daina ba har sai da Jummai Rubber ta Basu umarnin fita zasu yi magana da baƙo..

A haka suka fice yayin da Rubber ta zubawa Kawu ido tana nazartar shi.

“Takawar ka lafiya gwarzo jarumi, ka daki kowa ko zagi kowa, ko mutuwa tsoron ka take ji” Murmushi yayi da jin kirarin Rubber sannan ya maida hankalin sa gare ta.

“Rubber magana mai muyi” Dariyar shaƙiyyanci ta saka sannan tayi shiru “ai in na ganka idrisu na san magana ta kawo ka, ina jin ka”

“yau wani mummunan abu ya faru da ni” Nan ya kwashe drama ɗin su da Zahrah ta bata. Ita kanta abun ya girgiza ta in dai har kuwa da gaske ne akwai matsala.

“ni babbar samuwa ta ma bata wuce sanin Ni na kashe baban ta ba, ga kuma sanin ƙwayoyin da nake miki safara”

Cikin kwantar da hankali Rubber tace “Kaga kada ka wani damu, shawara ɗaya ce zan baka idan ka bita to zaka wuce wannan step ɗin”

Cike da ƙaguwa ya kalli Rubber sannan ya rungume ta (nace oh ita ɗin ma matar shi ne kam?) Cikin kunnen shi ta faɗa mishi wata magana wanda duk gulma ta ban jiyo meh suke faɗa ba sai ji nayi yace “gaskiya Rubber me ta daban ce” Murmushi tayi sannan ta manna mishi peck a kumatu daga nan wasan ya sauya salo (Authubillah)

Sai da suka gama suka yi wanka tare. A nan ya suka ci abinci kafin ya nemi wani ɗaki ya shiga. Wata ƴar Siriyar budurwa ce ta shiga ɗakin Bayan shi, jikin ta babu wasu kayan arziƙi haka ta shiga tana wani karairaya kamar macijiya. Tare da Kawu suka kwana suna sheƙe ayar su Ni kuwa nace (Allah ya shirye su).

★★★★★★★★

Alhamdulillah! Cikin ikon Allah jikin Zahrah yayi sauƙi, da safe Mamah da kanta tayi musu girki, bayan sun karya Mamah ta kai mata ruwan zafi toilet tayi wanka! Ba'a daɗe ba yaya Ishaq yazo. Tayi murnar ganin yayan ta sosai shima yaji daɗin ganin jikin da sauƙi..

Gaisawa suka yi da Mamah cike da girmamawa. Ya Ishaq yace “cutien yaya jiki yayi sauƙi koh" Cike da jin daɗi tace “eh yaya na warke”

Cike da zolaya ya ce “ai na yi zaton da safe zan zo cin jallof ne” Ya faɗa yana kanne mata ido. Cike da shagwaɓa tace “kai yayah! Ai sai ka riga Ni mutuwa ma” “ni rufa min asiri! Damah so kike na mutu ko” “aah yaya" ta faɗa tana zare ido “alright in kin ji sauƙi zuwa gobe sai na kai ki makarantar koh?” cike da farin ciki tayi hugging nashi tightly “na Gode Yaya Ishaq Allah ya ƙara maka buɗi ya faranta maka” “ameen cutie, to same Ni kafin ki karya ni ko” Ɗan tura baki tayi ta matsa gefe.

Haka suka yini suna shan hirar su har azahar, sallah yaya Ishaq yayi kafin ya dawo Mamah ta haɗa mishi nashi abincin. Ita kuma Zahrah ana rikici ita wallahi ba zata ci abinci ba ta ƙoshi

Da ƙyar da siɗin goshi ya lallaɓa ta suka ci tare, bayan sun gama yake sanar da Mamah batun makarantar da zai saka Zahrah yayin da ta ke ta sharɓar bacci abun ta.

“wacce makaranta da ɗin take zuwa Mamah" “nan makarantar gwamnati ne bayan inji mai wando” “ammah ta gama primary ai” “eh yanzu haka sun shiga jss 1 ne” “ohk shikenan goben zamu je sai a gama mata shirye shiryen saboda nimah sati mai zuwa zan bar ƙasar”

Da mamaki Mamah ke kallon Ishaq “ina kuma zaka je” “mamah zan je nayi masters ɗinah be, zan kammala biyan kuɗin jss ɗin ta, nasan zan shigo bayan shekara uku ko biyu”

Duk da cewa basu wani saba ba ammah Mamah tana jin Ishaq a jikin ta tamkar yaron da ta haifa.

“toh Allah dai ya bada abun da za'a ke nema ɗin” “Ameen Mamah bari zan wuce nikam, sai goben” “toh Ishaq sai ka dawo, ka gaida gida, Allah ya saka maka da alkhairi” “Amin” yace yana ficewa daga gidan.

Majalisar Kawu kuwa yau babu wanda ya zauna tun bayan jijjigar da suka ji anyi duk suka tsorata. Shima Kawu yana can yana sheƙe ayar sa gidan Rubber.

Da yammah jikin Zahrah ya warke, tace wa Mamah bari ta ɗan zagaya unguwar don Allah Bata hana ta ba ko ba komai jikin ta zai ƙara ƙarfi ai ina ta zagaya.

Wanka tayi ta fita tana yar waƙar ta har ta zo ƙarshen layin su, wata yar ajin su Lawisa Musa ta gani. Kamar wasu manya suka ɗan fara taɗi abun su “ah Zahrah Abdulkarim dama a unguwar nan kike?” Da mamaki Zahrah ta kalli Lawisa “kar ki raina min wayo mana Lawisa, ina banda uban ƙarya zaki ce baki san nan layin nake ba”

Sanin halin ta da Lawisa tayi yasa ta yi shiru kafin tace “sorry ƙawa ta, na shafa'a ne, toh ya gida” Farr da ido tayi tace “lafiya ƙalau" “jiya an zo duba masu fashi, Man Labour ya ɗauki sunan ku ammah ke Amira ta ce wai baki da lafiya da gaske ne” “eh wallahi Lawisa, jiya har asibiti aka kwantar da Ni" Cike da tausayawa Lawisa tace “Allah ya sauwaƙe Zahrah Abdulkarim, bari na wuce gida nikam, aika na Umma ta tayi”

Daga haka suka yi sallama. Zahrah ta juyo saboda duk ta gaji yar tafiyar da tayi.

A ƙofar gida suka ji karo da Kawu, ko kallon arziƙi bai samu ba daga wajen ta. Duk da cewa yana tsananin shakkar ta ammah hakan ba hana shi dakewa ba don da wuya ka gano tsoron Kawu.

“ke don ubanki baki iya gaisuwa ba neh?” Cikin halin ko ina kula tace “mutanen kirki masu daraja mutane su ake gaishe wa” ta faɗa tana gurmuɗa baki.

Shaye da mamaki ta tafi ta bar shi, ya rasa meh yake masa daɗin haka nan lokaci ɗaya yayi wata shu'umar dariya

“shawarar Rubber zata yi aiki kwanan nan inda ba haka ba zasu ruguza min buri na, kai!!! Basu isa ba, dole na dakatar da su. Dole.

Sallahr maghrib suka yi, sannan isha', ana kiran ishà Kawu ya fice ta uwar shayibu. Bayan sun yi dinner suka ɗan yi hirar su.

“mamah" Zahrah ta ambaci sunan ta “na'am Zahrah, menene?” “mamah yanzu haka zamu ci gaba da zama a gidan nan?, Wallahi Mamah Ni na gaji da rayuwar gidan nan, dubu fa duk mutane gudun mu suke yi saboda wannan banzan mijin naki”

“ke Zahrah! Ki kiyaye kalaman ki, kar ki manta ɗan uwan mahaifin ki ne shiɗin kuma miji na! Bana kuma son jin wannan zancen kinji ko”

Takaici duk ya cika ta tace “shikenan Mamah, toh Ni ki kai Ni wajen wata yar uwar ki manah! Ni tunda muke baki taɓa kai Ni wajen su ba” Ba tayi mamakin jin hakan daga Zahrah ba, tun bata kai haka ba take cewa su gudu gidan su Mamah ammah sai tace iyayen ta sun mutu.

Daga nan Zahrah bata kuma cewa komai ba tun da Mamah tayi shiru.

Ɓangaren Mamah lokaci ɗaya tsohon ciwon ta ya dawo sabo. Abun da take ƙoƙarin binne wa kullum kenan, sam bata so a dawo mata da zancen ko kaɗan.

Bata manta ranar da ta rabu da iyayen ta, shekaru 14years kenan! Lokacin da ta yi kunnen uwar shegu da ahalin ta! Gashi yanzu tana don zuwa gare su ammah ta kasa!!

“Ya Allah" kawai ta samu damar furta wa. Har wajen 2:00am bata yi bacci ba, yanke shawarar yin Sallah tayi ko zata ji sauƙi. Tana cikin sallar bugun gidan ya dira kunnuwan ta, bata katse sallar ba sai da tayi raka'āt biyu tukun nah ta fito.

Ƙoƙarin ta buɗe mishi sai dai abun haushi yau ma a buge ya shigo da ƙunshi ledar sa a hannu. Bangare ta yayi ya shigo ciki. Bayan ta rufe ƙofar itama tayi ciki tana takaicin banzan hali irin na idrisu. Ganin ya tsaya be shiga ɗaki ba ta ɗan taɓe baki ta wuce zata shiga ɗakin ta.

Jawo ta yayi ta faɗo jikin shi, cikin zafin Nama ta fizge jikin ta. Cikin Muryar ɣan maye yace “haƙƙi na zaki bani Madina" cike da takaici ta wuce zata shiga ɗakin ta ya ƙara jawo ta da ƙarfi. ɗakin ya cilla ta ya rufi kirif.

“Wallahi baka isa ba idrisu! Da ni zaka yi mu'amala kana cikin maye?” “toh meyeh....na..ga...naga....ke mata...ta...ce” “haƙƙin mata nawa ka sauƙe da zaka ce ina baka haƙƙin ka? Wallahi ba abun da zai haɗani shimfiɗa da ƙazami irin ka”

Cikin maye ya janyo dorinar da ya saba dukan ta da ita ya fara jibgar ta, ihu take ammah Kawu bai daina dukan ta ba kamar an aiko wahayi gare shi ne.

Duka sosai yake mata da shi kan sa sai da yaji jiki, tun tana ihu har ta daina. Duk budurin da ake yi Zahrah bacci ta take sha. Maƙwafta na jin ihu ya wuce misali suka fara fitowa.

Ammin Badi'a ce da mijin ta suka zo, ƙwanƙwasa ƙofar da suke yi shi ya tada Zahrah daga bacci. Jin babu Mamah a gefen ta yasa ta fito. A tsakar gidan ta tarar da ita yashe sai wani irin sauti take fitar wa ga Kawu kuma tsaye kanta da dorinar sa.

Bai lura da Zahrah ba sai da tazo wurin, ba tare da ta kula shi ba ta kwanta jikin Mamah tana sake wani kuka mai tsuma zuciya.

Jin ba a daina buga ƙofa ba yasa ta je zata buɗe, tsawa ya buga mata

“keeee....” bata kula shi ba ta wuce ta buɗe. Ganin Ammin Badi'a da mijin ta abun ya bata mamaki. Shigowa suka yi, Ammi ta riƙe hannun Zahrah suka shige.

Kawu bai jira wata wata ba ya fizgo Zahrah daga hannun Ammi. Dukan ta ya fara nan da nan tayi wani tsalle ta gudo bayan Ammi.

“Wallahi Kawu baka isa ba! Uban me Mamah tayi maka zaka mata irin wannan dukan, wallahi bazan taɓa yafe maka ba wani abu ya same ta. Meh yasa? MEH yasa nace MEH yasa Kawu? Ka cutar da rayuwar mu iya cutarwa, tabbas sakayyar Ubangiji tana jiran ka. Allah ya isa”

Daga haka ta kece da wani irin kuka mai ban tausayi. Jikin Mamah ta dawo ta na jijjiga ta

“ki tashi Mamah! Kada ki mutu, in kin mutu bashi da asara nice zan shiga maraici, Mamah ki tashiiii"

Ta ƙarasa cikin ƙaraji. Abban Badi'a ne ya umarci Ammi da ta taya Mamah ta kai ta ɗaki sannan ta bata taimakon da ya dace.

Zahrah gaba ɗaya hankalin ta baya jikin ta in ban da suruce suruce babu abun da take

“ke ma Mamah nace miki mu tafi wurin dangin ki kin ƙi toh ai dole muyi ta Fuskantar Matsala. Allah ya isa tsakanin mu da kai Kawu. Sai Allah ya saka manah.

MU HAƊU GOBE DUK YADDA AKA YI AKWAI WANI ƁOYAYYEN AL'AMARI MUJE ZUWA DON BA'A FARA WASAN BA SAI MUN JE BABBAN GIDA. CI GABA DA BIBIYAR ALƘALAMIN DIAMOND LADY....TARE DA ZABGA COMMENTS. Diamond Bhatool ce

[27/09, 6:07 p.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 05

Ina ƙaunar ki Qawa ta AISHA USMAN (Baby) namecy. Allah ya kula min da ke a ko ina ya cika miki burin ki. Much ƙauna

ƙawa ta ta kaina.. wannan shafi dai naki ne tawan....

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Ammi ce ta taimakawa Mamah ta kwantar da ita, sannan ta hango thermoflask Allah ya so akwai ruwa a ciki, a ɗan baho ta haɗa tayi mata tapid sponging. Mamah kuwa kuka kawai take yi. Ta rasa meh yake mata daɗi, Ammi kuwa sai aikin lallashi take tana danasanin abinda mutanen unguwar ke yi wa Mamah duk da cewa ita bata ciki.

"Tabbas matar nan na buƙatar taimako kuma zan taimaka mata iya iyawa ta." Ɓangaren Zahrah kuwa Abban Badi'a ne ya riƙe hannun ta suka fita zuwa gidan shi yana Allah wadai da irin halin Idrisu. Tare da fatan Allah ya saka wa iyalen shi da abun da yake musu.

Asubar fari hankalin ta ya dawo jikin ta, ganin ta a ɗakin ƴan gayu yasa ta zaro ido waje. Tunani ta fara MEH ya kawo ta nan sai ta tuna abun da ya faru daren jiya. "Toh asibiti aka kawo Ni kenan"

Ƙafar mutum da taji a kan tata yasa ta duba, "Badi'ah, MEH nake yi a gidan su kumah? Oh ashe jiya Ammin su ne suka taimaki Mamah"

Banɗaki ta nufa wanda yake cikin ɗakin tana mamakin gayu irin nasu Badi'a hala shi yasa ko a islamiyya bata kula Ni saboda gidan masu kuɗi take. Duk cikin ranta take zance.

A hankali ta buɗe ƙofar ɗakin ta nufi waje. Cikin sanɗa ta ke tafiyar kamar wata ɓarauniya.

"Zahrah ina zaki je asubahi haka" Abba ne ya dakatar da ita lokacin dawowarsa kenan daga masjid. Sunkuyar da kan ta tayi kafin tace "ina kwana"

Murmushi yayi "lafiya ƙalau Zahrah, ki koma kiyi sallah in gari ya waye sai ki koma" Bata yi mishi musu ba saboda kwarjininsa. Wucewa tayi simi simi kamar ƙadangare ta koma. Alwala tayi sannan ta ɗan taɓa Badi'a.

Itama tashi tayi ta shiga toilet Tana mamakin meh wannan maras kunyar take yi a gidan su. Sai da ta jira fitowar Badi'a cikin sanyin murya tace

"ki ɗan bani hijab nayi sallah" Bata ce mata komai ba ta buɗe wardrobe ta janyo hijab ta miƙa mata. Buzu buzu tayi sallar Badi'a na mamakin yadda take yi. Sai da ta idar ta ce mata ai ba haka ake sallah ba. Duk rashin mutunci irin na Zahrah sai ta ce toh koyamin.

Sai wajen ƙarfe 6:10am ta koma gida. Abun mamaki gidan tas.. ɗakin Mamah ta shiga. Abun mamaki kwance taga Mamah. Kusa da ita ta zauna can tace

"mamah" Cike da don manta abun da ya faru tace "zahrah! Kiyi wanka da wuri kafin Ishaq yazo." Sarai ta gano Mamah shi yasa tayi shiru abun ta.

Wanka tayi ta fito, a ɗakin ta tarar da Ammi zaune gefen Mamah tana bata abinci, haka kawai ta tsinci kanta da farin ciki maras misaltuwa.

"ina kwana Ammi" "Ɩpia ƙalau Zahrah, ki saka kayan sai ki je ki ɗebo abincin."

Tana shirya wa ta ɗebo abinci taci sai lokacin Ammi ta wuce gida. Mamah kuwa godia tayi ta shaƙa mata.

Da misalin ƙarfe 9:49am yaya Ishaq ya zo gida. Sun gaisa da Mamah kamar ko yaushe cikin sakin fuska. Basu ɓata lokaci ba suka nufi wata private school Mai kyan gaske. Makarantar ta matuƙar burge Zahrah kawai sai ta tsinci kanta da murmusawa..

ALMUNAUWARA ACADEMY

Yara ne ke wasa gwanin ban sha'awa, wasu bisa lilo Wanda da gani nursery students be. Wasu kuma ta wani ɓangaren

waɗanda uniform ɗin su ya bambanta da na sauran wasu na guje guje wasu kuma suna wasanni mabanbanta.

Biye take da yaya Ishaq yayin da zuciyar ta ke mata wani irin sanyi. Yau ita ce a cikin ALMUNAUWARA ACADEMY, “makarantar su Badi'ah fah kenan.” Ta faɗa tana sake wani irin ƙayataccen murmushi.

Daidai wani building suka nufa wanda da alamu shine staff room. Wani room Wanda aka manna signboard jiki ɗauke da “ADMIN" yaya Ishaq yayi knocking, izinin shiga ya samu suka shiga tare.

Sai da ta gaida mutumin kafin ta zauna kamar yadda taga yaya Ishaq ya zauna.

“Mallam Muhammad, Barka da safiya” yaya Ishaq ya faɗa tare da miƙa wa mutumin hannu. “barka mutumi na, wannan ce yarinyar da muka yi magana da kai kenan" “eh ita ce” Wasu takardu ya fitar ya miƙa wa yaya Ishaq. Bayan ya kammala cike su ya ɗauko books cikin wani bag ya miƙa mata.

Haka dai aka gama komai a ranar aka bata uniform ɗin ta set II, farin ciki wurin Zahrah ba'a magana.

“ki jira Ni waje zan yi magana da malamin ku” Ko amsawa bata yi ba ta fice zuwa jikin motar yaya Ishaq ɗin.

“Yauwah Man Please Please ka sanya wa yarinyar nan ido, ina so tayi karatu sosai” “Alright I'll in Sha Allah” Daga haka suka yi sallama. Direct gida ya yi dropping ɗin ta. “ki shiga zan shigo gobe na miƙa ki, ki gaida Mamah" “toh yaya Allah ya kiyaye hanya”.

Kar kuso ku ga murna wurin iya Zahrah! Duk sai wani rawar kai take, Mamah kuwa kallon ta kawai take tana ganin ikon Allah. Yayin da wani ɓangare na zuciyar ta ke tausayawa yarinyar Tata.

Da yamma yaya Ishaq yazo. Sabbin sandals da socks da wata school bag ya kawo mata. yayi mata ƙarin bayani a kan makarantar sannan ya ja hankalin ta kan ta maida hankali.

“cutie na!" Ɗagowa tayi ta kalle shi “ki dage da karatu kinji, ina so ki zama wata abu a rayuwa, ki zama abar alfahari gare mu baki ɗaya. Banda wasa, karatu kika je ba wasa ba, ki saboda haka ki maida hankalin ki ga karatun. Banda kula maza babu ruwan ki da su.... sannan banda faɗa. Kin gane ko?”

“eh na gane, in Sha Allah zanyi karatu da yawa" Murmushi yayi yace “Alright in naji labarin kinyi faɗa, hmmm”

Sallama yayi wa mama ya wuce shima don ya fara preparations na tafiyar shi London don yin masters ɗin shi. Haka kawai yake jin faɗywar gaba ko dan kawai sabon da suka yi da cutien shi ne ko kuwa, “only God knows” ya faɗa can ƙasan maƙoshi.

Washegari tun 6:30 ta gama shirin ta. Kayan sun matuƙar ƙarɓan ta tamkar ɗin ita aka yi, Coffee brown trouser be sai Brown coloured hijab da riga. Sun matuƙar haska kyakkyawar fuskar ta tamkar wata sarauniya.

Horn ɗin da taji ne yasa ta ruga a guje zuwa waje. Ko sallama bata yi wa Mamah ba ta fice abun ta.

Tun daga nesa yake hango ta tana tahowa. Ɗan lumshe idanuwan shi yayi ƙasan maƙoshi ya furta. “She look so breathtaking, tabarakallah”. Tana zuwa ta buɗe motar ta shiga

“ina kwana yaya Ishaq" Cike da zolaya yace “lafiya ƙalau zumuɗa, live kin daɗe da shirya wa.? Ehnn” Fuskar ta ta rufe da hijabi tana turo baki “kai fahimta kace na shirya da wuri” “shine kika biye min?, Damah dai zumuɗin kike yi faɗa min gaskiya cutie" ya faɗa yana ɗaga mata gira..

A haka suka isa sannan ya ja hankalin ta kan tayi karatu in yazo ɗaukar ta zata biya mishi. “bye”

Hannu ta ɗaya mishi sannan ta juya ta shiga. A lokacin ne students da dama ke zuwa. Kai tsaye ita ma shiga tayiba tare da nuna bata san school ɗin ba.

Unfortunately wani staff ya ganta. Da gani bai jin Hausa ma “hey!” ya faɗa yana nuna ta da yatsa.

Wurin da yake ta nufa sannan tace good morning" “morning, are u new here?” It's da bata san ma me yace ba kawai sai

ta ɗan tura baki da ta tuna da new na yace sai tace “yes” “ohk which class?” Wannan kam da yake ta sani caraf tace “jss one”

Da hannu ya mata alamar ta shiga wannan class ɗin “go and keep your bag there” Kai ta gyaɗa kamar ta ji meh yace.

(Nace zaki sani in ya gano baki jin turanci duk buge kike yi)

Yaji daɗin yadda suka yi da malamin kawai sai taji tana son ita ma ta ƙware a turancin nan wallahi. a hankali ta shiga class ɗin babu kowa, kawai sai ta ajiye Baga ɗin ta a front seat ta fita.

Hanyar ta ta fitowa taga Badi'a na tunkaro ajin kawai sai taji tana don jiranta..

“Zahrah a makarantar nan aka saka ki" kai kawai Zahrah ta gyaɗa. Badi'a ta ja hannun Zahrah suka shiga cikin class ɗin, dropping bag ɗin ta tayi ta ɗauko ta Zahrah da ta ajiye a left sided front seat zuwa middle raw daga nan suka fita tare.

Bayan anyi assembly suka dawo class. First period Basu English ne, gashi malamin bashi da kirki duk tsoron shi suke. Yana shigowa suka miƙa gabaɗaya

“good morning sir” “morning how's the weekend?” “fine sir" “ohk have ur seats"

Lesson plan ɗin shi ya ɗauko daga nan ya buƙaci marker daga wurin class rep. Bayan ya bashi ya rubuta TENSES sannan ya juyo “good morning once again, our topic of discussion today is TENSES. Is there anyone who'll tell us something about tenses?"

Shiru class ɗin yayi babu alamar motsi tamkar ruwa ya cinye su. Jin shirun su yasa ya yi pointing Badi'a, “Badi'ah Kabir Umar, please say something” shiru tayi tare da sunkuyar kanta.

“Alright, the girl next to Badi'a say something"

Bata san ma da ita yake ba saboda ba jin turancin take yi ba. Zaro ido yan class ɗin suka fara jin taƙi tashi. Zata jawo musu bala'i wurin Uncle Hashim. Badi'a ce ta ɗan buge ta hakan yasa ta yi tunani ko so take ta faɗa mata MEH abun yake nufi.

(Ku ji Zahrah, ke da baki san komai ba ke zata tambaya?)

Uncle Hashim da ya fusata cikin tsawa yace “you should get out of the class now” still shiru ita ina ta san ma da ita yake. Zaman ta tayi ta ci gaba da jin abun da ake. Ganin duka class sun zubo mata ido yasa ta galla musu harara.

Fita uncle ɗin yayi hakan ya baiwa yan clsss ɗin damar mata magana, wasu na zagin ta wasu kuma na cewa tayi sauri ta fita.

“Zshrah kina ji yana miki magana kika yi banza da shi ko?, Baya wasa ki fita in ba haka ba zaki ji a jikin ki" Badi'a ta faɗa tana ɗago hannun Zahrah alamun ta fita waje.

Kƙememe Zahrah tayi tace “toh Ni na san da Ni yake ne" Ku ji ikon Allah fah

Wannan shine ZAHRAH'S FIRST DAY AT SCHOOL MU HAƊU GOBE DON JIN YADDA ZATA KAYA TSAKANIN ZAHRAH DA KUMA UNCLE HASHIM SHIN MAKARANTAR NAN KUWA TA DACE DA YAR KAWU?

JUST FOLLOW MY INK AND COMMENT & SHARE ITZ DIAMOND LADY _Oum Zainab_

[27/09, 6:07 p.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 0□6□

Wannan shafi naku ne masoya littafin babban gida. Ku ci gaba da bibiyar alƙalamin DIAMOND LADY. Much ƙauna□□

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Uncle Hisham har ya dawo class ɗin Zahrah na zaune kamar ba da ita ake yi ba. Fita ya ƙara yi sai Gashi tare da uncle Suraj (Mr Mugu as hey said). Uncle Suraj na zuwa students suka miƙe suna gaishe shi. Ba tare da ya amsa ba yace su zauna. Kallon su yayi fuskar nan ɗaure kamar fuskar shanu "Among U who's the stupid girl that refused to obey Hashim's order? Ya faɗa in a husky voice nashi.

Zare idon kowa ya fara. Kʼasa ƙasa Badi'a tace "Zahrah don Allah ki tashi ki tsaya in ba haka ba in yʼan aji ne suka nuna ki sai ya miki shegen duka, don Allah ki tashi"

Banza Zahrah tayi mata kamar ba da ita ake magana ba. abu fah yayi abu, Zahrah ba dai taurin kai ba.

Duka su biyun sun tunzura,, hakan yasa suka wuce principal's office. Sanar da shi komai suka yi sannan ya ce su ƙyale ta, shi kuma uncle Hashim ya ci gaba da darasin shi after break za'a nemo yarinyar.

Ba don uncle Suraj ya so ba haka ya haƙura ammah tabbas yarinyar nan zata ci ƙwal ubanta.

Bayan uncle Hashim ya gama clsss ɗin yace lallai Zahrah taje principal's office yanzu. Bata ma San meh yake nufi ba ta dai ji principal kenan ƙarar ta ya kai. Hmm.

Bin bayan shi tayi har suka isa, sai bayan ya shiga ta shiga,

Gaida principal ɗin tayi da turanci, ya amsa mata. Kneel down ya saka ta a gefe yayin da uncle Hashim ke zaune kan kujera..

"What's that your name miss?" principal ya tambaye ta. "Ohoh wannan ai na sanshi" ta faɗa cikin ranta. "Zahrah Abdulkarim Kuru." daga haka tayi shiru. Kamar wanda ya gano bata jin turanci sai ya dawo mata magana da Hausa.

"malamah Zahrah MEH yasa malam ya baki umarni kika ƙi bi?" Kanta ta sunkuyar ƙasa "mallam Ni ban san da Ni yake ba, kuma ban ji MEH yace ba"

Kallon baki da wayo ya mata "kina nufin duk maganar da nayi baki ji ba, ƙarya kike" sai a lokacin ta fahimci ashe ya iya Hausa ma kuma shine da tayi shirin bai yi mata ba.

"Wallahi ban ji ba, Ni bana gane turanci da Hausa kayi min ai zan gane, kayi haƙuri"

Haƙurin da ta faɗa yasa ya sauƙo "meh yasa to baki jin turancin?" "makarantar gwamnati nayi makaman namu ma ba iyawa suka yi ba kuma yau na fara zuwa nan ɗin"

Nan da nan suka sake suna ta hira shi dai PC kallon su kawai yake.

"kina don ki koyi Turancin ko kuwa" "ina so sosai, sai dai ban san yadda zanyi ba" "shike nan kada ki damu zan na koya miki kullum ko abu biyu ne, lokacin break kike zama a aji zan ke zuwa. Cikin murna tace "na gode Mallam" "tashi ki koma class".

Haka suka yi second period ammah lokacin uncle ɗin su bai tayar da ita ba. Lokacin da aka tashi kuwa tana fita taga motar yaya Ishaq, da sauri ta ƙarasa ta shiga.

"yʼan makaranta, hope kin ji daɗin makarantar" ɗan yamutsa fuska tayi kafin tace "ga ta nan dai, Ni kam yau abun kunya dai nayi" Zaro ido yayi jin tace abun kunya "faɗa kika yi ko cutie" "aah Yaya, wani malami ne yake ta min turanci Ni kuwa ban san meh yake cewa ba ashe wai cewa yayi na tashi na amsa tambaya."

MEH yaya Ishaq zai yi in ba dariya ba. Ɓata ran da tayi yasa ya tsagaita. “toh ya kika yi kuma?” Ɗan bakin ta ta turo “ Ni zama na nayi ban kula shi ba shine yace na fita, Ni wallahi ban san da Ni yake ba” “ya zane ki kenan?” “aah ai ban fita ba saboda ban san da Ni yake ba, shine ya ƙira wani mai fuskar shanu ko dariya da baya yi”

“sai kuma shi mai fuskar shanun ya zane ki?” “aah shima cewa yayi na fita to ban san duk a kaina ake ba Ni kuwa nayi zama na, duk sai suka fita tare, shine malamin ya dawo ya ci gaba da darasin, Ni ban ma gane ba”

“shikenan kada ki damu zaki koyi Turanci fiye da malamin in kika sa kanki, mu bi na siya miki wani littafi ki gani” Girgiza kai tayi sannan tace

“baka tambaye Ni ya aka ƙare ba ai" “ina jin ki ai” Shine da ya gama yace muje office ɗin wani ina ga dai headmaster be"

Dariya yaya Ishaq ya saka yace “kai cutie babu headmaster a secondary School sai dai principal" Ranta ta haɗe tamau “toh ai Ni ba sani nayi ba” “shikenan ina jinki, principal ɗin ya duka ki kenan”

“aah shi da Hausa ya min magana shine na ce masa Ni ban fahimci da Ni yake ba kuma bana jin turanci, malamin kuwa yaji tausayi na yace zai je koya min”

Murmushi yayi daidai isowar su wani bookshop. “ki jira Ni ina zuwa”

Ɗauke da littafai a hannun sa ya fito “yauwah karɓi waɗannan cutie, ki riƙe su da iya su zaki ita turanci, sannan ki ƙara maida hankali, duk abun da baki gane ba ki tambaya kinji kar kiji kunyar kowa” “toh"

Ita kaɗai ta shiga gidan shi kuma ya juya. Duk wainar da ake soyawa Kawu bai sani ba.

Bayan ta ci abinci kawai sai taji sha'awar zuwa islamiyya. Wanka tayi ta fito. Ganin yadda uniform ɗin suka cakushe saboda rashin ya sa ta ɓata fuska. “ke kuma lafiya?” Mamah ta tambaye ta Kayan ta nuna mata sai wani tura baki take yi “kiga kaya na kamar daga bakin kura aka amso su” “toh ki shiga gidan su Badi'a ki goge mana kafin lokacin" da kamar bazata je ba sai wata zuciyar ta ce kije.

Sai da tayi nadamar zuwa islamiyya dan kuwa Ustaz Jamil sai da yaci ubanta kan fashi, kuma ya sata duk haddar da yake Binta sai ta biya.

Tun daga ranar kuwa tayi alƙawarin ba zata ƙara zuwa islamiyya ba ko za'a kashe ta, ammah da ta koma gida Mamah tace ai dole sai taje. Tsabagen bakin ciki kamar tayi kuka.

Haka rayuwar Zahrah ta kasance, cikin satin nan kuwa tayi mummunan sabo da ƙawar ta Badi'a yau in suna gidan Mamah to gobe suna gidan su Badi'a.

Ranar Asabat da yammah yaya Ishaq ya zo don yi wa su Mamah sallama. Mamah kam har da kukan ta saboda yace ba lallai ya dawo ba sai bayan shekara biyu ko uku. Uwar gayya Zahrah kuka kamar zata mutu,

“haba cutie, meneneh kuma abun kukan? Ba dai zamu na waya da sabuwar wayar Mamah ba?, Toh kiyi shiru kinji, idan ma kin dage a school in na dawo sai mu tafi tare kema ki shiga jirgi"

Jin yace jirgi nan da nan ta goge hawayen fuskar ta “shikenan yaya zan dage kuma zaka yi alfahari da ni” Murmushi yayi mata sannan yace zo muje ki raka Ni siyayya..

Shopping mall suka je ya siyo mata kayayyaki da mayuka da sauran su. Sandals talkalma duk ya siya mata a cewar shi ko baya nan ba sai ta siya ba. Daga haka suka dawo gida cikin farin ciki. Ranar tare suka yi dinner, sai wajen 9:45pm ya tafi cike da kewar cutie ita ma cutie ya bar ta da kewa. Ko ba komai soyayyar mahaifi da ta rasa tana samun ta wurin yaya Ishaq ga kuma sabuwar ƙawar ta da kuma Ammi har da Abba. Hakan ba ƙaramin daɗi ya mata ba tunda Kawu yanzu ko ya zage ta ba kula shi take ba.

Ƙarfe goma da rabi suka fara shirye-shiryen kwanciya kawai suka ji an banko ƙofar ɗakin.. shaye da mamaki Mamah ke

duban Kawu da ya shigo fuskar shi ɗaure kamr kumburarriyar fulawa. Zahrah ko ko kallon yadda yake bata yi ba. Duban Mamah yayi yana wani cika yana batsewa..

“ke Madina, ina so ki share gidan nan gobe tatas kina ji ko?” Caraf Zahrah tace “toh kaga gidan cikin datti ne da zaka yi magana?” Banu yadda ya iya da Zahrah kawai ya ci gaba da muzuran shi “ni dai na faɗa miki, ɗaki na mah a ciro komai na cikin shi don kuwa gobe dalleliyar amarya ta zata zo gidan nan”

Zaro ido Zahrah tayi lokaci ɗaya yanayin fuskar Mamah ya sauya. Bata ce mishi ƙala ba har ya gama surfa bayanan shi ya fice fuu Kamar Mahaukaci.

Daren Mamah bata samu ta rintsa ba, ba wai saboda kishi ba aah sai don bata san waye Kawu zai auro ba.

Washegari tun safiya Mamah ta cika umarnin Baba, da kanta ta gyara gidan tsab gudun kada taƙi yi ma ya ci mata mutunci gaban baƙin amaryar.

Dawowar Zahrah daga school ta kafa rikici ita ala dole ba zata je islamiyya ba tunda za'a yi baƙi a gidan.

“haba Zahrah, yanzu inda kin zauna uban meyeh zaki yi a gidan” Fuskar ta a kwaɓe take kallon Mamah “mamah naga yau za'a kawo amaryar Kawu, Mamah ina tsoro su zo bana nan nasan ko sun miki abu ba zaki rama ba ammah idan ina nan zan tare miki” ta ƙarashe da Muryar tausayi. “ke yarinya ce Zahrah, idan sun yi min ma a banza suka yi tunda ba kula su zan yi ba, maza tashi ki tafi makaranta.”

Ganin da gaske Mamah so take ta hana ta zama kawai ta ɓare baki ɓaaaaaa sai ihu “wallahi Mamah in na fita ba zan dawo ba, tsayawa zanyi mota ta buge ni shikenan ai koh” ta fice a guje. Mamah da ta rasa abun yi sai tabi bayan ta tana ƙwalla ƙira “zahrah, Zahrah ki dawo shikenan na yadda" duk da ta ji me Mamah tace tayi burus ta ƙara wa bujen ta iska, Mamah na biye da ita har suka kawo ƙofar gida tukun ta juyo. Marakraice fuska Mamah tayi hakan yasa ta dawo ta rungume ta duka su biyun suka fashe da kuka mai ban tausayi.

Sai zuwa yamma tawagar amarya suka zo, ihu da shewa ba'a magana. Sai da suka gama jere suka fito tsakar gida su ka fara zage zage.

“Munafika uwar kishi tayi luƙus a ɗaki” Wata daga cikin matan tayi caraf “kin san damah ba zata fito ba ai. Irin matan nan fah sai Saudatu ta dage, don kuwa ko meh kika musu ba zasu ji haushi ba” Ɗayar matar da ta fara magana tace “toh ai babu zuciya kin sani, shi yasa tayi shiru” Hannu suka tafa suna sake guɗa da shewa irin nan matan barikin nan. “ƙawa ta baki da dama, wallahi gaskiya ne maganar ki, kin san ance bata da dangi, kamar ma Idrisun tsinto ta yayi” “Toh Allah dai ya kiyaye, ammah dole Saudatu ta dage” “ke dai lantana kawai ki bari”

Comment Please

[29/09, 11:16 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 07

Wannan shafi sadaukarwa ne gare ku masoya littafin babban gida. Ku ci gaba da bibiyar alƙalamin DIAMOND LADY. Much ƙauna

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

A kunnen Zahrah suka faɗi komai yasa ta ce “Mamah bari naje banɗaki na dawo” Mamah bata ce komai ba saboda bata

ji MEH suka ce ba. Zahrah na fita ta Banka musu wani bazan kallo mai ɗauke da ƙasƙanci da tsana kafin ta ja wani tsaki “Mtsssss….daɗin ta ma gidan aka zo ana same ta”

Matar da ɗazu aka ƙira da lantana ce ta zaro idon ganin yarinya ƙarama na mata rasar kunya. A fusace ta yo man Zahrah babu shiri ta goje, wani ice ta gani a gefen ta tayi saurin rarumar shi” Lantana Bata haƙura ba ta ƙara biyo Zahrah ai kuwa bata aune ba taji ice a bayan ta. Ƙarar da tayi ne yasa Mamah da sauran yan kawo amarya fitowa.

Tunda ta jinka mata icen ta ja gefe tana sauƙe numfashi, lantana kuwa zube wa ƙasa tayi tsabar azabar da bayan ta yake yi. A hankali Mamah ta tako saboda ta taimakawa Lantana. Hannu ta miƙa mata cike da ƙuluwa ta doke hannun Mamah ta miƙe. Still ta ƙara yin kan Zahrah a fusace

“yau mai hana Ni cin bura uban yarinyar nan shima sai naci uban sa”

Babu alamar tsoro a tattare da ita sai karkaɗa jiki take. A hanzarce Mamah ta taho zata ja hannun Zahrah. Ɗaya daga cikin yan kawo amarya kuwa ta bangaje Mamah.

Abu ƙarami dai ya dawo babba. Don kuwa Zahrah janye Mamah tayi zuwa ɗakin ta. Jawo ƙofar tayi ta fito ta fara by bubbuga musu icen nan, ance Sarkin yawa yafi Sarkin ƙarfi ammah wannan karon naga ikon Allah.

Hayaniyar da ta kaurece ga kuma ihun matan ya jawo hankalin yan unguwar. Tuni gida ya cika ana ta tambayar ba'asi da ƙyar Ammi ta lallashi Zahrah suka wuce ɗakin Ammi. Labarin ya matuƙar ɓata ran Ammin. Saboda haka ta ja hannayen su duka biyun suka bar gidan.

Dare na yi aka kawo amarya tare da ƙawayen ta wanda shigar su kaɗai kaga kaga yan jagaliya, guɗa ce kawai ke tashi sai uban habaici da ake gabzawa wanda wacce suke yi wa bata ma san suna yi ba. Damah tuntuni labari ya isa kunnen Saudatu Kwalba, shi yasa ta tattaro duk ƙawayen ta da niyyar sai sun ci uban uwa da yar, sai dai babu yadda zasu yi takaici ya cika su ganin babu kowa a ɗakin, kenan har sun gudu?. Ai kuwa dabara ta zo wa Aunty Amarya kan in ango ya shigo ta haɗa shi da matar. Ai kuwa ta samu na nasarar hakan. Ran kawu ba ƙaramin ɓaci yayi ba “zasu dawo gidan su same Ni ai"

Su Kawu an ci amarci an gaji da amarci. Kwana biyu su Mamah basu dawo ba nan fah Kawu yasa sha jinin jikin sa.

“Fatan na Allah yasa dai ba aikin da nayi bane ya ɓaci, idan kuwa haka ne toh akwai matsala!” “kai bazai yiwu ba!!! Inaaaah! Madina wallahi bayan barki ba!, Dole mu rayu tare kuma dole kiyi rayuwar ƙasƙaci!.

Yanzu dai ina da zaɓi ɗaya ne, dole na fita ko ina na zaga saboda na nemo su!, Ina sun tafi fa komai ya lalace, duk burin da naci zasu ruguje!!! Zan nemo ku duk yadda kuka je ne”.

Ɓangaren yaya Ishaq kuwa ya keta hazo tare da kewar ƙanwar shi.

Wasa wasa sai da su Mamah suka shafe sati guda a gidan Ammi tukun na suka haɗo domin dawowa, Ammi ta bawa Mamah kayayyakin sakawa nata, na Badi'a kuma ta bawa Zahrah. Zuciyar su wasai suka dawo abun su. Lokacin da suka dawo Saudatu Kwalba na zaune akan shimfiɗar tabarma da tayi, gefen ta kuma ƙawar ta ce Asabe Bala'i sai hira suke yi.

Ɗauke da sallama su Zahrah suka shiga, Asabe ce ta ɗago tare da mamakin da ke bayyane akan fuskar ta sai kuma ta sauƙar da kan ta ƙasa. Ƙasa ƙasa gudun kada baƙin su ji ta tace “ke Kwalba waɗannan su waye” “ina kuwa zan san su waye” ta juyo wurin su Mamah. Ganin sun tunkari ɗakin kishiyar yasa ta miƙe zuwa wajen su. Cike da hatsabibancin ta irin na yan Iskan matan bariki ta wani riƙe kunkumi. “baiwar Allah uban meh zaki yi kin shigo gidan miji na ba izini kin dashi ɗaki kumah?”

Murmushi mamah ta cilla mata wanda yasa zuciyar ta ƙara tafasa. “kut!!!! Ina miki magana, toh don Ubanki jawo hannun yar ku mai zubin aljanun nan ki fita min gida” “a'ah!, Shi mai gidan bai faɗa miki cewa mata biyu gare shi ba?”

Amsar da mamah ta bata ne ya tabbatar mata da cewa ita ce Madina matar Idrisu. Lokaci ɗaya ta shiga ruɗu. Mamah kuwa ta ciro key ta buɗe ɗaki suka shige ita da Zahrah.

Mamaki ya matuƙar kama Saudatu har sai da Asabe ta zo ta ja ta suka wuce ɗaki.. “ke Bala'i ammah idrisu ya raina Ni, irin wannan yaudara haka” “wai MEH ya faru ne?" “ke da kike gani wannan tsuleliyar matar da kika gani da yarinya mai shegen kyau kamar ɗiyar Mayu matar sa ce fah!!” Shaye da mamaki Asabe ke kallon ƙawar ta. “lallai in dai haka ne toh bamu ga ta zama ba” “ai kuwa, yanzu meyeh abun yi?” “rabu da ita kawai, zan bata shekara biyu zuwa uku ta sarara sannan na aika ta lahira shikenan, ɗiyar ta kuma ta zama jaka ta” “Ammah Kwalba bakya tunanin a samu matsala kafin lokacin da kika bata?” “A'ah Bala'i, ba a so a fahimci komai game da mutuwar ta, yanzu haka zan aika a kawo min Bibalo ta dawo waje na da zama ko dan saboda cikar buri na. Idan Bibalo ta dawo nan kinga ai Sa'ar yarinyar ce, xan sa take cin zalin ta kuma na hana ayi magana har baƙin ciki ya kama uwar, daga ƙarshe cikin shekaru ukun da na ɗebar mata ciwon damuwa yayi mata mummunan kamu, sai na sa boka Bulebule ya ƙarasa min ita, daga nan kuma ɗiyar ta ta zama tawa, sai yadda nayi”

Dariya suka kwashe da ita suna tafa hannu “kai ƙawa ta baki da dama!, Kwaƙwalwar ki tana mugun ja” “ke dai ki bari, ko kin manta suna na ne ‘kwalba’?” “hhhhhh haka ne fah, shiyasa nake daɗa ƙaunar ki”

(TOH KUN JI FA KUDIRIN AMARYAR KAWU, KO YA ZA'A KAYA?

Ɓangaren Mamah kuwa suna shiga ta ƙara kaɗe ɗakin ta, ta gyara zaman kayan abincin su da kyau, sai lokacin ta tuna yau da Ishaq ya tafi. Addu'a da fatan alkhairi tayi ta jera masa. Daga nan suka yi zaman su a ɗakin..

“zahrah” jin mamah ta ambaci sunan ta yasa gaban ta faɗuwa don ta San in tayi mata irin kiran nan toh abun is serious. “na'am Mamah ta” “kina ji na koh” “eh Mamah ina jin ki” “ko da wasa ban amince kiyi wa matar kawun ki tsiwa ba, kinga idan kika yi mata zaki jawo mana kawun ki ne shiga rayuwar mu, don Allah Zahrah ki mata biyayya kin ji" Cikin sanyin jiki ta ce “toh mamah naji ammah wallahi idan ta shiga harƙa ta ba zan ƙyale ta ba” “zahrah kenan! Ba zaki taɓa sauya wa ba, baki tunanin gaba ne kam? Yanzu in aka ce bana nan rai yayi halin sa gashi kuma baki da kowa a duniyar nan fah? Su ɗin dai sune dolen ki a lokacin, kuma baki da wanda suka fisu, ya kamata zuwa yanzu ac kinyi koyi da hali na” “haba Mamah Allah ma ya sauwaƙe, Ni zan riga ki mutuwa ma kuma mamah ai ko kin mutu akwai ahalin ki, shiyasa nake cewa Ni ki haɗa Ni da su ko da ace ke ba zaki je gare su ba”

Lokaci ɗaya yanayin Mamah y sauya, abun da take ji a ƙirjin ta Allah kaɗai ya sani, hawaye ne kawai ke zuba daga idon ta. Nan hankalin Zahrah ya tashi don. Ko kaɗan bata son ɓacin ran Mamah. “mamah ta don Allah kiyi haƙuri Ni nayi miki laifi ko" Jijjiga kai tayi don a halin yanzu ko kaɗan ba zata iya magana ba. “shikenan kiyi haƙuri ba zan ƙara tambayar ki ahalin ki ba tunda na fahimci ba kyaso, kiyi shiru haka don Allah” ta ƙarasa itama hawaye na zuba daga idanuwan ta yayin da take goge wa Mamah nata hawayen.

Da ƙyar Mamah tayi shiru sannan ta kamo hannun Zahrah ta ƙanƙame cikin nata tamkar za'a ƙwace mata ita. “ɗiya ta Zahrah, ba wai bana so ki san ahali na baneh sai dai kawai in anyi maganar ina shiga wani yanayi, kada ki damu wata rana da yardar Allah zaki gan su har ki rayu da su” “shikenan Mamah na ta kaina na daina ba zan ƙara tambayar ki ba, to yi murmushi muga" Ta faɗa tana lakuce kumatun Mamah. Nan da nan kuwa suka ware suka ci gaba da hidimar su.

Wajen azahar Ammi ta aiko Badi'ah da basket ɗin abinci ta kawowa Mamah. Sun daɗe suna hira da ƙawar tata kafin ta tafi. Suka ci abincin su kafin su fitar da kayan Masar Mamah su ka ƙara tsaftace su.

Da yamma Mamah ta wuce kasuwa wurin kasuwancin ta, alhamdulillah yau kam da wuri ta gama har aka zo ana neman masa. Da taimakon Lauwali suka dawo. Bayan ta sallame shi ya tafi. Duk abun da yake faruwa akan idon amaryar Kawu, jira kawai take mai gidan ya dawo ta zuba mishi yasha.

Ana yin Sallah sai ga Badi'ah da basket ɗin abinci, Mamah ta amsa tayi godiya sannan ta bata wancan na ranan because it's already washed. Badi'a na shirin fita taji an riƙe kafaɗarta, a tsorace ta ɗago ɗin ganin waye. Murmushi mai ɗauke da ma'anoni ta ke zuba mata.

“yan mata nace waye yake aiko ki kawo abinci?” tun da ga nan ta harbo matar, “kenan wannan ce auntyn Zahrah, tab, tallai akwai matsala dole na sanar da Ammi" jin bata bata amsa ba yasa ta ƙara maimaita mata “yan mata wai waye ke

aiko ki kawo abinci ne” “nimah ban sani ba, sake Ni na tafi gidan kada a neme ni” “kenan ba aiko ki ake yi ba” “eh Ni nake kawowa da kaina, sake Ni" Banu yadda Saudatu ta iya ta sake Badi'a, a tsorace ta isa gida.

“Ammi Ammi Ammi!” “kai Badi'a irin wannan ƙira haka ba ƙaƙƙautawa?” ta faɗa yayin da take fitowa daga bedroom ɗin ta. “Ammi wallahi amaryar gidan su Zahrah abun tsoro ce, kamar ƙaruwa take. Ammi har tsayar da Ni tayi tana tambaya ta wai wa yake aiko Ni na kawo abinci” “subhanallah sai kika ce mata MEH?” “cewa nayi Ni nake Aiko kaina manah" “yauwah good girl, u're very clever daughter, Allah yayi miki albarka” “Amin ameen Ammi na”

Kawu bai shigo gida ba sai wajen 11:00pm na dare, yana shigowa kuwa ya fara washe baki yana nufar ɗakin amaryar shi. Lokacin tayi shirin ta ta zaba kwalliya tamkar zata fita yawon bariki. Da sauri Kawu ya nufi yadda take. Peck tayi mishi haɗi da hugging nashi “sannu da dawowa mai gida na“ Cike da ɗauki yace “yace sannu amarya ta abar ƙauna ta” Ɗan sake shi tayi, “oyah muje kayi wanka kaji” ba musu Kawu ya biyo ta suka fito da yake toilet ɗin su a waje yake. Cike da ƙwarewa a harƙar barki ta kama hannun shi ta raka shi bayan yayi wanka suka dawo tare ta taya sanya kaya. Abincin da Rubber ta aiko musu da yammah ta zuba mishi, bayan yaci yayi hani'an tukun ya ɗago yana kallon amaryar.

“ko wannan matar ko ta dawo” Cikin halin ko ina kula tace “wace mata kenan?” “ina nufin wannan banzar mai ɗakin can” Ita kuwa jin ya ambaci matar shi da banza farin ciki ya mamaye zuciyar ta, cike da murnar samun nasara a Oman ɗin ta tace “eh toh wata jemammiyar mata da yarinya dai sun shigo lokacin ƙawa ta Asabe tana nan, ai ka santa?” Cike da ƙaguwa yace “eh na san Asabe ƙawar ki” “toh matar tana shigowa ita da yarinyar ta suka yo kan mu suna tambayar wacce ce daga cikin mu amarya. Da Asabe ta nuna musu Ni sai suka kwashe da dariya, duk fushi da rashin mutunci irin namu kasa mata magana nayi ina jin ta riga da ta asirce Ni ne” Ta faɗa tana sakin kukan munafurci. Shi kuma sai lallaɓa ta yake kamar wata uwar sa. “yi haƙuri amarya ta ki faɗa min me ke faruwa manah, tabbas duk wanda ya taɓa min ke zai ga fushi ne” Ɗan guntun hawayen ta ta goge ta ci gaba da fuskantar shi “kawai matar sai ta rufe mu da zagi, a nan ta kora Asabe sannan ta juyo kaina, yarinyar da suka shigo tare ita ma ta ɗaurabkan yadda matar ta tsaya sai zagi na suke wai Ni karuwa ce, abun babu daɗi” ta ci gaba da kukan munafurci nata. “shine na basu haƙuri da ƙyar suka haƙura kuma sun ce idan na faɗa maka sai ta min shegen duka. Daga haka ta juya ta nufi ɗakin gefen can naga ta buɗe, sai a lokacin na gane ita ce matar ka da kuma yar ka”

GA FA WANI SALO DA AMARYAR KAWU TA FARA MUJE ZUWA, BA'A FARA WASAN BA. KUYI COMMENTS DA YAWA DON SHINE ƘWARIN GUIWA TA.

ITZ DIAMOND LADY Oum Zainab

[29/09, 11:16 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing   *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 0 8

Bazan manta da ke ba ƙawa ta Murjanatu Abdulwahab Yusuf, ina matuƙar ƙaunar ki saboda Allah. Na gode da ƙaunar ki gare Ni. Ubangiji ya ƙaunace ki.

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Ran Kawu idan yayi dubu toh duk ya ɓaci a fusace ya fita daga ɗakin amarya yayin da ta daka tsalle saboda murnar cin nasara. Yana isa ko sallama bai yi ba ya fara buga ƙofar ɗakin yayi shaye da mamaki maka ta buɗe Bata aune ba kawai taji sauƙar mari s fuskar ta. Bata tsaya ba kawai ita ma ta rama. Mamaki ne ya kama Kawu wai yau shi Madina ta mara don ya mare ta, gaskiya akwai matsala. A kasalance ya koma ɗakin amarya yana huci..

“mai gida ba dukan ta kayi ba koh, bana so ko kaɗan taji haushi na” Murmushin yaƙe yayi “shikenan mata ta damah warning na kashe mata” “yauwah mai gida ammah gobe ya kamata ace an raba mana girki da kuma kwana ko” Shaye da mamaki yake kallon ta kafin yace “ai nikam kullum ina nan, MEH zanyi da waccar matar kuma” “aahmai gida ba za'a yi haka ba, zata ga kamar ina zaluntar ta ne” nan kuwa cikin ranta daɗi take ji. “aah mu bar zancen nan, Ni anan zan je kwana” “shikenan tunda ka ce haka” ta ɗanyi shiru sannan ta ci gaba. “sai batun girki, ai yanzu tunda ta dawo sai a raba“ “ke dai zan ke baki ki girka, ita dama can ita take ciyar da kan ta da ɗiyar ta” Daga haka ya miƙe zuwa gado, su basabun ba Kawu an samu gadin banza. Ita kuwa amarya farin ciki ne fal ranta.

Mamah kuwa tunda ta rama marin da Kawu yayi mata ta fara jin wani sanyi a ranta, kullin da take yawan ji a ƙirjin ta sai taji kamar ya ragu....ɗaki ta koma tayi alwala sannan ta fara jera nafilfilu daga nan bacci ya ɗauke ta. Washegari da wuri suka tashi, Zahrah ta shirya cikin uniform ɗin ta sannan ta zauna jiran Badi'a, ba'a jima ba ta shigo hannun ta ɗauke da basket, “mamah Ina kwana" “lafiya ƙalau Badi'a ya su Ammi?” “suna lafiya, ga breakfast in ji Ammi Zahrah ki samu ki shirya kafin Abba ya gama breakfast” “toh Allah ya amfana, ki gaishe da Ammi” “toh" sannan ta juya zuwa gida. Chips ta zuba a plate ta fara ci, tana gamawa tayi brush ta fito. Sai da ta shiga ta gaida Ammi suka fito ita da Badi'a don jiran Abba. Abba na fitowa suka gaida shi sannan suka tafi sai school.

Rayuwar school tana yi wa Zahrah daɗi a halin yanzu don kuwa cikin sati da ɣan kwanaki ta fara gane darasi sosai, uncle Hashim na yin iyakar iyawar shi wajen ganin Zahrah ta na koyon abubuwa. Alhamdulillah, da yake ƙwaƙwalwar ta na ja tuni tayi nisa. Ga kuma Badi'a ita ma ba'a barta a baya ba wurin taimaka mata.

Yau suna da English, uncle Hashim ya shigo yayi delivering class ɗin shi kuma kowa ya gane daidai gwargwado. Bayan ya fita aka yi sauran three classes ɗin daga nan aka tashe su. Kamar kullum.ya Abba ne ya zo ɗaukar su, suka gaida shi. Bayan su isa gida kowa ta wuce gidan su. Zahrah na shiga taci karo da amaryar Kawu na girki, ɗauke kanta tayi don ita ba mai shiga abun da ba'a sanya ta baneh. Kamar daga sama taji Muryar matar “ɣata babu gaisawa ne?” Harara Zahrah ta cilla mata tare da nufar hanyar ɗakin Mamah. Murmushin mugunta amaryar Kawu tayi sannan ta ci gaba da girkin ta.

Wanka tayi sannan ta ɗauko uniform ɗin ta na islamiyya ta zura..Mamah na fitowa daga bayi daidai isowar Badi'a da abinci ita ma cikin shirin ta na islamiyya. Sannu Mamah tayi mata ta amshi abincin.

Zahrah na gama ci ta ɗauki jakar ta ta fice, da yake islamiyya ba wani nisa sosai daga gidan su yasa suka taka da ƙafa. An samu sauyi sosai don yanzu Zahrah tana maida hankalin ta ga karatun ta na islamiyya, kuma hadda sosai take bayar wa.

Bayan sun dawo daga islamiyya wanka kwai tayi ta sauya kaya sannan tayi wanki. Tana gamawa ta fice zuwa kasuwa wurin Mamah. Sai bayan maghrib suka dawo. A daren suka wanke kayayyakin amfanin su kafin suyi dinner da aka aiko daga gidan Ammi.

Haka rayuwa ta ci gaba a gidan Kawu, babu abun da ya taɓa haɗa Baba Amarya da Mamah har suka shafe watanni uku a gidan sai dai a ɓangaren baba amarya kullum akwai abun da take ƙunsawa kuma har yanzu Kawu baya ciyar da Mamah da Zahrah. A irin wannan lokacin ne su Zahrah suka fara exams, Alhamdulillah an gama kuma sakamako yayi kyau, Badi'ah Kabir Umar ita ce first sai Umar Yusuf sai kuma Zahrah Abdulkarim Kuru. Farin ciki kamar suyi yaya Abba yayi musu kyauta ta Musamman kuma lokacin Hutu Badi'a da Zahrah suka tafi Jos gidan yayar Ammi.

Hajiya Barira yayar Ammi ce, uwar su ɗaya uban su ɗaya. Tana da yara huɗu, yaya Affan, Aunty Fadila, Aunty Aisha sai ƙaramar su Khady.. sun samu tarba ta musamman daga wurin Hajiya da kuma yaranta..

Yaya Affan baya nan yana Cyprus, a can yake karatu, Aunty Fadila da Aunty Aisha su kuma sun gama secondary sun fara karatu a ATBU ammah an saka auren su tare. Khady kuwa sa'ar su ce, yarinya mai ɗan karen kinibibi da rashin ji, rayuwar su a Jos tayi musu daɗi, sai da suka shafe sati biyu suka dawo Bauchi. Abun mamaki duk budurin nan Kawu bai san Zahrah baya nan ba, abinci kuwa kullum sai Ammi ta shigo da kanta ta kawo.

Baba Amarya abun na ci mata tuwo a ƙwarya saboda haka tun da Kawu ya dawo take mishi kuka wai ita ta gaji. “nikam

Soyayyanovels

na ganiii zan bar gidan nan don har ga Allah bazan iya rayuwa cikin sa ba" "yi haƙuri amarya ta meh aka yi miki har kika gaji da gidan" Share ƙwallar idon ta tayi tace "Wannan matar taka bata son zaman lafiya, haka kawai sai ta turo yarinyar ta mai zubin Mayun nan tayi ta zagi na, yarinyar nan har da zubar min girkin da nayi maka wai kowa ya rasa tunda su baka basu, nikam tsiro nake kada wata rana baka nan su yanka Ni" Rungume ta yayi jikin shi "aah ki bar Ni da su, zan hukunta su kuma ba zasu ƙara shiga rayuwar ki ba, ke da gidan ki ai ina kin ce na kora su sai na kaɗa su. "uhm uhm ka bar su zasu ce nayi musu munafurci an kore su, Ni ina son zaman lafiya tare da su, suna bani tausayi" "shikenan zan bar su ammah zan gargaɗe su akan ki don baza su takura miki ba a Cikin gidan ki, Yanzu dai zubo min abinci naci"

Bayan yaci abinci yayi wanka ya nufi ɗakin mamah. Ta idar da Sallah a lokacin tana tasbihi ya shigo bata ko kalle shi ba ta ci gaba da tasbihin ta. "keeee Madina, kwana biyu ina ɗaga miki ƙafa daga ke har shegiyar yaƴar ki zaku takura wa amarya ta. Kar ki ga nayi sanyi kiyi tunanin tsoron ki nake ji, wallahi daga ke har ita Zahrah zan azabtar da kuma fiye da tunanin ku akan mata ta" Daga haka ya fice a fusace, a tsanake Mamah ta bishi da ido har ya fice. Ta girgiza kanta sannan ta maida hankalin ta kan karatun Alkur'ani da ta fara.

Ranar da su Zahrah suka dawo sun dawo da goma sha tara ta arziƙi daga Jos.... kayayyakin sawa da makamantansu duk sun samu ga kuɗin da aka basu. Mamah tayi farin cikin dawowar Zahrah gida don kuwa kullum sai tayi kuka ina ta tuna ta.

Sun koma makaranta lafiya tare da ƙara maida hankalin su a karatun su both ALMUNAUWARA da kuma IMAM MAKIK. Zahrah ta zamo zakara don yanzu ana matuƙar ji da ita cikin school ɗin su. Sam bata shiga sabgar kowa in ba ƙawar ta Badi'a ba, ammah duk wanda ya shiga sabgar ta toh ya shiga sabgar ta bata ƙyale wa.

Ɓangaren Mamah ta ci gaba da suyar Masar ta a kasuwa, kuɗin kuwa tana adana shi saboda gaba, don a halin yanzu babu abunda ta nema ta rasa, abinci za'a kawo tun daga breakfast, lunch har dinner daga gidan Ammi. Sun ɗauke su tamkar jinin su hakan yasa damuwar Mamah ta ragu uwa uba yanzu babu wata alaƙa tsakanin ta da Kawu, sai ya share watanni biyu basu haɗu ba hakan ba ƙaramin daɗi yayi mata ba lokaci ɗaya daga ita har Zahrah suka murmure jiki ya ƙara kyau. Bana amarya ma dai bata shiga sabgar su saboda bata samu damar hakan ba ammah ƙudurin ta yana nan dangane da su.

Tufafi ma dai basu rasa ba saboda Abban Badi'a yana siya musu, school fees kuwa already Yaya Ishaq ya biya mata har kammala junior studies nata.

Wasu lokutan in ta zauna ita kaɗai babu abun da ke faɗo mata sai yaya Ishaq wanda a halin yanzu bata san ya yake ba, ko yana lafiya ko akasin haka. Takan yi mishi fatan alkhairi domin kasancewar shi haske cikin rayuwar ta, sanadiyar shi yanzu ta samu wayewa fiye da da, addu'a kuwa kullum cikin sallolin ta bata mantawa da yaya Ishaq tare da fatan Allah ya dawo da shi lafiya.

Bahaushe yace sannu sannu asarar mai rai yanzu haka Zahrah sun kammala jss 1 ɗin su, sakamako mai kyau mai haskaka wa kowa mamaki yake yadda Zahrah Kuru ta zama popular cikin school ɗin duk da cewa lokacin da tazo makarantar she's nothing but a stupid girl. An now she shines everywhere gata dai yarinya ce ammah akwai ƙwaƙwalwar manya. Hakan yasa ta samu farin jini da ɗaukaka kama daga yaƴan uwanta students, seniors ɗin ta, teachers na baa barsu baya ba hakan duk da taimakon uncle Hashim da kuma Aminiyar ta Badi'a.

WANNAN KENAN TEAM ZAHRAH KUYI FARIN CIKI MUTUNIYAR KU TA DAGE FAH KO INA YAYA ISHAQ HAR YAU BAI NEMI CUTIEN SHI BA? HAJIYA BABS AMARYA FA TANA NAN TANA SHIRI, KO ZATA CI NASARA.

KU BIYO NI TARE DA ALƘALAMI NA DON JIN YADDA ZATA KAYA. BA'A FARA WASAN BA HAR YANZU.

DIAMOND LADY □□ CE (Oum Zainab)

[29/09, 11:16 a.m.] □Diamond Bhatool □: _____★★★_____ Typing □ □ *A BABBAN GIDA* □ _(All in a big family□)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL*□ _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 0□9□

Wannan shafi naku ne masoya littafin babban gida. Ku ci gaba da bibiyar alƙalamin DIAMOND LADY. Much ƙauna□□

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Yau rana ce ta musamman da aka ware a cikin makarantar ALMUNAUWARA ACADEMY kamar yadda ya kasance cikin tarihin makarantar duk shekara akan gudanar da bikin yaye ɗalibai -speech and prize giving day-.

Ko ina na makarantar ya ƙawatu kasancewar makarantar ta yaye masu hannu da shuni ne. A nan aka fara gabatar da programs da ke a agenda na taron.

Cikin programs ɗin akwai drama show da wasu students zasu gabatar. Drama ɗin an shirya ta ne only to motivate the students. Cikin lokaci MC ya sanar da agenda na gaba, wanda shine drama show.

Wani curtain da ya kasance tamkar decoration naga an yaye. Babu abun da ya bayyana sai herarrun seats da aƙalla zasu kai 30 daga can baya. Ta gaba ɓangaren hagu akwai evidence box sai kuma ta can tsakiya kujeru biyu da kuma tables biyu. Ɗaya ɓangaren by the right hand side wasu kujeru ne dake facing waɗannan seats sai kuma can jikin bango babban table da wata lallausar kujera.

Haka wajen ya tsaru, babu ɓata lokaci jama'a suka fara shigowa suna zama a waɗannan seats ɗin. Badi'a ce da kuma khalid suka shigo cikin kayan lawyers ɗauke da files a hannun su. Suna zama sai ga Umar ya shigo ya tsaya near the evidence box.

Maryam kuma ta zauna a seat ɗin dake facing mutanen by the right hand side. Onportunately sai ga Zahrah well dressed in judge's dress, ga kuma wasu sanye da kayan police na biye da ita.

A hankali ta ke takowa har ta iso seat ɗin da aka tanada domin ta. Kowa a lokacin ya miƙe har sai da ta zauna sannan ɗaya daga cikin police ɗin ya miƙa mata files da sauran abubuwa gaban ta.

Ba tare da ɓata lokaci ba ta ciro glasses □ ɗin ta ta sanya, nace MASHA ARRAHMAN, Files ɗin ta fara buɗe wa sannan ta umarci Muhammad da ya karanto cases da suke da shi. Cikin harshen turanci ya fara magana a nutse..

"Case na farko: Ana zargin Mallam Uba Idi da safarar yan mata da kuma miyagun ƙwayoyi tare da lalata wata yarinya da tazo Companyn shi neman aiki wacce a halin yanzu ta mutu. Case na biyu: Ɓarayi guda uku, Dauda, Muhammadu, Idris da shiga gidan wani attajiri don satar daga ƙarshe har ta kai ga kashe mutumin da ahalin sa"

Daga haka ya ɗan rusuna sannan ya zauna. Zahrah da ta make ta ce “su waye lauyoyi” Badi'a ce ta fara tashi haɗe da rusunawa “Suna na Barr.. Badi'a Kabir, nice lauyan Wanda yayi ƙara” sannan ta rusuna ta zauna. Khalid ma ya miƙe “I'm Barr. Khalid Umar, I'm for defense counsel" daga haka ya rusuna.

Cike da ƙwarewa suka yi zaman nan tamkar dai a court ɗin gaske suke gudanar da shari'ar sannan aka yanke wa masu laifi hukunci daidai da laifin su. Daga nan aka sauƙe curtain.

Manyan baƙin mu appreciated the drama sannan sun bada kyaututtuka da dama wa waɗanda suka yi wasan, yayin da wasu suka ware kyauta ta Musamman ga Justice Zahrah Kuru wacce ta matuƙar burge mutane da damah.

Haka aka ci gaba da gabatar da programs har aka kammala. Daga nan aka fara raba prizes. Zahrah ta karɓi prizes sosai ita da Badi'a. Irin prizes ɗin da ta karɓa yasa a wajen wakili Governor ya Bata kyautar garin kuɗi har 100k haka sauran jama'ah suka yi ta mata kyaututtuka na ban mamaki. Anyi taro lafiya an gama lafiya. Lokacin tashi Abba yazo ya ɗauke su sai gida. Mamah da Ammi sun yi matukar alfahari da yayan nasu ammah duk wannan sha'ani da ake yi Kawu da

amarya babu wanda ya sani. Shaye shayen Kawu kuwa sai abunda ya ƙaru...dabar su ma ta dawo tamkar dai da yanzu kuwa har shiga cikin gidan suke yi saboda samun dama daga Bana amarya.

Ranar Monday suka je makaranta. Principal ne ya aiko a ƙira mishi Zahrah Kuru. A tsorace ta fito daga class ɗin su ta nufi office ɗin principal da sallama ɗauke a bakin ta ta shiga bayan ya bata umarnin hakan

“good morning sir" “morning Zahrah, how's studies?” “Alhamdulillah sir. I was informed that u want to see me”

Ba tare da ya bata amsa ba ya ɗaya phone ɗin shi ya kara a kunne, bayan few seconds aka yi picking. “Assalamu Alykum" baa jin meh ake cewa daga ɗaya ɓangaren daga bisani ya miƙa mata wayar. Ba tare da ta san wanene ba cikin Muryar ta mai daɗin sauraro tayi sallama. A lokacin kuma principal ya fita daga office ɗin.

Jin Muryar cutien shi ya sake wani murmushi mai ɗan sauti “wa alykumussalam cutien yaya” Bata san lokacin da ta cilla wani ihu ba saboda farin ciki sai kuma hawaye sharrrr “aah cutien yaya kuka kike yi? Toh shikenan lemme hang off the call and I won't call again” Da sauri ta share hawayen ta kamar tana gaban shi “i'm sorry yaya Ishaq, kukan farin ciki ne, ina kwana ya karatun" “Alhamdulillah cutie, ya Mamah?” “lafiyae ta ƙalau, kusan kullum sai tayi jajen ka” “Ayyah ki gaishe ta zan aiko muku saƙo in Sha Allah” “toh Yaya mun gode, i thought har ka manta da mu" “ni ina na isa na manta da ƙanwa ta!, Rufa min asiri kullum cikin kewar ku nake" Murmushi mai ɗan sauti tayi daga ɗaya ɓangaren yace “ba wannan ba dai cutie, jiya naji abun alkhairi da kika yi, kuma na gani. Ina alfahari da ke ƙanwa ta, ki ƙara dagewa Please” “in sha Allah yaya” “shikenan sai anjima, damah I called only to complement on your performance and I'm proud of you zahrah" “thank you yayah, bye”

Daga haka ƙiran ya katse. Principal ne ya shigo tare da uncle Hashim da uncle Suraj. A nan kowa ya yabe ta tare da faɗin irin alkhairin da makarantar ta samu sanadiyyar drama show ɗin su, Governor daga baya da kanshi ya aiko wa makarantar saƙo kuɗaɗe masu yawa haka manyan mutane suka bada kuɗaɗe su mah. She's totally speechless on how victorious she's, and she promised to do better than this. Daga ƙarshe yace ta turo baban ta domin karɓa mata kyaututtukan da ta samu, in ta fita ta kira mishi Badi'a. “ohk sir" daga haka ta fice zuwa class. Badi'a ma same message aka yi passing mata. Finally they decided to send Abba, don ita ko karen huka ne ya cije ta ba zata taɓa turo Kawu matsayin wani nata ba. Toh me mah ya kai ta? Mutumin da bai san ci ko shan ta ita da mahaifiyar ta ba a matsayin shi na wadda hakƙin su ke a wuyan shi, bai don ko da lafiyar su da rashin ta ba. Inaaaah ba zata taɓa ba ko da kuwa alkhairi zai wuce ta ne.

Haka har lokacin tashi suka koma gida daga nan suka tafi islamiyya. Bayan sun dawo kowa ya wuce gidan su.

★★★★★★★

Tafiya suke ita da Asabe Bala'i cikin wani ƙungurmin daji wanda ke da matuƙar duhun tsiya suna tafiya suna sare ice saboda irin bishiyoyi masu canopy ɗin an ne a ciki. Sunyi tafiyar da ta kai kimanin 2hours kafin su iso wajen wani old building Wanda ke zagaye da wasu bishiyoyi masu baƙaƙen leaves. Daidai ƙofar wajen suka nufa.

Tsawa aka buga musu “kai!!! ba'a shigowa nan da ƙafar damah! Ku fice” A tsorace dukan su suka juyo don irin yadda Muryar ta kasance maras daɗin sauraro da kuma mugun tsoratarwa...

“zaku iya shigowa yanzu ammah kada ku kuskura ku shigo min da ƙafafun dama” A ruɗe suka shiga kamar dole. Wani irin gini ne maras kyawun fasali, jikin ginin baƙi ƙirin ga wasu ƙwari baƙaƙe dake yawo jikin ginin, duhu ne ya mamaye wajen lokacin ɗaya suka rasa inda da zasu sanya kansu yayin da suka ji wata guguwa ta tashi, rumtse idanuwan su suka yi sannan suka ji iskar ta janye su zuwa wani sashe. Lokaci ɗaya haske ya bayyana a wajen, suna buɗe idanuwan su suka gansu zube gaban wani mutum mummuna..

Idan nace muni to fah munin ya wuce misali, fuskar shi ne baƙa ƙirin ta yamutse ga uban gashin kai kamar na wata baindiya sai dai nashi babu alamun gyara, gemun shi ya kai saitin guiwar shi Tsayin sa kuwa ba'a magana haka girman jikin sa ya wuce misali. Sam ba shi da daɗin gani. Dariyar shi ce ta ƙara tsoratar da su suka fara zazzare idanuwan su kamar waɗanda suka yi wa sarki ƙarya.

“Hhhhhhh.....Saudatu Kwalba tare da ƙawar ta Asabe Bala'i. Hhhhh...hhhhhhh.....barkan ku da zuwa fadar Bulebule Bokan kowa hhhhhhh....hhhhhhh....” “mun go....de...ran....ka..shi...daɗe....”

Lokaci ɗaya ya haɗe fuskar shi ya fara duban su. “Kwalba kin zo akan kishiyar ki ko?" Cike da mamaki ta ɗan kalli boka Bulebule. “kin zo ne akan ta mutu ammah ba yanzu ba sai nan da shekara biyu sannan ki mallake mijin ki da kuma yar ɗan uwan sa zahrah”

“eh haka ne ranka shi daɗe ka taimaka min” “shikenan kada ki damu"

Wata ƙwarya ce ta bayyana a gaban shi, cikin ta ya fara surkulle yana furta wasu maganganu. Can ya buga kwaryar nan da nan ta ɓace

“Akwai matsala! Matar nan ba zata mutu ba sai dai zanyi miki wani aiki da zata haukace, idan ta haukace ita da kanta zata fara jinya sai ta gudu ta bar gidan. Ita kuma ɗiyar ta zaki mallake ta ammah akwai babbar matsala don kuwa akwai manya manyan sheɗanu a tattare da ita wanda Ni kaina tsoron taɓo su nake. Mijin ki ki sa a ranki kin mallake shi. Hhhhh....hhhhhhh...hhhhhhh..”

“yauwah ranka shi daɗe na gode sai kuma kuɗin aikin" Dariya yayi sannan yace “bulebule baya karɓar kuɗi kasafai sai dai ladan aiki da zaki bashi wanda ya kasance mai sauƙi. Zaki zauna a tare da ni na kwana biyu, zan yi amfani da ke sau biyar” Ba tare da ta damu ba tace “shikenan ranka shi daɗe na gode”

“ke Asabe zaki iya tafiya ita sai nan da kwana biyu ammah in kina so zaki iya zama zan baki ɗaki kema anan” “shikenan ranka shi daɗe zan kwana a nan ɗin”

(Authubillah!!! Annabi Muhammad Sallallahu alaihi Wasallama yace :duk wanda yake wurin ɗan duba, ko kuma boka, kuma ya aminta da abun da ɗan duban ya faɗa masa toh haƙiƙa ya kauracewa abun da aka sauƙin min”

Mata muji tsoron Allah mu sani mutuwa tana nan tana jiran mu, MEH yasa in muna da bukata bazamu riƙa wurin Allah ba? Shi fah in ka roƙe shi zai amsa maka kuma baya gori dan ya baki. Saboda haka ki kiyaye in son mallake mijin ki toh ki kyautata masa da haka zaki sace zuciyar sa kai har ma da ta dangin sa matsawar kina kyautata musu.

Allah ya tsare).

★★★★★★★

Abba da kan shi ya amso musu kyaututtukan su. Cike da farin ciki ya dawo yana nunawa Ammi. Sunyi farin ciki da nasarar yaran musamman Zahrah da ta kasance babu mai tsaya mata damah. Sai da yammah dab da dawowar su daga islamiyya suka wuce zuwa gidan Mamah.

Tabarma ta shimfiɗa musu “sannun ku da zuwa maraba lale” “sannun mu Maman zahrah” Bayan sun zauna ta ɗebo musu ruwa. Ba tare da nuna ƙyama ba Ammi ta kurɓi ruwan. “ina wunin ku ina gajiya” “lafiya ƙalau Maman Zahrah" “ya hidima kumah, Allah dai ya saka muku da alkhairi Abban Badi'a" “amin babu komai Maman Zahrah ai yiwa kai ne," Murmushi mamah tayi. Abba ya gyara murya sannan ya fara magana “toh kamar dai yadda kika ganmu a nan mun zo ne don taya ki murna bisa nasarar da Zahrah ke samu a makarantar su ta boko. Shekaranjiya anyi tarin yaye ɗalibai a makarantar tasu, toh a nan ta samu kyaututtuka da dama, akwai kuɗaɗen ta kimanin Naira Dubu ɗari biyu (200k) Wanda ta samu daga wurin manyan mutane a faɗin jahar da kuma wajen ta. Saboda haka ne ma na amso musu saƙon ita da yar waje na Badi'a.”

Cike da farin ciki Mamah tace “madallah Allah ya saka da alkhairi Allah yasa mai amfani ne” Ammi ta amsa da “Ameen” “toh saboda haka ne nake ganin MEH zai hana kije ki buɗe account sai a zuba miki kuɗin a ciki” girgiza kai mama tayi “Aah Abban Badi'a ba za'a yi haka ba, kawai ka riƙe kuɗin a wajen ka ina ga zaifi. Idan a waje na ne zai iya salwanta a banza ammah idan a wajen ka ɗin ne kamar zai fi. In yaso in an tashi amfani da shi sai ayi nan gaba"

Abba bai Musa da shawarar Mamah ba haka Ammi. Girman ta kuwa a idon su ya ƙara ƙaruwa. Daga nan suka yi sallama suka wuce gida.

TOH GA FA BABA AMARYA DA KUMA TUGGUN TA GA MAMAH DA ƊIYAR TA GA KUMA YA ISHAQ SHIMA ASHE YANA NAN.

KU CI GABA DA BIBIYAR ALƘALAMIN DIAMOND LADY DON JIN YADDA ZATA KAYA COMMENTS DIN KU KAWAI NAKE SO SABODA SHINE ƙWARIN GUIWA TA. DIAMOND LADY CE □□ Oum Zainab.

[29/09, 11:16 a.m.] □Diamond Bhatool □: _____★★★_____ Typing □ □ *A BABBAN GIDA* □ _(All in a big family□)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL*□ _____★★★_____

□

PROLOGUE

PAGE 1□0□

Bazan manta da ku ba ɣan uwa na kuma rabin jiki na Aminatouh Adamu Hassan (Dr. Meenal) Sa'adatu Adamu Hassan (Shaheedah) A'ishah Saleh Uthman da kuma Safiyya Saleh Uthman (Autar Umma)

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Haka rayuwa ta ci gaba da tafiya, yau daƈi gobe akasin haka. Tun ranar da BABA AMARYA ta dawo daga wurin boka Bulebule komai ya sauya a gidan nan. Cikin sati guda ta fara shimfiƈawa Kawu sarautar mulkin ta a gidan, tana cewa abu har rawar ƙafa yake don yayi mata. Wannan shine mafarin zancen.

Zaune take akan taburmar da ta shimfiƈa yayin da Kawu ke mata tausa a tsakar gidan. “mai gida tashi ka ƈaura mana sanwar nan manah don Ni na riga da na gaji” Da sauri ya miƙe kamar mai cika umarnin mahaifiyar sa ya fara haƈa ice cikin murhu. Ba don komai ta sashi ba sai don kawai haka tayi ra'ayi. Da ƙyar wutar nan ta kama ammah haka tace ya daure yayi musu girkin nan. Tun bai wuce 11:20am aka fara girkin ba har 1:00pm da ƈori ba a saka shinkafa ba.

Lokacin da Zahrah ta dawo daga school tayi arba da Kawu na girki. Shewa ta buga sannan tayi hanyar ƈakin Mamah tana dariya. Batayi tsammani ba sai jin Muryar shi tayi yana ƙwalla mata ƙira..

“Zahra'u zahrah'u”.....babu alamun zata tsaya ballantana na ta amsa ta wuce ciki abun ta. Kamar yayi kuka haka ya tasa tukunya da murhu a gaba, gashi babu yadda ya iya tunda gimbiya ce ta bashi girkin.

Ana cikin haka Badi'a tayi sallama da basket ƈin abinci a hannun ta, a hanzarce ya miƙa ya zo gaban ta yana miƙa mata hannu. “ƈan matsa zan wuce” “kawo na shiga da shi” da ƙyar Badi'a ta danne dariyar da ta kama ta sannan tace “gyara na wuce ko sai na yi wa bodyguards ƈina magana” kasancewar bai san ta ba kuma yaga ɣar gayu yasa yayi tunanin da gaske ne. Direct ƈakin Mamah ta miƙa abincin sannan ta fita.

Kawu da ya gama galabaita ga rana, ga zafi ga hayaƙi in Banda zufa babu abun da ke ketowa daga jikin shi. Bana amarya kuwa ta tsare ina bai dafa ba ko ta dafa ba zai ci ba don ba bashi zata yi ba.

“kiyi haƙuri kizo ki amshi girkin nan, Ni babu abunda zan iya wallahi yanzu haka na wahala” Hararar shi tayi ta gatsina hanci tukun tace “ita waccar ta ƈakin uban meh take yi a gidan da bazara dafa ba, maza je ka taso ta”

Zungui zungui babu kunya ya ja ƙaton kanshi zuwa ƈakin Mamah. Lokacin kuwa sun zuba fried rice da kuma papper meat da aka kawo daga gidan Ammi suna ci. Yawun Kawu duk ya tsinke ammah ya dake. “madina ki fito in ji amarya kiyi girki” Idan gini na magana toh, Mamah ko kallon shi bata yi ba gashi yanzu duk jin zuciyar sa yake yi a mace ba zai ma iya dukan ta ba. Ya fi 10minutes yana jira ko zata fito ammah shiru, hakan yasa ya ja dogon ƙafar shi ya koma wajen bana amarya. Marairaice mata fuska yayi “don Allah gimbiya kiyi haƙuri ki zo ki ƙarasa, gaba ƈaya sun ƙi kula Ni su ma.

(Nace ah su Kawu anyi luƙus kenan”

Harara ta ƙara banka mishi “toh ita ƈin uwar ka ce da ba zaka ce ta fito ba, koma kace ta fito” haka ya ƙara komawa

kamar ɗan ta. “tace wai ki fito" banza Mamah ta ƙara yi mishi. Babu yadda ya iya ya ƙara dawowa. Wasa wasa abinci har 3:00pm ba'a zuba shinkafa ba. Da ya gaji kawai ya fice shagon gyaran babur da yake ya zauna Allah ya taimake shi wani ya kawo gyara sannan ya samu ya ci abinci.

Haka rayuwa ta ci gaba da tafiya, duk shekara sai lashe kyaututtuka masu yawa daga makaranta da kuma wajen makaranta. Yanzu har su Zahrah suka shiga aji uku (jss 3) kwacakwam hankalin su ya koma kan karatun su, gashi Badi'a na shirin yin sauƙa saboda damah can tayi wa Zahrah nisa.

An samu sauyi cikin gidan Kawu sosai don kuwa yanzu Kawu ya zama dolo, babu abun da ya isa yayi sai da umarnin baba amarya. Ya bi ya rame har abun tausayi ammah hakan bai taɓa zuciyar Zahrah ba.

Yaya Ishaq har yau shiru babu shi, sai dai wasu lokutan ya kan kira wani staff ya haɗa shi da Zahrah. Su Zahrah an girma,duk ƙiriniya irin ta Zahrah yanzu babu, ko dan ance zama da maɗaukin kanwa wai shi ke kawo farin Kai. Toh Zahrah ma dai ta sauya. Ga wani irin kyau da take yi yanzu wanda ake kira da ƙyalƙyalin yan matanci....ta ko ina Zahrah batada makusa. Idan kyan fuska ne toh Zahrah ƙarshe ce, kana ganin ta kaga fuskar Mamah kamar anyi copy sai dai Mamah da yake wahala ta dafar da ita yasa Zahrah ta fita haske sosai. Uwa uba wani rashin don magana da Zahrah ta ɗauko abun mamaki idan har kaga tana magana toh an taɓo ta ne. Hakan ba ƙaramin ƙara mata kwarjini a idon ƙawayen ta yayi ba don kuwa kowa shakkar ta yake.

Zahrah ce zaune a class yayin da mates ɗin ta suka kewaye ta tana kwatanta musu yadda ake solving wani equation a maths, da ƙyar suka samu suka fitar da amsar. Bayan sun gama ne ta ci gaba da koya musu sauran abubuwan da suka kamata. Aikin su kenan kullum a school yanzu idan sun je saboda an ma daina shiga clsss ɗin su.

A lokacin exams kuwa Zahra ta nutsu ta rubuta abun ta. Bayan an kammala aka sallame su har sai result ya fito za'a neme su don yin registration na senior class, ranar sunyi kuka iya kuka saboda wasu ba a nan zasu ci gaba da karatu ba. Zahrah na ɗaya daga cikin waɗanda suka cire tsammanin dawowa ALMUNAUWARA don ci gaba da karatu duba da sponsor nata baya nan kuma babu alamun zai dawo, kuɗin kuma yafi ƙarfin mahaifiyar ta. “Dole zan koma government school ne na sani ammah Alhamdulillah for these three good years I've learned a lot” Da haka ta lallaɓa zuciyar ta tare da fauwalsws Ubangiji komai. Yanzu iya islamiyya suke zuwa. Zahrah ta maida hankalinta sosai kan karatun addinin ta, wanda ya kawo sauyi mai kyau cikin rayuwar ta.

Rayuwar ta haskaka sosai, a da Zahrah bata iya riƙe bakin ta duk maganar da ta zo mata ko a waye kwaɓa mata take yi ammah yanzu Alhamdulillah an samu great improvement don kuwa a rana maganganun Zahrah ƙirgaggu ne, sanadiyyar islamiyya yanzu Kawu yana cin arziƙin gaisuwa daga gare ta, haka baba amarya ma idan ta ganta takan gaishe ta. Sana'ar Mamah ta ja baya sakamakon jinya da take yawan yi yanzu sauƙin ta ma suna samun abinci ko da yaushe ga kuma kyakkyawar kulawa daga sabon ahalin su. Jinya abu yaƙi ci yaƙi cinyewa, an je asibiti abu yaƙi yiwuwa. Duk san ɗin da za'a yi sai ya nuna normal hankalin Zahrah duk ya tashi. Damuwa ce fal a ranta ga wata dama da ta fara yi.

Fahimtar haka da Ammi tayi yasa ta yanke wata shawara ita da mai gidan ta. “Ni wallahi Abban Badi'a abun ya ɗaure mun kai, mutum mai lafiya lokaci ɗaya sai jinya, duk da cewa ba abun mamaki baneh kaɗan daga hikimar Ubangiji ammah jinyar Maman Zahrah akwai sa hannu astaghfirullah, a ce duk wani investigation da aka yi sai ya nuna normal bayan kuma gata nan tana jin jiki” “ni kaina nayi tunanin hakan, ita wannan mata gaskiya tana ganin jarrabawar rayuwa, kiga fa mijin ko sau ɗaya ban taɓa ganin an zo da shi ba” “wallahi kuwa Ni haushi yake bani daga shi har amaryar tasa mai zubin karuwai. Wallahi haƙƙin Madina da ɗiyarta kaɗai ya ishe shi, da sannu zai fahimci hakan tun anan duniya. “Allah zai saka musu kam” “Ammah Ni ina da wata shawara fah, ko za'a gwada ISLAMIC medicine me?" “shawara Mai kyau sai mu gwada ai.”

Tun da aka fara ISLAMIC medicine ta ɗan fara samun sauƙi, sai dai yanzu ta fara wasu irin surutai musamman ina tana bacci. Wani lokacin Zahrah sai dai ta zauna tayi ta sharar kukan ta daga ƙarshe ta ɗaura da yiwa Mamah addu'a.

Yau da safe Zahrah na zaune gefen Mamah yayin da take bacci kawai taji Muryar Mamah na magana. “Tabbas na riga na cuci rayuwa ta da na gudu na bar dangi na wanda bana jin har abada zan ƙara ganin su, Alhaji Baba da kuma Hajjaty ina

roƙon ku yafe min bana jin zan iso gare ku mutuwa zata riske ni.... Nan da nan jikin Mamah ya ji ƙera da zufa sai wani karkarwa take yi. Addu'a ta tofa mata nan da nan taci gaba da bacci ta.

“Tabbas akwai ɓoyayyen al'amari game da rayuwar Mamah na, ya Ubangiji kafi kowa sanin ɓoyayyen al'amari da kuma bayyananne, ya Rabb! Ka bawa mahaifiya ta lafiya ka kuma bani ikon haɗa ta da dangin ta” ta ƙarasa hawaye na zubowa daga idanuwan ta.

Kwanci tashi asarar mai rai Mamah ta shafe wata guda tana jinyar da aka gagara gano wace iri ce, a lokacin kuma baba amarya ta fara shiga tana gaishe ta kullum. Ita dai Zahrah bata kawo komai a ranta ba don yanzu babu laifi suna gaisuwar mutunci da BABA AMARYA ɗin.

Ana cikin haka result ɗin su ya fito, a ranar kuwa suka dukufa zuwa school bisa tursasawar Ammi. “Zahrah ki tashi kije ki shirya a can tare da Badi'a kuje school za'a buɗe muku result” cikin fuskar dake bayyana tsantsar damuwa tace “Ammi don Allah ki barni na zauna a nan tare da Mamah, Badi'a sai ta duba min" “Aah Zahrah tashi zaki yi ku tafi, ina nan zan kuka da mamah”

Babu yadda ya iya ta wuce gidan Ammi a can suka shirya suka shiga adaidaita saboda Abba ya tafi Kaduna. Suna isa ganin classmates ɗin su Zahrah ta ɗan ware, ihun murna suka yi da suka hango Zahrah da Badi'a. Da gudu suka rungume su tamkar zasu faɗi ƙasa.

Murya uncle Hashim me ta dakatar da su “Hey! Are You alright?” waskewa suka yi suka ce “yes sir” Yace “Alright You guys should FOLLOW me to the computer library so that your results will be checked”

Yana tafe suna bin bayan shi har suka iso. Ɗaya bayan ɗaya ake dubawa kuma Alhamdulillah duk duk sun samu abun da ake so na tafiya senior class. Badi'a ce second to the last, Tana fitowa tayi hugging Zahrah “best frightful and colourful result” Tsalle Zahrah tayi “Alhamdulillah, bari na dubo nawa ki jira ni”

Kamar yadda Badi'a ta fito da gudu haka Zahrah ta fito da gudu “Awful and marvelous result" Farin ciki tamkar su yi yaya.

[29/09, 9:21 p.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 1

Wannan shafi naku ne masoya littafin babban gida. Ku ci gaba da bibiyar alƙalamin DIAMOND LADY. Much ƙauna

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Bayan an duba wa kowa PC ya haɗa musu assembly.

“Good day to you all our graduating junior students, you indeed deserved to be honored because you all perform well an fantastic.” Tap tap tap sukafara tafi “The most amazing part of your success is that three students from this school were honored with money .” Tap tap tap “I'll like to see Mayam Muhammad on the stage” M² ta fito a natse, “the state's board of junior secondary School examination awarded 100k to you for your wonderful performance and this school specifically honored you scholarship in to the senior class.”

Nan da nan ihu ya kacame sai tafi Tap tap tap A hankali ta koma tana murmushi.

“Badi'ah Kabir Umar, shi also perform wonderfully in this exams the board awarded 300k to you, congratulations Badi'a,

and to you also the school management awarded a scholarship to you in to the senior class”

Ihu ta ka ina da ƙyar suka yi shiru.

“The champion, Zahrah Abdulkarim Kuru being the overall best student to write this JSSE in this state at large was awarded the sum total of 500k and same, management of the school awarded a scholarship to you"

Murna ta ko ina sai da PC ya tsawatar musu suka yi shiru.

“Congratulations to you all, I hope you'll improve and do better next, Maryam, Badi'a, Zahrah see me in my office" Daga haka kowa ya watse yana farin ciki bayan an raba musu admission letter nasu da deadline na registration ɗin. Zahrah tafi kowa yin farin ciki ko babu komai Ubangiji ya kawo mata mafita. A office ɗin PC aka ɗauki pictures nasu aka ce su turo iyayen su gobe before a sallame su. Daga haka suka wuce. Abba, Mamah ammi duk sunyi farin ciki.

Alhamdulillah jikin Mamah yayi sauƙi kwanan nan saboda amfani da magungunan ISLAMIC da take yi. Yayin da suka fara sabawa da baba amarya.

Da yake babu registration bana, on their resumption day sassafe suka fice don yanzu Abba ya samar masu driver da zai ke kula da zuwan su da komawar su. Direct old ss1 suka nufa. Around 7:30 kuwa sauran students suka fara zuwa, da yawa sun dawo ammah wasu sun sauya school ne wasu kuma barin gari zasu yi. Bayan anyi assembly Uncle John who's the only Christian cikin staff ɗin su ya fara shigowa. “good morning sir” “morning, sit down” Bayan sun zauna ya fara yi musu bayani cikin harshen turanci. “Ina yi muku Barka da shiga ajin senior. Fatan zaku ƙara maida hankula ku ga karatun ku. Shi wannan aji da kuke gani na senior mataki ne daga cikin matakan rayuwa, idan kika tafka kuskure cikin sa yana iya wargaza ƙaddarar rayuwar ki. Saboda haka ku nutsu ku san MEH kuke yi”

Nan ya ci gaba da bayani wanda a fakaice career guidance ya Basu. Cike da zumuɗi da farin ciki bayan ficewar Uncle John suka fara magana.

Zainab Sani tace “Ni fah da kuke gani tun ba yau ba na riga na ware abun da zan karanta nan gaba. A rayuwa ta ina matuƙar ƙaunar yadda Nurses ke kula da maras lafiya. The way they show their concern, care and love to their patients drove me to like the profession”

Idanuwan su suka zuba mata yayin da ta ci gaba da bayani. “kun san MEH, yadda suke salwantar da lokacin su don kula da patients, Baku gani doctors zuwa kawai suke na wani lokaci su tafi, ammah Nurses suna yin 8hrs suna kula da patients da zarar wata ta tafi wata zata zo saboda kada abar patient a haka. Da wannan profession ɗin zaki samu lada da yawa, sai ki samu aljanna sanadiyyar su”

Kowa ya gamsu da bayanin Zainab. Ɗan gyara zama Zahrah tayi tace “Babban buri na a duniya bai wuce na zama cikakkiyar alkaki wato judge mai cikakken iko ba. Ina so naga ko yaya mai laifi yake an hukunta shi. Akwai wani babban rabo a rayuwa ta da yasa nake don ganin duk mai laifi ya karɓi hukunci daidai da laifin shi.”

Shiru kowa yayi yana nazarin Zahrah. Sun daɗe suna ta maganganu game da career nasu. Har lokacin tashi yayi Duk malamin da ya shigo maganar da yake yi musu kenan tare da basu shawarari kan yadda zasu yi karatun su successfully.

Bayan Zahrah ta koma gida ta tarar da jikin Mamah babu daɗi. Ina banda kuka babu abun da take yi tana roƙon Ubangiji da ya bawa Mamah lafiya. “mamah tah! Ke kaɗai ke gare ni bayan Allah. Don Allah Mamah na ki tashi ko kaɗan bana son rasa ki.”

Cikin bacci taji kukan Zahrah ita ma lokaci ɗaya hankalin ta ya tashi. Cikin Muryar ciwo ta kamo hannun Zahrah “Ɗiya ta! Ki sani kowanne rai sai ya ɗanɗani mutuwa, dole ko ban mutu yanzu ba zan mutu nan gaba. Addu'ar ki kawai nake buƙata Zahrah! Ke kaɗai Allah ya bani kuma ina da burin zuwa ga ahali na sai dai na kasa. Amma ke bazan so ki ci gaba da rayuwa tare da wannan maras imanin ba ko da kuwa bayan raina ne.

Yanzu ki tashi ki shirya ki tafi islamiyya"

Maganganun Mamah sunyi matuƙar tasiri a zuciyar Zahrah, gyara mata shimfiɗa tayi ta zuba abinci a plate sannan tayi feeding Mamah. Sai da ta bata ruwa ta tabbatar ya tsirga kafin ta kwantar da ita. A gaggauce ta samu ta shirya gashi lokaci ya kusa ƙurewa. Sallama tayi wa Mamah ta wuce gidan Ammi.

Ammi kaɗai ta tarar a parlourn zaune tana kallo. Da sallama ta shiga sannan ta zauna jikin ƙafar Ammin. Cikin Muryar ta mai sanyi tace “Ammi ina yini” Murmushi Ammi tayi tana yabawa da nutsuwa irin ta Zahrah wacce lokaci ɗaya ta zo ba tare da tsammani ba tamkar wahayi. “lafiya lau zahran Mamah, ya jikin mamah” “da sauƙi” “toh Allah ya ƙara sauƙi, Badi'a Badi'a ki fito manah tun ɗazu Zahrah ke famar jiranki” Daga room ɗin ta ta ce “sorry zahrahty gani nan zuwa”

Bayan Badi'a ta zo suka wuce islamiyya. Yau gabaɗaya Ustaz ya kasa fahimtar Zahrah, fuskar ta ɗauke take da zunzurutun damuwa. Zuwan ma kawai tayi ne ba wai ɗin taso ba. Gani take kamar ina ta bar Mamah mutuwa zata zo ta ɗauke ta.

“Zahrah! Zahrah!! Zahrah” bakin shi uku ammah bata amsa ba. Babu alamun ma ta san MEH ake ko a Ina take. Badi'a na taɓa ta ta zabura sai wani zare ido take yi. “zahrah baki da lafiya ne yau gabaɗaya hankalin ki baya kan aji. Baki na yafi uku ammah baki san ina yi ba" Cike da basarwa ta ce “lafiya ƙalau Ustaz kawai tunani ne yayi min yawa.” “Zahrah tunani meh kike yi haka yar ƙarama da ke da zai sa ki shiga irin wannan yanayin?” Bata yi tsammanin jin irin wannan tambayar ba daga Ustaz shiyasa kawai tace tunani take yi.

Murmushin da iyakar shi fuska ne tayi sannan tace “laaaaa Ustaz ba fah wani tunani nake yi ba kawai duniyar ne ban jin daɗin ta” “toh Allah ya sauqaqa Zahrah ammah ki rage tunani” daga haka ya wuce.

Badi'a dake nazartar ƙawar ta tunda suka fito daga gida gashi yanzu fararen idanuwan ta sun yi jazur da su. “Zahrah, gaba ɗaya yau tunda muka fito nake nazartar ki, anything wrong?” “just nothing” ƙura mata ido Badi'a tayi kafin tace “ƙarya kike Zahrah akwai, kawai dai ban kai matakin ki faɗa min baneh na gode” Ta faɗa cike da fushi. Kamo ta Zahrah tayi kafin tayi murmushi “yi haƙuri ƙawa tah, kin kai har kin wuce ki ji damuwa ta. Ba komai ke damu na ba in banda rashin lafiyar Mamah, yau da na dawo abun yayi worst, kin ga yadda Mamah ke shan wahala, Badi'a bazan iya jurewa ba bazan iya jurar ganin Mamah a haka ba” Ta faɗa ƙwalla na zubowa daga cikin idanun ta. Cikin sigar rarrashi Badi'a tace

[30/09, 10:20 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 2

Wannan shafi naku ne masoya littafin a babban gida. Ku ci gaba da bibiyar alƙalamin DIAMOND LADY. Much ƙauna.

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Kamar daga sama ta jiyo Muryar Mamah na ƙiran sunan ta. “Zahrah, Zahrah zahrah” ta faɗa tana lalumowa ko zata ji ta. A firgice ta tashi jin kamar mafarki take. “mamah” ta matso daga da Mamah dake zaune, “kunna haske” cike da mamaki take kallon Mamah. “mamah ke kike magana haka, Alhamdulillah Alhamdulillah”

Rufe mata baki tayi sannan ta fara magana ƙasa ƙasa yadda babu wadda zai ji su “ki kunna haske, zan nuna miki abu ne” Lalumowa hasken tayi ta kunna sannan ta zuba wa Mamah ido.

Da ƙyar ta miƙe ta nufi wata yar adakar ƙarfe dake ɗakin, ɗan murɗa wasu abu dake jiki kamar zobe tayi sannan adakar ta buɗe. Wata haka da ta sha ƙura ta gani ta ɗauko sannan ta rufe adakar.

A hankali take takowa dan kuwa ba wani ƙarfin jikin ta take ji ba. Zahrah da mamaki yayi kusan kashe ta ga wani tsoro da ya shige ta lokaci ɗaya. Ta ma rasa wane irin tunani zata yi. Ta tuna taji ana cewa idan mutum yan jinyar ajali toh

Soyayyanovels

yakan samu sauƙi daf da mutuwar shi. Saurin kawar da wannan tunani tayi jin an dafa kafaɗarta.

“Zahrah!", Ta ambaci sunan cikin raunananniyar murya yayin da Zahrah ta kasa amsawa sai ma wani firgici da ya mamaye ta. “Zahrah! Ke kaɗai Allah ya bani, kuma bana so ki ci gaba da wannan rayuwar idan aka ce babu Ni. Ina ji a jiki na bazan yi tsawon rai ba, sai dai yanzu naji wani ƙarin guiwa na tunkarar ki da batun ahali na. Tun ba yau ba kina tunkara ta da maganar ina basarwa saboda yadda nake jin wani mololo ya tare min zuciya da zarar an yi min tambayar. Yau bana jin abun shiyasa nake son sanar da ke Ni wacece, ban ce ki ci gaba da zama cikin gidan nan ba saboda babu rayuwa mai daɗi cikin shi. Ina da rai ma baki samun kulawa daga wajen kowa sai Ni yin idan babu Ni ban san ya zaki ji ba.

Ammah a matsayi na na mahaifiyar ki kuma mai ƙaunar ki,ko da bayan raina ne bazan zo ki bar cikin gidan nan ba saboda shi ɗin tamkar gidan mahaifin ki yake. Ammah idan kika ji ba zaki iya ba ko kin takura da hakan, ko kuma anci gaba da tauye hakkin ki toh ki nemi ahali na.

Wannan jakar da kike gani mallaki na ne kuma ita ce motar da zata sada ki da dangi na, zan damƙa ta a hannun ki da zarar na sanar da ke labari na, kuma zan so ki adana ta kamar yadda nima na adana ta.”

Ɗan dakata wa Mamah tayi da bayanin tare da ƙanƙame hannun Zahrah cikin nata yayin da hawaye ke zubowa daga cikin idanun ta, ga kuma alamun gajiyawa a tare da ita. Ganin hakan yasa Zahrah share nata hawayen.

Cikin ranta kuwa tunani take “kamata yayi ace nayi farin ciki da wannan daren, kamata yayi ace naji murnar da ban taɓa ji ba a wannan daren saboda tsantsar tarihin da zai buga cikin rayuwa ta. Daren da zan samu abun da na daɗe ina fatan samu tun ina ƴar ƙarama ta, abun da tambayar da ke sa mahaifiya ta tayi fushi da ni gashi kuma zata bani shi a yau.

Ammah meh yasa Ni bana jin naji wannan labari da na daɗe ina son ji?, Labarin da zai kasance makullin baƙin ciki na?”

“Tabbas ina don sanin tarihin ki Mamah, ina son sani idan nace bana so toh nayi ƙarya. Ammah Mamah ba a irin wannan lokacin ba. Ina don ki sanar da Ni labarin ki ne a lokacin da in naji zanyi farin ciki, a yanzu baki da lafiya kuma bamu da kowa sai Allah, sai kuma bayin sa Ammi da Abba da ya aiko cikin rayuwar mu. Zan so ki Dakata da faɗin labarin nan zuwa wani lokaci”

Itama Mamah ɓangaren ta tunani kawai take yi game da rayuwar ta, yarintar ta, tasawar ta i zuwa auren ta da masoyin ta Abdulkarim Kuru. Haihuwar ɗiyar ta Zahrah, da mutuwar ba zata da mijin ta yayi, auren ta da Kawu da kuma irin baƙar izayar da ya gasa mata ita da yarinyar ta.

Shiru shiru babu wanda yayi magana cikin su, Mamah na jiran amsa daga ZAHRAH kan ta fara bata labari yayin da Zahrah ta kurma cikin duniyar tunani.

Mamah da ta gaji da zama ne ta ɗan kishingiɗa, hannun ta dake cikin na Zahrah ne ya zame wannan shine dalilin farkawar su duka biyun daga duniyar da suka faɗa ta tunani.

Bubbuga ƙofar da suka daɗe basu ji anyi ba ya sa suka miƙe tsaye a tare. Har Mamah ta miƙe zata buɗe ƙofar Zahrah tayi saurin dakatar da ita.

“aah Mamah, na san bai wuce Kawu baneh kuma ba zaki buɗe masa ba" bata yi mamakin jin maganar Zahrah ba hakan yasa ta zauna bakin bed Babu musu. Jikin ƙafar ta Zahrah ta zauna tare da kwantar da kan ta kan cinyar Mamah. A hankali ta ɗago ta kalli idon Mamah sannan ta kawar da nata gefe.

“mamah ba haka kawai yasa na tsani Kawu ba sai don rashin nuna ƙaunar shi gare ki a matsayin ki ta iyalin shi. Ba ma wannan ba tunda kika kwanta bai taɓa tako ƙafar sa don ya duba jikin ki ba balle yace yau a kai ki asibiti ko ya karɓi takardar magani yace zai siyo ba bayan kuma Ni da kaina na sanar da shi baki da lafiya.”

Tabbas abun da Zahrah ta faɗa bata ga laifin ta ba ko kaɗan at least ya kamata ko sau ɗaya ace ya zo ya duba ta ɗin.

Gyangyaɗin da Zahrah ta fara ne yasa Mamah cewa ta dawo su kwanta gobe da kammala maganar su. Ba musu Zahrah

ta kwanta jikin Mamah nan da nan bacci mai daɗi yayi awun gaba da su. Safiya ta gari.

Ba su suka tashi ba sai da gari ya fara wayewa Mamah ce ta fara tashi ɗauke da addu'ah a bakin ta. A hankali ta sauƙo ta fita, ɗan watsa ruwa tayi a jikin ta ta haɗo da alwala sannan ta yi sallah. Bayan ta isar da Sallah ta yi azkar ɗin ta. Miƙewa tayi don tashin Zahrah tayi arba da jakar nan, a kasalance ta ɗauke ta ta jefa ta cikin wardrobe ɗin kayan ta dake sama can.

Bayan ta tashi Zahrah ta ɗan fara kaɗe ɗakin. Tana yin Sallah ta gaida Mamah “ina kwana mamah” “lafiya zahrah” “ya kwanan jikin?" “Alhamdulillah, yi maza ki tashi kiyi wanka kada ki makara" “toh" tace tana miƙewa, ninke sallayar tayi sannan taje tayo wanka. Uniform ɗin ta ta manta ba'a goge yake ba, a hanzarce ta shiga gidan Ammi ta goge lokacin Badi'ah ta tashi.

Sanya uniform ɗin ta tayi tana gamawa Mamah ta zubo mata jallof ɗin taliyar da ta musu, ita dai Zahrah mamaki take don rabin ta da cin girkin Mamah tun kwanaki basu fi biyu ba bayan kwantar da ita da aka yi a asibiti yau kuma ta tsiro girki.

Bayan ta ci abincin tana santi ta wanko hannun ta tayi brush daga nan ta zari school bag ɗin ta da kuma hijab ta zura ta fito. A bakin ƙofa suka ci karo da Badi'a ita ma ta shirya tsab”

“har kin shirya kenan, bari na miƙa wa Mamah sai mu wuce" ba tare da ta amsa mata ba tayi waje. Tana miƙa wa tayi wa Mamah ya jikin ta fito, driver ne ya kai su school sai dai yau Zahrah tamkar ba ita ba, tunani ya addabe ta.

Babu abun da ya tsaya mata a rai irin hirar su ta jiya tare da Mamah. Hirar da ta tsaya mata cikin zuciyar ta.

“meh Mamah take nufi kenan,idan na fahimta akwai ɓoyayyen al'amari dangane da ita, bana son rasa Mamah don ita ɗin numfashi na ne, ammah cikin maganganun ta na jiya naji zuciya ta na karye wa” Other heart ɗin ta tace “haba Zahrah, damah ai yanzu kam kin kai ki san tarihin mamar ki” “ƙwarai to ammah bana so rada ta ai” “duk da haka dai ya kamata ki saurare MEH Mamah zata sanar da ke, la'allah ƙarshen zaman ku da azzalumin kawun ki yayi” “ai kuwa dai, nimah na ga hakan” Haka tayi ta magana da zuciyar ta har uncle Hashim ya shigo. Dukkan students suka miƙe suna gaida shi, sai dai Zahrah hankalin ta baya ma ajin, bata san wainar da ake toyawa ba. Bai yi mata magana ba ya basu umarnin zama, har ya fara clsss ɗin bata san MEH ake ba sai da Badi'a ta buge ta.

Firgita ta waro ido tana kallon Badi'a. “ke wai tunanin meh kike yi ne?” “banu komai” Ƙasa ƙasa ta harare ta tace “kina nan kina tunani har uncle Hashim ya shigo kina zauna muka gaida shi kuma kice ba tunanin komai kike yi ba?, U better concentrate” daga haka ta zunguri ƙeyar ta.

Daf da lokacin closing PC ya sa aka kira Maryam, Badi'a da kumah Zahrah zuwa staff room. “ba komai ne ya sa na kira ki ba sai don na sanar da ku cewa yanzu ba sai anjima ba zaku tafi Jos zaku yi representing school ɗin nan a wani programs so nayi magana da iyayen ku akan tafiyar. Yanzu ku ɗauko school Bags ɗin ku ku ajiye su a nan. Tare zaku tafi da Academic officer da kuma Hashim. Please Behave well” Suka haɗa baki suka ce “ohk sir” Ɗauko bags ɗin su suka yi suka ajiye. Lokacin Academic officer ya ce su fito. Abun mamaki PC ya tsayar da su. “ku zo” Zuwa suka yi ya miƙa musu sabbin uniform da gani goge su aka yi saboda ɗumin dake jiki. “ku tafi da wannan, ina zaku tafi wajen sai ku sanya.” Bayan sun amsa suka koma daga nan motar su ta tashi sai Jos.

RACAS FOUNDATION COLLEGE, old airport jos, plateau suka nufa. Ɗan zagayawa A. Officer yayi da su sannan suka koma zuwa destination da aka basu don sai da safe za'a yi competition ɗin. Abinci mai rai da lafiya yayi order, bags uku ya aiki musu suma suka ɗauki two bags.

Bayan sun ci abinci sun kora da drink suka yi sallah. Hutawa suka kwanta suka yi, ba su suka tashi ba sai 4:12pm, suna tashi suka watsa ruwa suka maida kayan su sannan suka yi sallah.

Knocking door ɗin aka yi, Badi'a ta buɗe, Academic officer ne yace su zo. Wani ɗan cool down area suka samu suka zauna. Yayi musu bayani akan programs ɗin da kuma wanda kowa zai yi participating. Daga nan ya ƙara haska musu hanya tare da taimakon uncle Hashim, bayan an kwatanta wa kowa nashi A. Officer ya ce “ toh bari a gwada kowa Muga

yadda zai yi”

Maryam zata yi representing school ɗin ne a junior spelling challenge and pronounciation yayin da Badi'a zata yi essay writing sai kuma Zahrah impromptu speech.

Marya aka fara gwada wa and Alhamdulillah she's done it well. Tayi da kyau har sun saka rai kan spelling challenge nasu.. Badi'a ma ya bata piece of paper sannan ya bata topics. Within short period of time ta kammala, he's impressed by the way she answer the question, ita ma aka dasa alamun nasara a tattare da ita.

When it turns to Zahrah, a topic is given to her also, and tayi yadda ya kamata, her confidence, gentleness, the way she speaks like she's from Elizabeth's palace.

Bayan sun kammala ya ƙara gyara musu kowa aka faɗa nata corrections nata, and they all master it. Da yake lokacin sallah ya gabato kai tsaye komawa suka yi suka yi alwala suka yi sallah. After they prayed suka ce su gwada playing Qur'anic trick, Zaki janyo ayah sai ki zaɓi ɗaya cikin su ta faɗi wani surah take, idan ta canka daidai sai ta karanto cigaban. Haka suka yi tayi har lokacin ishà.

Alwala suka yi suka watso ruwa sannan suka jona sallah, suna idarwa bayan azkar suka Fara hirarrakin su.

Few minutes da fara hirarrakin su aka yi nocking, abincin su aka kawo musu sai lokacin duka tuna a na rana da aka kawo akwai extra bag da basu taɓa ba. Ɗauko ta suka yi kads ayi asara suka fara cin ta. Bayan sun ci suka buɗe Bags ɗin daren, chips ne sai egg sauce da kuma milk drink. Bayan sun cinye tas suka ci gaba da hirar su. Ba su suka kwanta ba sai around 10:00pm. Safiya mai albarka marvelous squad.

Cikin baccin ta tayi mafarkin Mamah. Sai ga ta nan kusa da ita suna wata magana, bayan sun gama maganar sai Mamah ta damƙa mata wata haka wacce bata san ta miye ba tare da gargaɗin ta kada ta buɗe ta kwana kusa. Bayan ta karɓa sai Mamah ta ɓace ɓat, tana ɓacewa sai Zahrah ta fara kuka tana neman taimako, wai sai ga baba amarya ta fito tana sheƙa mata dariya can kuma ta ɓata rai.

A zabure ta miƙe gani gari har ya waye. Ɗaya bayan ɗaya ta tayar da su suka yi sallah, sannan kowacce ta shiga tayi wanka. Suna fitowa suka shafa cream ɗin da suka ga ajiye gaban dressing mirror dake room ɗin. Around 7:00am aka kawo breakfast, suna ci suka yi brush suka fara Sanya uniform saboda za'a fara program ɗin ne by 9:00am and suna so su je da wuri.

“Zahrah wannan kam daidai ɗin ki ne ke zaku saka” Badi'a ta faɗa tana miƙo mata wata bujen riga. Zumɓura baki tayi ta harare ta. “u're out of your mind actually Ni zan saka wannan burgujejiyar rigar?” Gira Maryam ta ɗaga mata wanda yasa ta cilla mata ita. “ke maryam ke ce uwar mata cikin mu ke zaki saka ta” “wannan rigar nimah bazan saka ta ba sai dai na mayar da tsohuwa ta” Dariya suka kwashe da ita sannan Badi'a ta tsagaita ta ce “wa yaga new plus old which is equivalent to mark reduction” ta ci gaba da dariyar ta. Maryam ta ƙulu iya ƙuluwa kafin tace “shikenan na haƙura zan sa ammah dai kun min wayo ne. Gwalo Zahrah tayi mata sannan tace “don't wear it if u like Mamah baby” Jin sunan da Zahrah ta ƙura ta yasa ta wulla rigar. Suna cikin haka aka yi knocking su a guje Maryam ta janyo rigar ta saka tana hararar Zahrah yayin da Zahrah ke tayi mata dariya.

“if u're ready we can go” A nutse suka fito suka bi bayan shi zuwa motar su. Daga nan motar su ta lula sai RUCHAS FOUNDATION COLLEGE.

TOH, MU KASANCE GOBE DA KU DON JIN WACECE MAMAH DA KUMA DALILIN ZAMAN TA TARE DA KAWU? ME KUKE TUNANI ZAHRAH ZATA YI BAYAN SANIN ASALIN MAMAH SHIN ZASU CI COMPETITION ƊIN NE KO KUWA? DUK CIKIN LITTAFIN BABBAN GIDA KU CI GABA DA SAMBAƊO MIN COMMENTS REMEMBER FILIN BADA SHAWARA DA KARƁAR KƘORAFI A BUƊE YAKE

ITZ DIAMOND LADY _Oum Zainab_

[03/10, 3:43 p.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing   *A BABBAN GIDA* _(All in a big

family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL*
_____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 3

kada ku mance gabaɗaya littafin sadaukarwa ne gare ku AISHATU USMAN (Baby Unah) sai dai gashi sai rabar da pages ɗin nake ba tare da sanin ki ba ammah na san ke ɗin mai fahimta ce ai... Haka wannan shafin ma dai sadaukarwa ne gare ku A'ISHAH MB (Baby Isha) marubuciyar littafin Rayuwa da macijiya Pinky darling marubuciyar littafin SO FAIZA ALMUSTAPHA (Fa'eeh BG) marubuciyar littafin a mafarki na santa. Matar Dear marubuciyar littafin Albasa. I guys mean a lot to me, so much love u....Allah ya ƙara muku hazaƙa da zaƙin hannun.

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Suna isa suka yi parking motar su. A lokacin ba'a wani zo da yawa ba saboda sai 9:00am za'a fara. A nutse suka shiga cikin ƙatoton ball ɗin da aka jere shi da kujeru fiye da dubu biyu. High table already well set kawai mutanen ake jira.

Front seat suka samu suka zauna duk da cewa wurin is meant specifically for audience, suka ci gaba da gwada yadda zasu yi har aka fara zuwa.

The first person to come wani Black timid balded man ya zo wurin su bayan sun gaida shi ya amsa sannan ya tambaye su su waye su. Cikin nutsuwa Maryam tayi mishi bayanin cewa sun zo representing school nasu ne, ya tambayi wani school suka faɗa mishi nan ya rubuta a paper dake hannun shi daga nan yace su tashi nan wurin isa not meant for them, bayan shi suka bi ya nuna musu wurin da aka wani don participants a nan suka zauna.

Tun daga lokacin aka fara zuwa, people from various schools da wasu ma ba a Jos ɗin suke ba, baƙi duk suna ta zuwa kowa sai wuri yake samu Abun ku da Nigeria iyayen african time sai wajen 9:15am aka daina shigowa alamun kowa ya kammala zuwa.

Ba tare da ɓata lokaci ba MC ya fara gabatar da programs ɗin da za'a yi tare da welcoming address na manyan baƙi da kuma shuwagabannin taron. Everything is well set so ba a ɓsta lokaci ba aka fara.

Schools fiye da hamsin ne suka halarci taron, aka fara da Spelling challenge and pronounciation. Ɗaya bayan ɗaya aka ƙira partipants na kowanne school suka samu wurin da aka tanada don shi wannan program ɗin.

Bayan sanar da su cewa duk wanda ya zaɓa number, bayan yayi spelling ba daidai ba za'a yi withdrawing nashi daga masu participating. First round aka cire 39 schools second round baa cire kowa ba, third round aka cire 20 schools sai kuma fourth round aka cire 15 schools ya rage saura 5 partipants representing 5 schools.

Da ƙyar aka cire biyu aka bar biyu, Maryam kaɗai sai wata Christian suka rage, sun fafsta sosai kafin daga ƙarshe aka cire wannan ɗayar.....Nan da nan aka saka tafi raf raf su Academic officer da uncle Hashim Baki har kunne student ɗin su won the Trump.

Sara ɗin ta na da ta koma ta zauna kusa da sauran yan uwanta, ba'a wani ɓata lokaci ba aka shiga essay writing, Abu da rubutu time kawai aka basu daga nan aka basu question papers. Within an hour suka kammala kowa yayi submitting, Babu wanda ya San Mai nasara a wannan ammah kowa na fatan kasancewa mai nasara. Daga nan kuma Badi'a ma ta dawo wurin ta.

Hayaniyar da aka fara ne yasa mu ya roƙi mutane da suyi shiru, bayan an yi shiru tamkar babu kowa aka yi introducing last program Wanda duka ya fi tsayi a ciki, sai dai za'a iya ɗaukar four good hours tukunna a kammala.

Shima aka kira partipants ɗin suka fito. Bayan sun fito aka faɗa musu dokokin su da kuma Marks awarded to each step.

Successfully aka fara kuma duk Wadanda suka yi they performed well. Mutum 20 ne suka yi daga nan aka tsayar da taron aka je break na 2hours. Sallah suka yi a wani nearest mosque sannan suka samu wuri suka zauna, suna zaune uncle Hashim ya kawo musu abinci, a wurin suka ci sannan suka koma hall din lokacin kuwa babu kowa a ciki.

Bayan cikar lokacin mutumin dazu wasu the first to enter, ya kara daukar sunan school nasu. Bayan kowa ya dawo aka ci gaba da impromptu speech. Zahrah was second to the last to be in the stage.

Cike da nutsuwar ta wacce mutane ke ganin kinibibi ne da kuma yanga sai dai haka abin yake a jikin ta ta wuce ta dauki paper din ta mika kamar yadda sauran suke yi, abun magana aka mika mata a lokacin da ake karanta mata topic nata. Yana kammalawa ta juyo ta fuskanci shuwagabannin, a nutse cikin Muryar ta mai daukar hankali tare da turancin ta wanda mutane da dama ke cewa kinibibi ne da karyata ta fara gaida su mataki zuwa mataki har ta isa ga audience.

Tafi ne kawai ke tashi a ball din duk da cewa mutane da dama sunyi saidai wannan ya kasance daban, everything with her is unique, her approach, Grammer and pronounciation was different uwa uba kuma voice nata da take magana da shi cike da gayu da kuma kwarewa.

Ci gaba da zubo turancin ta tayi wanda Ni reporter dai ban samu ikon haddacewa ba balle na karanto manah, Allah i know is tayi fiye da duk wanda suka yi, babu wanda zai ji bai yaba ba sai dan hassada.

Abun mamaki sauran na baya basa concluding time ke cika ammah Zahrah sai da ta kammala komai gashi tayi bayani yadda ya kamata, tana gamawa kuma lokacin ta na cika. Hakan ba karamin burge mutane yayi ba, babu wanda Zahrah bata tafi da imanin shi ba sai dan bakin ciki. Gashi dai mostly ba Hausawa bane partipants din kuma kamata yayi ace sun yi fiye da ita musamman da ya kasance ita din ba ta samu Foundation mai kyau ba ammah duk ta wanke su.

Mutum na karshe na gamawa aka fita hutun rabin hour din cire sakamako da kuma hada gifts. Basu bar halal din ba saboda babu wani abu da zasu yi in sun fita din. Cold and chill drink aka mika musu daga malaman su suka sha abun su sannan suka fara dan hiran abun.

“kai Zahrah, kin matukar kayatar fah, wallahi babu wanda ya kai ki yi, Ni har na baki winner na category naku” Hararar wasa tayi wa Maryam “kinji fah su chairlady of the occasion, sai ki ga kuma Ni da kike tsammani bana cikin masu nasarar.” Caraf Badi'a tace “Allah ma ya tsare ai kin basu a jikin su, ke kam Maryam naki ma a bayyane yake, nice dai cikin duhu" “nothing but succes from Allah in Sha Allah” Zahrah ta rufe musu baki da hakan.

Bayan lokacin hutu ya kare still dai su kadan ne a hall din sai lokacin aka fara shigowa, mutumin na ya kara daukar sunan school nasu ya wuce. Within few minutes kowa ya dawo don jin sakamako.

Ashe duk abun da ake an watsa shi duniya, ta channels da dama sun daura live ne saboda yadda COMPETITION din ya sanu, gashi ana samun kudi sosai in mutum yayi winning. Chairman na taron sai da yayi dogon bayani gamsasshe tukun ya bada space wa shugaban alkalan COMPETITION din.

A natse ya fara magana,ya fara da gaisuwa da kuma karfafawa partipants baki daya guiwa kan cewa duk sun yi kokari. Daga nan ya fara fadin result.

Dummmmm gaban kowa ya fadi saboda kowa zai so ace school nasu tayi nasara. “let's start with the first category, that is spelling challenge and pronounciation. The first and the winner of this category goes to ALMUNAUWARA ACADEMY Bauchi, in person of Maryam Aminullah. You can come forward and receive you gift. Bayan ta amso ta juya ya kara cewa miss Maryam in addition to the gift, Senator Umar Bukola awarded 100thousand Naira to you. You can have it now” A natse ta amso envelope din ta juyo bayan pictures da aka dauka.

“To the second category, the best essay writer of the year award goes to ALMUNAUWARA ACADEMY Bauchi, in person of Badi'a Kabir Umar. Here goes the best essay writer of the year from same school, congratulations ALMUNAUWARA ACADEMY. Your gift and award is here.”

Itama har ta juya zata dawo yace “i'm not done with you Miss Badi'a, a another gift of 100thousand naira from sir Umar

Bukola was added, come forward and get it"

Bayan ta amsa ta dawo yayi shiru, sai bayan tafi da ihu ya kafa ya ci gaba. “A lady from Elizabeth's palace here won the yeae's impromptu speech with the required Marks without skipping any. You're indeed an angel Miss Zahrah Abdulkarim Kuru from the glorious ALMUNAUWARA ACADEMY Bauchi. This shows to us that ALMUNAUWARA ACADEMY promote and produce capacitive intelligent and amazing students, Zahrah Abdulkarim come forward”

A nutse ta ƙarasa ta amshi aware ɗin da gift ɗin ta ta juyo. Muryar shi ce ta dakatar da ita “Miss Zahrah again received 100k cash from sir Umar Bukola, in addition to this members of the high table have the sum total of 200k for you miss Zahrah ”

A nutse ta amso su ta dawo, ihu hali ɗin ya saka da ƙyar aka yi shiru Zahrah na dawowa seat ɗin ta tayi hugging colleagues nata kowa ya taya kowa murna daga nan shiru ya biyo baya.

Ci gaba da magana yayi “Again we've the year's award to the glorious ALMUNAUWARA ACADEMY, participants from the school should come forward”

Ƙyas ƙyas ƙaran camera kawai kake ji na tashi bayan sun amsa sun koma zaman su kenan aka ƙara ƙira..

“people of time, people that have respect for time, being the first to arrive to the hall, the first one resume after the first break and the last to resume after the last break. Your award and gift is ready, ALMUNAUWARA ACADEMY again won this award. Congratulations ALMUNAUWARA ACADEMY"

Su uku suka amsa sannan suka dawo. Bayan sun dawo aka fara fita, da taimakon Academic officer da uncle Hashim suka kwashe gifts da award nasu zuwa mota daga nan kuma suka koma wurin da suke.

Bayan sunyi sallah suka yi wanka suka ci abinci sannan suka ɗan huta. Sallar maghrib suka yi daga nan suka ƙara yasuwa saboda gajiya.

Basu koma ba a ranar saboda haka bayan dinner suka kwanta. Early morning suka naushi motar su sai Bauchi. School suka fara isa, daga nan suka ajiye gifts da sauran abubuwa kowacce aka mayar da ita gida.

Tana shiga ta tarar da Mamah tana zabga amai a ƙofar ɗakin da gani ma ta jigata da ƙyar take ƙaƙarin kana ganin ta ka ga gajiya da rauni . Da gudu ta rugo tana isowa gurin Mamah, duk wahalar da take ji lokaci ɗaya ta ɓace ɓat, rungume ta tayi ta fashe da wani irin kuka mai ban tausayi. “mamah tun yaushe ne baki da lafiya” Cike da ƙarfin hali Mamah tace “taimaka na wanke baki na zamani koma ɗaki...” A hankali ta sake ta ta miƙe don ɗebo ruwan, tana kuskure bakin ta ta taimaka mata suka isa ɗaki... bisa gado ta kwantar da ita daga nan ta fito ta tsaftace wajen. Ganin basket ɗin gidan Ammi ya tabbatar mata da abinci aka aiko, tsakura tayi ta isa gefen Mamah, da ƙyar ta ɗan ci 3spoons sannan ta koma, ita ma ci tayi ta dawo gefen Mamah ta kwanta.

Bata aune ba baccin gajiya yayi wuff da ita, cikin baccin ta ji mama ta ƙanƙame ta firgit ta farka ta juyo gare ta. “mamah kina son wani abu ne” “a'ah ta amsa tana kaɗa kanta. Daga nan suka ƙara kwanciya basu daɗe da kwantawar ba ta ƙara ƙanƙame ta. Wannan karon tana farka wa taji Muryar Mamah a kunnen ta. “tashi Zahrah zamu yi magana" da sauri Zahrah ta miƙe tana fuskantar Mamah “mamah menene kike don faɗi haka?” “zahrah bani da lokaci isasshe ya zama dole na sanar da ke Ni ɗin wacece saboda ina jin kamar ana ka na zaafita da Ni wajene. Bata kawo komai ranta ba tace “mamah babu abun da zai faru” “buɗe wardrobe ki hau kan kujera zaku ga jakar da na ɗauki daren ranar ki fito min da ita kinji?” Ba tare da ta amsa ba ta ɗauko jakar tana miƙowa Mamah. “aah Zahrah ki riƙe a hannun ki ban kuma amince ki buɗe ta ba har sai ranar da kika ji zama gidan kawun ki ya ishe ki ko kuma lokacin da wanin su yayi ƙoƙarin Cutar da rayuwar ki” ta ɗan yi shiru yayin da zuciyar Zahrah ta riga ta karye da bayanin Mamah.

MU HAƊU GOBE, KADA KU MANCE COMMENTS ƊIN KU SHINE ƙWARIN GUIWA TA! INA ƘAUNAR KU SOSAI.

[03/10, 3:46 p.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL*

_____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1□4□

Wannan shafin naku ne mutanen channel ɗina _Diaomond Bhatool's library_ thanks a lot for Ur support.

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

FLASH BACK ABATCHA ESTATE ABUJA

Tun daga titin da zai sada ka da ABATCHA ESTATE zaka tabbatar wa kanka wuri na musamman zaka dosa. Ga kuma wani ƙaton signboard da ke ɗauke da ABATCHA ESTATE make a roundabout. Wani makeken Black gare ne wanda tunda nake ban taɓa ganin irin shi ba ko da kuwa cikin manya manyan estates dake birnin Abuja. ABATCHA ESTATE kenan. Hamshaƙin ESTATE da in dai kana rayuwa cikin birnin Abuja ne toh ka sanshi sai dai ba kasafai zaka samu labarin wadda ya taɓa shigan shi.

ESTATE ne da ya tsaru iya tsaruwa, an kashe kuɗi sosai wurin gina shi. Uwa uba ba kowa ake bari ya shiga ESTATE ɗin ba don kuwa hardly kaga wani bare ya je, sun keɓe kansu kuma ba sa mu'amala da Barr in ba larura ba, a cewar su iya su sun ishi kansu rayuwa.

Wasu manya manyan guards ne wanda girman su kaɗai ka gani hankalin ka sai ya tashi, tsaye suke bakin gate ɗin fuskokinsu su tamkar ta shanu, babu fara'a ko kuma alamun ta. Ga wasu irin khaki da suka sanya mai colourn Blue. Da ƙyar na samu hanya don na shiga in ɗauko report.

“masha Allah” Naira tayi kuka cikin wannan ESTATE, wani titi na ƙara miƙewa yayin da nayi arba da wani haɗaɗɗen mansion Wanda Kai tsaye zan iya cewa fada ce ta wani mai sarauta.

ABATCHA ESTATE, Ainihin sunan mamallakin wannan ESTATE shine Mohammad Abatcha, haifaffen garin Birnin Gwari ne dake jihar Kaduna. Ammah asalin iyayen su Fulani ne na ƙasar Niger.

Alhaji Kabir Abatcha da kuma matar shi Sa'adatu Fulani ne usul daga garin Birnin Gwari dake jahar Kaduna. Kiwo ita ce ainihin sana'ar su kuma sunyi auren zumunci ne da Sa'adatu.Bayan haihuwar ɗan su na fari wanda yaci sunan kakan da ABATCHA shine dalilin sayar da shanun su suka dawo cikin Kaduna da zama. Bayan tattaunawa ta musamman tsakanin su suka yanke shawarar fara sayar da babur da kuma keke. Alhamdulillah cikin ikon Allah Allah ya buɗa musu sosai sai dai tunda suka haifi ABATCHA Allah bai ƙara basu wani ɗan ba.

ABATCHA ya taso ne ciki gata, kulawa ga uba soyayyar iyaye. Tun yana ƙarami Allah yayi masa farin jini da saboda tsantsar kyau da yake da shi irin na dukkanin asalin nan. Yayi karatun primary ɗin da ba kamar iyayen shi ba da suka yi iya karatun Allo. Bayan ya kammala secondary school ɗin shi kuma ya fara karatu a ATBU, mechanical engineering yayi saboda yana son ci gaba da kula da kasuwancin mahaifinsa wanda a yanzu ya bunƙasa sosai.

A lokacin da yake karatun ne suka haɗu da Karima ɗiyar Abokin Baban sa ne wanda kasuwanci ya kai shi Kaduna. Duk da cewa iyayen sun so ya koma tushe ne yayi aure basu ƙi ba kasancewar mahaifin Karima aboki ne na kusa ga baban sa. Ba'a daɗe ba kuwa aka yi musu aure.

Bayan auren su da watanni kaɗan Baffa ya damƙar da kasuwancin da hannun ɗan shi, a lokacin kuma suka koma Birnin Gwari da zama a cewar su zasu fi samun nutsuwa. Abun ka da zamani yayi wa kasuwancin sa register da “ABATCHA AUTOMOBILES”. Lokaci ƙalilan Allah ya sa albarka ciki kafin kace meh wuri ya sanu ga kuma uban ci gaba da aka samu.

A lokacin ne kuma Hajjaty matar Alhaji Baba ta samu cikin farko zo kuga ɗauki wajen su da kuma iyayen su. Bayan wata

tara ta haife ɗan ta mai suna Abubakar. Kyakkyawa da shi kamar mahaifinsa ga kuma farin jini da yaron ke da shi.

Bayan shekara biyu da haihuwar shi ta ƙaro ɗanta mai suna Umar, daga nan Uthman sai kuma Aliyu wanda shine ƙarami cikin maza.Daga nan Hajjaty bata ƙara haihuwa ba.

Dukkan yaran sun tashi cikin kulawa da kuma gata, ahali ya ginu gashi suna matuƙar jin daɗin rayuwar su. A lokacin da Aliyu yake Aji biyar na primary Alhaji Baba ya ƙara aure. Basu wani damu da auren shi ba kasancewar basu sanya damuwar wasu a ran su. Amarya Khadijatu bata yi dogon zango ba Allah yayi mata rasuwa. Babban ɗan ta Muhammad mai sunan Baffa sai ƙaramin Yusuf. Bayan haihuwar Yusuf ne Allah yayi mata rasuwa, to da yake lokacin ita ma Hajjaty cikin ta ya kusa haihuwa kawai aka yi inducing labour ta haife shi kafin lokacin. Wannan karon mace ta samu saboda irin farin cikin zuwan yarinyar suka saka mata suna Madina.

Madina da Yusuf duka Hajjaty da kanta ta shayar da su cike da so da ƙauna. Madina ta ga gata fiye da kowa cikin gidan, gatar kuwa ta ko'ina tun daga wurin babban yayan su Abubakar har zuwa kan yayanta Yusuf ga kuma soyayyar iya duka kasancewar ta yayan ɗaya tilo da suke da.

Madina tayi karatun Addini MASHA Allah haka boko ba'a barta a baya ba. Tun tana ƙaramar ta bata da ƙirininya da rashin ji irin na yara. Bayan ta gama secondary Yaya Abubakar ya samar mata admission a nan KASU. Wasa wasa tana karatu sosai har ta cinye semester ta farko. Kowa yayi farin ciki da ita sosai. Daga nan ne kuma ƙaddara ta sauya mata salo haɗuwar ta da Abdulkarim Kuru wanda shi ma ɗalibi ne cikin makarantar sai dai shi yana dab da gamawa. Soyayya suke yi mai cike da kulawa yayin da shi Abdulkarim iyayen sa Allah yayi musu rasuwa tun yana yaro.

Ya taso ne a gidan ɗan uwan mahaifiyar sa wanda rayuwarsa tare da su babu abunda yake tsinta sai wahala musamman wurin matar gidan da kuma yaron ta Idrisu. Haka ya daure ya ci gaba da zama tare da su har suka kammala primary. Tun lokacin kuma ya fara neman sana'ar hannu don tallafawa kan sa. Sai dai kash, ko da yayi ya damu yan kuɗaɗen sa sai umman idrisu ta ƙwace ta bawa ɗan ta gashi kuma shi babu aikin da yake yi sai zama a dabar yan shalli tun yana yaron sa.

Bayan ya kammala secondary bai sa ran ci gaba da karatu ba saboda mahaifin idrisu ma Allah yayi masa rasuwa,hakan yasa tun lokacin ya fara sana'o'in hannu, dako, garuwa da sauran su babu wanda bai yi ba sai dai kuɗin duka a gindin ummah ya ke ƙarewa, ko kaɗan bata tausayin sa gashi da shi yake cefane a gidan ammah abincin gidan babu rabon shi.

Haka ya ci gaba da rayuwa bayan wani lokaci wata rana suka haɗu ad abokin sa na primary wanda yanzu baban sa shine chairman na yankin su, da taimakon abokin ya samu damar tafiya jami'a ammah baban abokin ya zaɓa masa KASU saboda kada yake mantawa da shi.

Tare da abokin sa Bello gadauji suka ci gaba da karatun su kuma Alhamdulillah Abdulkarim na samun ci gaba sosa yana kuma samun nasara. A shekarar shi ta ƙarshe ne suka haɗu da Madina Abatcha ɗiyar hamshaƙin attajjirin da babu kamar sa cikin Kaduna state da kewaye. Da farko ya ji tsoron alaƙar su ammahdaga baya suka ware suna zabga soyayya.

Ranar da Madina ta tunkari Hajjaty da maganar aure take so bata kula ta ba sai ma cewa da tayi ta samu yayan ta Abubakar wanda yanzu yaron sa na da Shekara biyu a duniya. Tunkarar yayan ta da tayi ya jawo babbar matsala don kuwa cewa yayi ba ta isa tayi aure yanzu ba kuma ko zata yi sai dai shi da kan shi ya samar mata miji ko daga dangin Hajjaty ne.

Kuka sosai Madina tayi bayan jin bayanin yayan nata gashi kuma Hajjaty da Alhaji Baba sun ƙi saka baki. Ana cikin haka Abdulkarim ya kammala karatun sa sai dai bai samu aikin yi ba. Basu rabu ba har bayan komawar sa gida. A nan yake sanar da baban Bello maganar Madina. Kwantar masa da hankali yayi daga nan ya wuce don gaida umman su. A lokacin ya tarar da mummunan abu don kuwa idrisu shaye shaye yake ba kuma ƙafar yaro, ga kuma bin yayan unguwa yana lalata su tun iyaye na kai ƙara har suka gaji suka fauwalala Allah komai. Ɓoyayyen batu ma ashe har boka gare shi wanda yake rufe masa bakin iyayen yara.

Idrisu yayi baƙin ciki sosai gani ɗan uwan sa cikin rahama gashi kuma wai har karatu yayi. Wurin Bokan shi kai tsaye ya nufa bayan yayi masa aiki kan cewa Abdulkarim ba zai taɓa samun aiki ba ya dawo. Shiru shiru babu aikin yi gashi kuma tsakani da Allah shi yana ƙaunar Madina kuma auren ta yake so yayi.

Aikin hannu ya fara yana zama a matsayin yaron shago ma wani ɗan kasuwa cikin haka da idrisu ya gano ya haɗa masa ramin mugunta har aka kore shi. Yanke shawarar neman auren Madina yayi dai dai iyayen ta sun ce aah saboda sun riga sun mata zaɓi.

Madina tayi kuka sosai kamar ba gobe har rashin lafiya tayi ammah yayun ta suka ƙi amincewa da batun ta. Ana cikin haka sheɗan yayi mata huɗuba ai kuwa ta hau tayi daram. A hankali ta fara haɗa kayayyakin ta masu muhimmanci wuri ɗaya, sarƙoƙin ta da kuma abubuwan ta masu tsada duk ta haɗa su wuri ɗaya sai dai bata san ta yaya zata fita da su ba.

Shawara ce ta faɗo mata ai kuwa tayi na'am da ita. Dare nayi tazo ta fito da su a hankali ta zuba cikin motar ta da take fita school da ita, bayan ta gama ta kwanta tayi bacci kamar bata da wata damuwa. Da safe ta shirya kamar dai zata wuce school tayi wa Hajjaty sallama sannan ta ja motar ta. Maimakon ta wuce school sai ta nufi hanyar garin Bauchi.

Sai bayan azahar ta isa tana isa ta samu wani restaurant ta ci abinci daga nan ta shiga cikin gari neman habibyn ta wanda tasha wahala kafin samun sa. Bayan ta sanar da shi ƙudurin ta da kuma dalilin guduwar ta ne ya fara lallamin ta akan ta koma gida ammah fit ta ƙi daga ƙarshe ta e wallahi in Basu je anyi musu aure ba to zata sheƙe kanta. Babu yadda ya iya ya sanar da baban Bello da ya so yin jayayya shima daga ƙarshe ya yadda.

Sati na zagayowa aka ɗaura auren su tare da masoyin ta Abdulkarim, sai dai shi ko gida bashi da shi, cikin sarƙoƙin ta masu daraja ta bada ɗaya aka siyar, da kuɗin ya sayi gida ɗan madaidaici, two bedroom apartment with one parlour sai kuma kitchen da toilet. Sauran kuɗin kuma ta sashi ya nemo jarin kayan shago tunda akwai jikin gidan su ya zuba. Sannu a hankali suka shimfiɗa rayuwar su mai cike da soyayya da kulawa. Wasu lokutan Madina kan shiga ɗaki ta sha kuka ta fito ammah ta ɗauki alwashin ba zata raba auren ta da masoyin ta ba, su kuma familyn ta suje ita ma ta yafe su.

Duk wannan waina da ake toyawa idrisu bai sani ba sai ranar yazo wucewa ya e bari ya tsaya ya siya sigari. Yana shiga yaga Abdulkarim a shagon, tun daga lokacin ya wuce wurin Bokan sa. A lokacin Bokan ya sanar da shi ai shagon Abdulkarim ɗin ne kuma yana da mata ma, har da juna a jikin ta.

Cike da hassada yace boka ya durƙushe kasuwancin kowa ya rasa kuma shima ya kashe masa shi. Boka yace gaskiya shi duk hatsabibancin sa baya kisa sai dai ina shi da kan sa ya kashe shi tunda ɗan uwan sa ne. Ana cikin haka fah kasuwanci ya fara ja baya, kafin shekara shago ya zama fankayau. Shawara ta bashi kan su sayar da gidan su nemi wanda bai kai wannan ba. Bayan sun sayar suka koma wata unguwar a haka ahaka bar ta haihu.....yarinya kyakkyawa ta haifa wacce kowa ya gani sai ya yaba don kuwa bata bar komai na Madina ba.

Ranar suna yarinya ta ci sunan Fatima Zahrah sunan mahaifiyar Abdulkarim taci. Sannu sannu yarinya ta fara wayo gashi sai ƙara kyau take yi. A haka suka ci gaba da rayuwa har zuwa lokacin bata san wani idrisu ba ballantana shirin sa.

Kwatsam wata rana mai baƙin tarihi wacce ta kasance katanga tsakani ta da masoyin ta Abdulkarim. A ranar ne aka samu gawar sa a kusa da wani gidan mai an yi mishi kisan wulaƙanci, Madina tayi kuka sosai har sai da aka kwantar da ita a asibiti. Bayan taji sauƙi aka sallamo ta. Kai tsaye gidan ta aka wuce da ita da taimako mamar Bello.

Bayan ta gama takabar ta ne ta yanke shawarar komawa gida saboda wanda ta gudo domin shi ya tafi ya barta. A ranar da ta gama shirye shiryen ta ne aka ce ana sallama da ita a waje. Bayan ta fita ta tarar da shi cikin wani koɗaɗɗen yadin sa da yaji jiki. Suka gaida ta tambaye shi ko shi waye yace ai shi ɗan uwa ne ga marigayi idan ba zata damu ba shi yana so ya aure ta ne. Cikin zuciyar ta kuwa wani tsoron mutumin ne ya ɗarsu lokaci ɗaya ta amince da batun sa aka ɗaura musu aure. Cikin gidan ta na da ta tare sai dai tun da ta shiga gidan farin cikin ta ya ƙare.

Farkon auren ya kan kyautata mata, abinci haka baya mata shamaki da shi. Bayan watanni kaɗan da auren salon shi ya sauya, a kowacce rana sai ya jibgi Madina tamkar dai mahaifin ta haka ya mayar da ita, yarinyar ta Zahrah baya ƙyale ta, akan idon ta yake jibgar ɗiyar ta ta sai dai babu yadda ta iya saboda mugun tsoron shi da take ji.

Shan giya da sauran kayan maye babu abun da ya bari sai ƙaruwa ma da yayi gashi bata da ikon hana shi, a na haka ya fara kafa majalisar matasa irin shi masu zaman kashe wando haka zasu yi ta busa hayaƙi a ƙofar gidan. Ranar da ta yijarumta ta tunkare shi da maganar majalisa sai da yayi mata dukan Kawo wuƙa, a lokacin Zahrah bata haura shekara biyu a duniya ba haka ita ma tayi ta kuka ganin irin dukan da ake wa mahaifiyar ta. Tun daga wannan rana yarinyar ta sanya tsanar kawun ta a cikin ranta har zuwa girman ta.

Abinci da yake hana su daga gidan mamar Bello ake kawo musu, su ma bayan wani lokaci suka tarkata komatsen su suka koma Birnin Abuja da zama, hakan ba ƙaramin tayar da hankalin Madina yayi ba, takan ji ina ma ta gudu ta koma ga iyayen ta sai dai duk lokacin da tayi yunƙurin hakan sai ta gwammace bata yi ba, rashin lafiya ce zata kamata ga wani abu da zai tsaya mata a ƙirji kamar dutse. Hakan yasa ta fauwala lamurran ta ga Allah ta bar batun guduwa.....

Yanke shawarar sayar da wata sarƙar ta tayi bayan ta siyar ta siyo kayan suya kama daga tanda, bahuna plates na roba da sauran su ta fara soya Masar siyarwa sai dai ba'a kai ko ina ba mutanen unguwar suka daina siya dalilin mijin ta idrisu. Ganin yunwa zata iya yi musu illa ita da ɗiyar ta yasa ta fara soya Masar a kasuwa wanda hakan ya zama maslaha gare ta.

Bayan Zahrah ta kai shekarun shiga makaranta ta sanya ta a makarantar gwamnati, Zahrah ta tashi da rashin haƙuri da kuma masifa ga rashin kallon mutuncin manya, tun tana ƙarama tsanar kawun ta ta ɗarsu a ranta shiyasa ta ƙudurta a ranta duk ranar da tayi ƙarfi sai ta ramawa Mamah dukan ta da yake yi.

Kwanci tashi babu wuya a gurin Allah har Zahrah ta shiga primary school wanda Mamah ke ɗawainiya da komai nata kama daga sutura zuwa karatun ta da kuma cikin ta. Sam yarinyar ta tsani maza, a tunanin ta duk maza haka suke mugage marasa tausayi shiyasa ta ɗauki aniyar kare kanta daga kowanne irin farmaki namiji zai kawo gare ta, faɗa da maza baya damunta kuma koyaushe takan yi ƙoƙarin ganin tayi nasara kan su. A kullum burin Zahrah bai wuce ta zama alƙali ba saboda take kulle duk wani mai laifi.

★★★★★

[04/10, 7:45 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 5

Shafin nan naku ne Ahlul-moonlight , ubangiji ya ƙara haɗa kanmu ya kuma ƙara ɗaukaka mu

SHARE AND COMMENT PLEASE! _____★★★_____

Zahrah yarinya ce ƙarama sai dai Allah ya bata kaifin basira tamkar wata babba. Kukan da take yi ta tsayar jin kiran Sallah yayin da Mamah ta rungume ta kamar za'a ɗauke mata ita. “Zahrah ta! Ke ɗin ta musamman ce kuma inada yaƙini akan ki, zaki iya ɗaukar fansar mahaifin ki ta hanyar da ta dace koda kuwa bayan Ni bana nan domin ina ji a jiki na zama na da ke ƙaiyadadde ne.”

Zame jikn ta tayi a hankali sannan ta share hawayen ta yayin da ta mayar da hannayen ta bisa kafaɗar Mamah. “Na ɗauki wannan alƙawarin Mamah tah! Nayi miki deduk wanda na kama da laifin raba mahaifi na da rayuwar shi bazan ƙyake shi ba, dole doka ta hau kanshi kamar kowa.” Murmushin yaƙe Mamah tayi ta ƙara rungumo Zahrah jikin ta. “na yadda dake ɗiya ta, Ni na kasa ɗaukar fansar masoyi na ammah nasan ke zaki ɗau fansar mahaifin ki. Fatan nasara takasance dake a kowanne yanayi.”

Da ƙyar suka tashi suka yi sallah musamman Zahrah da ke fama da gajiya shiyasa ta ce yau ba zata je islamiyya ba,

abinci Mamah ta girka bayan sun ci suka kwanta don su huta. Yinin ranar Zahrah a sukwane tayi shi ga wata fargaba da take ji. Zuciyar ta wani irin bugu take yi innalillahi wa inna ilayhi rajiuun kawai take maimaitawa.

Bayan Badi'a ta kawo abinci kamar kallum Zahrah ta amsa suka ɗan yi taɗin su kafin ta wuce. Serving nasu tayi a plate ɗaya ita da Mamah daga nan suka zauna suna ƴan zantukan su.

Ita dai yau Zahrah cike take da mamakin Mamah, yadda yau take ta ɓarin magana kamar mota maras birki, tun daga taɗin family nata har zuwa kan rayuwar ta gidan Abban Zahrah. Daga ƙarshe da ta ɗauki hakan a matsayin kewa tayi wa Mamah yawa shiyasa take maganar.

Bayan sallar isha'suka yi addu'a kamar kullum suka kwanta bacci. Bacci mai uban nauyi ne ya kwashe Zahrah.

★★★★★★★

Tafe take cikin wani baƙin daji mai ɗauke da duhun gaske, babu alamar akwai halitta cikin shi. Ta jima tana tafiya tare da fatan Allah ya haɗa ta da wani wanda zai taimaka mata ta koma gidan kwatsam ta fara jiyo sauti daga can nesa. Yanke shawarar zuwa guriin sautin tayi tare sa fatan Allah yasa mutane ne. The more ta yi tafiya the more sautin ke ƙaruwa.

Tayi doguwar tafiya kafin ta kusanto wurin sautin sai dai alamu sun nuna cewa sautin ba na mutane bane....gurnanin da take ji ne tare da wata mahaukaciyar dariya mai ɗan karen sauti da amo maras daɗi yasa ta ɗan ji tsoro daga ƙarshe kuma ta yanke shawarar ƙarasawa.

Bata kai ga ƙarasawar ba taji ƙasa na wata irin girgiza wanda hakan tayi sanadiyar faɗuwar ta ƙasa, da ta tayi ƙoƙarin tashi sai ta koma saboda girgizar ƙara ƙamari take yi. duk ƙoƙarin ta na tashi tsaye ya gagara hakan yasa ta kwanta tare da runtse idanuwan ta tana miƙa wuya

Wasu munanan halittu ta gani masu munin gaske, kayuwan su manya manyan wanda ke ɗauke da ƙaho biyu, na hagu jibgege na dama kuma ɗan ƙarami. Fuskar su ja jawur da ita ga idon su ɗaɗɗaya ne manya manya marasa daɗin kallo. Baƙin su kuwa ya kai faɗin randa Wanda ke ɗauke da wasu gabza gabza haƙora da suke da launin shuɗi. Gangar jikin su irin ta mutum ce sak ga kyan fata da suke da shi sai dai bakin su da yake a wangale yana zubar da wani kore da jan jini suke ƙara wangalewa.

Ta riga ta saddaƙar cewa tata ta ƙare hakan yasa ta ƙara runtse idanuwan ta tare da karanto wasu addu'oin tsari. A hankali halittun suka matso daf da ita suka ɗaga ta....basu ajiye ta ba sai cikin wani cage Wanda ke ɗauke da wasu mutane kusan biyar.....ana cikin wannan abu sai ga wata mahaukaciya ta bayyana gaban cage ɗin, jikin ta duƙu duƙu ga wasu kayayyakin ta da suka ji jiki. A hankali mahaukaciyar ta jawo ƙofar cafke ɗin tana motsa bakin kamar mai karanta wani abu.

Tana gama buɗe ƙofar ta jawo su ɗaya bayan ɗaya daga ƙarshe ta janyo Zahrah ta faɗo jikin ta. Bata kai ga gane fuskar waye ba taji kiran sallar asuba, ɗauke da addu'ah a bakin ta tayi miƙa. Mintuna kamar 10 ta kwashe tana nazarin mafarkin da tayi tare da hasaso ko meh yake nufi. Kan ta ne ya fara juyawa hakan yasa ta buɗe idanuwan ta da suke lumshe. A hankali ta shashima gefen ta ta gano ta ina Mamah take sai dai babu kowa gurin.

Ƙafar ta ta sanyo ƙasa yayin da ta ware idanuwan ta. A hankali ta fita don gabatar da alwala tunanin ta Mamah na banɗaki, ganin ƙofar a buɗe yasa zuciyar ta bugawa sai tayi saurin kawar da abun da zuciyar ta ke shirin shirya mata ta hanyar ɗiban ruwa a buta, sai da ta gama ɗiba ta shiga bayi bayan ta fito tayi alwala ta koma ɗaki don yin Sallah.

Tana idarwa bata iya ko yin azkar ba bacci yayi awun gaba da ita. Ba ita ta farka ba sai wajen 8:12am sanadin mummunan mafarki da ta ƙara yi na wannan mahaukaciyar. A sukwane ta miƙe tsaye sai dai ƙara kallon gado da tayi sai taga still babu mamah. Zuciyar ta ne tayi wani irin bugu har sai da ta kusa faɗuwa.

A hankali ta duba wurin da Mamah ke sallar asuba ko yaushe taga wayam kuma babu sallaya shimfiɗe. Mamaki ne ya cika ta yau ko ina Mamah ta tafi?. Bayan ta fito tayi wanka ta dawo still Babu Mamah babu alamar ta hakan yasa ta

tsorata da lamarin. Kaya kawai ta sanya ta nufi gidan su Badi'a ko can Mamah ta nufa sassafe.

Karo suka ci da Abba ya fito daga part ɗin shi, a natse ta kalle shi tare da sunkuyar da kanta ƙasa. “ina kwana abba” “lafiya kau Zahran Mamah ya Maman ki?”

Tsoro tambayar ta bata, wane irin ya Mamah bayan kuma nan ta zo. Kawar da abun da zuciyar ta ke saƙawa tayi tare da faɗin “lafiyar ta ƙalau” “toh madallah” daga haka ya wuce ita ma Zahrah ta shiga part ɗin Ammi. Breakfast ta tarar Badi'a da Ammi nayi wanda hakan yasa zuciyar ta yin wani mummunan bugu, a daidai lokacin ta faɗi ƙasa a yashe.

Cike da ruɗewa Ammi da Badi'a suka yi kan Zahrah. Tunani meh za'a fara yi mata Ammi tayi cikin ruɗu tace “badi'ah kawo ruwa masu sanyi” Da gudu Badi'a ta nufi fridge ta ɗauko ruwa. Har Ammi ta gama yayyafawa Zahrah wannan ruwan babu alamun numfashi a tattare da ita. Kuka Ammi take yi kamar ranta zai fita haka Badi'a, gashi ƙwaƙwalwar ta duk ta toshe ta ma rasa MEH zata yi.

A cikin wannan yanayin Abba ya shigo ganin suna kuka yasa shi ƙarasowa yadda suke da sauri. “Lafiya kuke kuka haka” kasa magana suka yi hakan yasa ya kai kallon sa ga wurin da idanuwan su ke. Ganin Zahrah da suka gaisa tare cikin mintuna marasa yawa yasa ya matso “meh ya samu zahrah?" Badi'a da ta shiɗe tace “Abbah Zahrah ta mutu, shikenan ta mutu kuma babu abun da aka yi mata” A hankali Abba ya kai hannun shi ya riƙo hannun ta, jin akwai pulse yasa ya ɗago Zahrah da sauri. “ku biyo baya na”

Cikin hanzari ya fita da Zahrah direct parking. Space ya nufa ya kwantar da ita, Ammi da Badi'a suka shiga. Kai tsaye Northern Specialist hospital ya nufa da ita. Ba a ɓata lokaci ba aka karɓe ta saboda yanayin da aka zo da ita.

Cikin aƙalla 30minutes aka taro numfashin Zahrah da taimakon doctors da kuma Nurses. Daga nan aka saka mata line na N/A sannan aka yi mata antidepressants injection tuni bacci yayi awun gaba da ita.

Ganin doctors na fitowa yasa Ammi saurin nufar su “ehm Please ta tashi ko? Zahrah bata mutu ba ko yauwah ku faɗa min meh ke damun zahrah” Ganin yadda ta bi ta ruɗe yasa doctor murmusawa have “she's Alright now, ammah tana buƙatar hutu, so zuwa jimawa za'a ɗauke ta daga nan a mayar da ita paediatric medical ward sai ku duba ta” Jijjiga kai ammi tayi ba tare da ta fahimci dogon bayanin shi ba tunda yace she's alright.

Reception suka koma suka zauna suna ta addu'ar fatan sauƙi wa Zahrah. Sai a lokacin Ammi ta tuna basu bi sun sanar da Mamah ba can tace ba sai an sanar da ita ba kawai saboda kada a ɗaga mata hankali bayan ba cikakkiyar lafiya gare ta ba.

Har wajen azahar shiru hakan yasa Ammi komawa A&E wadda ɗin, karo suka ci da doctor ɗin da yayi mata bayani. “ehm doctor Bata tashi ba har yanzu?” “eh yanzu dai a je a nemo mata abun da zata ci zuwa jimawa zata iya farkawa anytime” “ok” daga nan Ammi suka koma suka yi girki suka dawo.

Har yamma Zahrah bata tashi ba, hankalin su ba ƙaramin tashi yayi ba shine Mamah ta yanke hukuncin sanar da Mamah kada ta ji Zahrah shiru. Abba na gida kawai ta ƙira shi tace ya aika yaro ya sanar da Mamah Zahrah na asibiti ammah ba sai ta zo ba da an sallamo ta zasu dawo.

Cikin sauri Mamah ta yi picking call ɗin da ke shigowa wayar ta. “Eh ina ji” Ta ɗaya ɓangaren kuma ban ji MEH aka ce ba. A zabure ta miƙe tsaye “ban gane ba.....tooooh ko zaka sa a tambayi amaryar gidan ko tana kwance ba lafiya ne ita ma?.....ohk ina jira”

Daga haka ta dawo ta zauna. Wasa wasa maghrib tayi kuma Zahrah dai bata farka ba, kuma Abba bai ƙira Ammi ba. Yanke shawarar barin Badi'a tayi in yaso in Zahrah ta tashi kafin su dawo ma ita tana nan.

Tana isa bayan tayi girki ta nufi gidan Mamah, ɗakin Mamah ta nufa kai tsaye tare da sallama a bakin ta. Jin shiru babu amsa wa tasa ta shiga da sauri tunanin ta ko Mamah na bayan gida ne. Shiga tayi ta ɗan zauna saboda ta jira ta. Jira shiru shiru Mamah bata fito ba gashi Ammi na son wucewa asibiti. Kai tsaye ta nufi hanyar banɗakin. “da mutum ne a ciki?” Sai da Ammi ta maimaita sau biyar ammah shiru ita ma nan da nan zuciyar ta buga wani irin tsoro ya kama ta.

Ganin jiran ba shi da amfani yasa Ammi ta shawarar tambayar baba amarya ko ta ga fitar ta. Wani kallon banza Baba amarya ta wulla wa Ammi tare da jan tsaki ta koma ɗaki bayan jin ƙudirin Ammi.

Cikin ruɗu Ammi ta fice zuwa gida, ta sanar da abba kafin yace ta wuce babu damuwa wata ƙila Mamah gidan wasu ɣan uwan su ta tafi.

Har lokacin da Ammi ta koma ba'a sauyawa Zahrah waje ba saboda har lokacin bata farka ba. Allah Sarki ƙauna Badi'a kam kasa cin komai tayi sai kuka ta ke yi

“kiyi haƙuri kiyi wa Zahrah addu'a idan kina kukan babu abun da zai miki sai dai kema ki fara ciwon kai.” Kai ta gyaɗa tace “toh mamah” “oyah zo ki ci abinci” babu musu ta ƙarasa Mamah tayi serving nata, ta ɗauki spoon kenan zata kai loma tace “Ammi baki bi kin yi wa Mamah magana ba ne?” “eh tana kan hanya” haka kawai ta faɗa saboda kada ta tayar mata hankali.

Bayan Badi'a ta ci abinci ta ƙara barin reception ta nufi wurin A&E ta tsaya. Tana cikin tsayuwar Dr. Ya fito. Ganin ɗazu ya ganta tare da Ammi yasa ya nufe ta. “Baby ina mamar taku?” “tana can reception” kallon ta yayi yace ta ƙura Maman su. Da sauri ammi ta biyo bayan Badi'a suka taho. Ganin irin tashin hankalin da Maman nasu ta shiga yasa Dr. Yin murmushi.

“Yauwah Hajiya ke ce kika kawo wannan yarinyar ko?” “e...eeeh nice ta farka ne?” “eh ta farka ammah bata cikin hayyacin ta, so yanzu za'a sauya mata ɗaki sai a bata abinci taci” “tooh shikenan”

Bayan an sauya wa Zahrah ɗaki zuwa medical ward Ammi da Badi'a suka wuce. So da yake amenity suka kai ta ya sa duk su biyun suka shiga.

Lumshe idanuwan ta suke yayin da fuskar ta tayi pale, sai kamannin ta da Mamah ya ƙara bayyana.

Ƙarasawa wajen ta suka yi suna ambaton sunan ta.

MU HAƊU GOBE DON JIN YADDA ZATA KAYA HAƊU GOBE DON JIN YADDA ZATA KAYA

[05/10, 7:26 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 6

Dedicated to Aunty fateemah (oum sa'eem)

Masu son labarin daga farko kuyi following channel ɗin nan: https://whatsapp.com/channel/0029VanUFkw5kg7G2ci16o2X

SHARE AND COMMENT PLEASE _____★★★_____

A hankali Zahrah ke buɗe idanuwan ta yayin da suka buɗe ras sun sauƙa kan Ammi da Badi'a. Juya idon tayi don gane a wani wuri take, ganin I.V line maƙale hannun ta ga kuma ruwan da ke zuba a hankali yasa ta fahimci a asibiti take. Ammah me ya kawo ta? A hankali ta fara tuna last scene nata ta shiga duba Mamah gidan Ammi kuma bata ganta ba daga nan ta manta yadda take.

Katse mata tunani Ammi tayi ta hanyar zuba cips and fried egg da ta soyo mata a plate. Kujera ta na ta zauna yayin da ta miƙawa Badi'a plate ɗin wacce fuskar ta ke ɗauke da murmushi. A hankali Ammi ta ɗago Zahrah bayan ta zaunar da ita da kyau ta amso plate ɗin hannun Badi'a ta fara feeding Zahrah, bata Musa ba ta buɗe baki ta naɗi child ɗin tas.

Bayan ta kammala ci Ammi ta dama mata tea Mai kauri ta Sha, daga nan nurse da ke duty ta shigo, ganin IV fluid ɗin ya ƙare yasa ta zare mata shi kada jini ya zuba. Daga nan ta turo doctor. Dr. Yayi farin ciki sosai ganin ta ji sauƙi har ya jata da zance. Tuni ta ware kamar babu abun da ke damun ta. Da zai fita ya kira Ammi zuwa office ɗin shi, a nan ta sanar da ita abun da ke damun Zahrah "ba komai ke damun ta ba sai anxiety Wanda yayi sanadiyar faɗawar ta shock ammah abun bai yi nisa ba Alhamdulillah, sai dai yarinyar taki na buƙatar kulawa ta musamman in ba haka ba akwai matsala. So yanzu na rubuta drugs sai ku bi pharmacy ku amsa. Don Allah Hajiya a kula da ita kuma a nuna mata soyayya"

Daga nan Ammi tayi mishi godia ta koma ward ɗin cike da fargaban ina Maman Zahrah ta je yau kuma, sannan menene dalilin faɗuwar Zahrah.

Basu ɓata wani lokaci ba aka yi discharge nasu, bayan shawarwarin da nurse ɗin da ke duty ta Basu. A gajiye suka wuce gidan Ammi. Ɗakin Badi'ah Ammi ta raka Zahrah, ta haɗa mata ruwa mai zafi ta sata tayi wanka. Bayan ta shiga wanka ta turo Badi'a wurin ta sannan ta koma gidan ko mamah ta dawo sai dai shaaaaam kamar yadda taga ɗakin Mamah yanzu haka yake. A sukwane ta dawo gidan lokacin Zahrah tayi wankan ta ta saka light gown na Badi'a.

Ita dai Zahrah baki ƙimmm bata ce komai ba tunda suka shigo gidan, ganin haka yasa Ammi ta bar ta zuwa safiya suji meh yasa ta faɗi. "daughter ki kwanta ki huta, sai da safe." Kaɗa kai Zahrah tayi daga nan suka kwanta ita da Badi'a.

Ɓangaren Ammi da Abba abun ya ɗaure musu kai. Abba tun bayan Ammi ta sanar da shi mamahn Zahrah fah Bata nan shima ya shiga halin mamaki. Daga ƙarshe suka yanke shawarar neman ta gobe bayan sun ji damuwar Zahrah ɗin.

★★★★★★★

"gaskiya ƙawata aikin boka Bulebule kamar yankan wuƙa yake" Tafawa suka yi ita da Asabe kafin Asabe tace "ke dai ki bari yanzu bani labarin abun da ke faruwa manah, shegiyar ta mutu ne" Kallon ta baba amarya tayi kafin tace "ke har kin manta boka Bulebule baya kisa ne?," "ooooh haka fah" ta faɗa tana riƙe baki alamun ta tuna Baba amarya ta Kamo hannun Asabe ta riƙe sannan tace "ina baki labari, ban san yaushe shegiyar matar ta fita ba ammah dai zancen da nake miki an rasa ta....wataƙila yanzu kam ta riga ta kama bolar zama" Ta faɗa suna sheƙewa da dariyar shaƙiyyanci. "baki da dama ƙawa ta, toh ita yar tata fah?" Ɗan zare ido tayi sannan tayi fari "ohoooh Ni ban sani ba, ammah na sani babu makawa aikin boka ya yi ina jira ta dawo ta sane ni nan"

Girkin da take yi ta ƙarasa ta zuba musu shi duka a tray, suna ci suna magana kamar wasu mahaukata. Bayan sun cinye suka ji gaba da hirarrakin su. Baba amarya ta dubi Asabe ta ce "ƙawa ta yaushe ya dace na ɗauko Bibalo ne daga ƙauye don yanzu kam ita ma nan zata dawo NBmu zauna mu mulki ɗiyar shegiyar tare" Dariya Asabe tayi tace "ƙwarai ya kamata ki ɗauko mana Bibalo gashi kuma ba zata fi sa'ar yar kishiyar taki ba" Jin kishiya yasa Baba amarya makawa Asabe harara. Da yake duk yan duniya ne tuni Asabe ta harbo jirgin ƙawar tata sannan tace "Kaji uwar kishi, kin zo kin samu mata da ya gidan su ammah ke kike kishi ba ma ita ba" "yo ai dole nayi kishi da ita, da ace irin banzayen nan ne ma tooooh, ammah baki ga matar ba ga kyau ga kamala ni wallahi bata yi min kama da yar talakawa daga gani yar babban gida ce" "ai kuwa na lura da hakan, ammah ko ma yar jibgegen gida ne ba babban gida ba yanzu kam ai kin wulaƙanta ta ta zama kashi"

Tafawa suka yi suna dariya kafin Baba amarya tace "yanzu dai gobe ki raka ni ƙauye mu ɗauko Bibalo mudawo nan saboda ina son mu gasawa shegiyar aljanar yarinyar nan aya a hannu, ta yadda zata daina rasar kunyar da ta zama mata jiki" "Ai Ni yar nan tun ranar tariyar ki na ƙullace ta saboda abun da tayi ga kuma shegen kyau har ta so ta fi uwar fa" Bana amarya ta ce "hmm ke dai ki bari kawai, zamu ci uban ta ne ai" Haka suka yi ta hirar su daga ƙarshe Asabe ta koma gidan mata da yake dama can ita a can take da zama.

★★★★★★

Asuba nayi Zahrah ta tashi a hankali tayi alwala tayi sallah bayan tayi ta tayar da Badi'a ma tayi. Bayan sun yi sallah suka yi wanka saboda yau zasu koma makaranta bayan sun dawo daga Jos. Basu shirya ba sai around 6:30am suka nufi kitchen don taya Ammi aiki sai dai Ammi ta kora Zahrah kan ta huta ai bata da lafiya ita kam.

Da wuri suka yi breakfast ganin akwai sauran lokaci mai ɗan yawa yasa Ammi tace “zahrah” a hankali ta ɗago da kanta ta mayar da hankalin ta kan Ammi “jiya MEH ya same ki bayan jin zo nan kika faɗi??” Bata ɓoyewa Ammi komai ba daga baccin su da tashin ta daga bacci har zuwa rasa Mamah da tayi.

Rarrashin ta Ammi tayi tace mata kada ta damu Mamah za ta dawo coz Abba ya sa a nemo ta. Cike da farin ciki tayi a Ammi godiya sannan suka wuce school.

Har suka dawo babu wani labari da aka samu akan Mamah, hakan ya ƙara sanya Zahrah cikin halin damuwa duk da cewa Ammi da Badi'a har da Abba na ƙoƙarin kwantar wa Zahrah hankalin ta. A haka suka wuce islamiyya bayan sun dawo ammah Mamah shiru Babu it's Babu labarin ta.

★★★★★★

Kwanaki uku kenan da ɓatan Mamah ammah shiru babu labari, duk wani radiostation da aka sanar babu wani ci GABA. Gashi har TV stations an sanar harda picture ammah babu ko tari balle wani ya ganta.

Yau da safe Zahrah ta cewa Ammi zata je gida ta ɗauko wasu kayan ta. Tana fita Kai tsaye gida ta shiga, bata tsaya ko Ina ba ta ahiga ɗakin Mamah, cike da damuwa da ƙunci Zahrah ke kallon ɗakin Tana hawaye.

Ɗauko wanna bag din da Mamah ta Bata a daren da zata ɓata tayi tana manna shi a ƙirjin ta. Wani sanyi take ji tamkar Mamah tayi hugging. “Allah sarki Mamah na, Ina matuƙar ƙaunar ki, Ina Kika tafi haka Kika bar ɗiyar ki ɗaya? Don Allah Mamah ki samu ki dawo kada ki bar ni Ni kadai a nan” Tsagaitawa tayi da maganar sannan ta ci gaba tamkar Mamah take gani “aah Mamah nafi so ko zan je gidan ku wurin su Hajjaty da Kika bani labari muje tare da ke tunda ke ce dolem su”

Haka zahatah tayi ta surutai wasa wasa sai da ta kwashe awa guda a wurin. Motsin da ta ji ne yasa ta miƙe ta waiwayo ko zata ga mamah ammah wayam, hakan yasa ta ɗauki bag din tare da haɗa wasu kayayyakin ta ta wuce gidan Ammi.

Baba AMARYA dake tsaye bakin ƙofar ɗakin ta ta Kama kunkumi sai wani jijjiga take tamkar wacce ta ke jiran abokiyar faɗa ta kawo mata dambe. Ashe tun shigar zahrah da taji motsi ta leƙo ganin shegiyar yarinyar da take jiran dawowar ta yasa ta tsaya Tana jiran ganin ko zata fito tace zata taho.

Don't forget to react and share [06/10, 6:23 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 7

Dedicated to mah sister saddeeqah. Much love dear SHARE AND COMMENT PLEASE _____★★★_____

Fitowar Zahrah yayi daidai da matsowar Baba amarya bakin ɗakin Mamah. Babu zato babu tsammani ta fara zubowa Zahrah uban Bala'i “yanzu ke dan uban ki ina kuka gudu ke da shegiyar uwar taki...” Bata kai ga gama faɗa ba Zahrah ta kai mata duka jin ta zagi missing mamahn ta. Baba amarya ta jawo Zahrah har sai da bag ɗin da ta ɗauko ya faɗi....

“don ubanki da shegiyar uwar ki Ni nafi ƙarfin ki har Ni zaki kaiwa bugu don ubanki, toh wallahi yau sai naga wanda ya tsaya miki a gidan nan...bari kiji babu inda zaki ƙara fita don uwarki shegiyar yarinyar mai siffar mayu”

Tana shirin kai mata bugu da bulalar da ta zaro daga bayan ta kwatsam Badi'a ta shigo don kiran Zahrah. Ganin Aminiyar ta hannun shegiyar babar ta yasa ta fita da sauri ta sanar da Ammi. Da sauri ammi ta biyo ta suka dawo lokacin kuwa Baba amarya ta jibgi rabon ta. Ganin mata yar gayu da yarinyar da ke shigo da abinci kwanaki yasa ta tsayar da dukan tana cilla Zahrah gefe wacce ta faɗi ƙasa.

Kallon tuhuma Ammi ta maka mata sannan tace “meh tayi miki kika duka ta?” Daga haka ta ƙarasa ta ɗago Zahrah dake yashe. “badia riƙe ta ku koma gida” Caraf baba AMARYA tace “gidan uban wa?” “gidan da za'a kula da ita” Daga haka Ammi ta ɗauki bags ɗin Zahrah ta bi bayan su.

Cike da takaici suka koma gida Ammi ta sa Zahrah ta ƙara wanka, Badi'a kuma ta wuce school. Tunda Badi'a ta fita Zahrah bata furta uffan ba don yanzu mugun shakkar Baba amarya take yi. Kafin Badi'a ta dawo zahrah ta ɓoye bag ɗin da Mamah ta bata.

Bayan sun yi lunch Ammi take sanar da Abba abun da ya faru ɗazu. “lallai matar nan ba ƙaramar muguwa bace, toh menene damuwar ta da yarinyar da ba kulata ma take yi ba? “nimah abun ya ɗaure mun kai gaskiya, shiyasa nace ya kamata a samo wa Zahrah mafita tunda yanzu ba wata lafiya isasshiya gare ta ba” “worry not dear, zan san abun yi, idan ma magana zanyi wa baban nata sai ya bar min ita a nan su zauna har zuwa lokacin da za'a samu mamar tata.”

Suna cikin zancen suka ji ana wani mahaukacin knocking da ake yi kamar za'a ɓalla gaye. Da Abba ya fita yana isa bakin gate ɗin bayan ya buɗe kawun Zahrah ne kamar wani mahaukaci. Ƙure shi da ido Abba yayi kafin yace “lafiya kake buga min ƙofa kamar wani mahaukaci” “yoh ai dole na haukace bayan ka sace min yarinya toh wallahi ka fito da ita ko na ƙona gida” ya faɗa a hasale yana nuna wa Abba gallon na petrol dake hannun shi. “toh ka ƙona ka gani, wallahi sai na sa an ɗaure ka har ka bar duniya a prison zaka zauna”

Jin abun da Abba ya faɗa yasa Baba rusuna yace “shikenan bazan ƙona ba ammah ka bani yarinya ta na wuce” “aah babu inda Zahrah zata je a nan zata ci gaba da zama zuwa a samu mahaifiyar ta” Ba tare da Kawu ya damu da jin sai an samu mamar ta ba yace shi bai yadda ba.

Wasa wasa haka suka yi ta ɓata lokaci daga ƙarshe Abba ya ce zata koma ammah da sharaɗin zai kula da ita. Kawu ya amince saboda shi yanzu damuwar shi bai wuce ta koma ba don tsoron Baba amarya yake kamar mutuwa shiyasa tana cewa ya nemo ta ya zo nan ɗin.

Bayan ta sha kukan ta Ammi tayi mata nasiha daga haka ta wuce.

Tunda Zahrah ta koma Baba amarya ta saka ta gaba da faɗa har da duka, daga ƙarshe yace ita zata ke yin aikin gida gabaɗaya. Tsananin shakkar ta ya hana Zahrah cewa komai. Bayan tayi girki baba AMARYA tace ai babu rabon ta a abincin. Haka daren Zahrah bata ci abinci ba.

Sassafiya ta tashi saboda ta yi ayyukan da aka gindaya mata su don bata son makara. Tana gama shara tayi wanke wanke ta ɗaura musu girki, abun da bata yi kullum Mamah ke girka musu ammah yau ita zata girkawa maƙiyar mahaifiyar ta.

Sai around 7:25am Baba amarya ta fito daga ɗaki tana hammah alamun ko salla bata yi ba. Ido ta ƙurawa Zahrah dake gaban wuta tana izawa. Yayin da zuciyar ta ke ƙara saƙa mata irin izayar da zata yi wa Zahrah, ba zata taɓa bari ta ji daɗi ba wallahi. “ke don ubanki baki iya gaisuwa bane?” Zahrah da bata san da fitowar Baba amarya ba ta sunkuyar da kanta ƙasa “ina kwana” Harara ta maka mata kafin tayi tsaki “yo da ban kwana ba zaki ganni ne shegiya kawai mayya”

Ita dai Zahrah baki ya mutu bata ce komai ba, sai da Baba amarya ta kewaya taga Zahrah ta gama komai yasa takaici ya cika ta cikin ranta tace “zaki ci ubanki ne, aikin zan ƙara yawan sa”

Taliya leda ɗaya baba amarya ta Bata bayan ta dafa ta soya manja da yaji ammah baiwar Allahn nan ta hana Zahrah. Ba tare da ta damu ba ta shirya a gaggauce sai dai lokacin already Badi'a ta wuce, Ammi sai da ta tambaye Zahrah ko taci abinci tace A'ah. Kai kawai ta gyaɗa taje ta haɗa mata basket ɗin ta sannan ta kaita school da kan ta bayan ƙorafin da ta shigar kan makarar Zahrah. Daga nan ta wuce.

Zahrah kenan, gaba ɗaya bata jin daɗin rayuwar fatan ta Allah ya ɗauke ta ta huta ita ma, ina Mamah ta gudu ta bar ta ita bata sani ba gashi yanzu ta dawo ƙarƙashin kulawar Kawu, mutumin da tafi tsana, mutumin da sanadin shi ta tsani maza with the exception of Yaya Ishaq ɗin ta da Abba. Bayan an tashi suna komawa Zahrah ta shige gida abun ta, tana shiga babu wata wata ta cire uniform tayi wanka, daga nan ta zo bakin ƙofar Baba amarya, ɗan rusunawa tayi saboda

hango ta baje kan katifa da tayi. “ina wuni Baba amarya” Ai bata amsa ba ita kuwa Zahrah tayi tunanin ko bacci take yasa zata juya, bata ankara ba taji sauƙar dorinar Baba AMARYA a jikin ta. “don ubanki shegiya mayya Gara na kashe ki na huta, gidan uban wa kika tafi ɗazun” Cikin Muryar kuka da azabtuwa Zahrah tace “makaranta naje kuma ai na gama aikin safe”

Ɗan dakatawa tayi tana bin Zahrah da matsiyacin kallo kafin tace “toh kafiku uban karatu, kin fi ƙarfin tambaya ta to ba zaki ƙara zuwa makarantar ba” Lafazin ta na ƙarshe yasa Zahrah ba shiri ta kamo ƙafafuwan ta tana kuka “don Allah Baba AMARYA kar kiyi min iyaka da makaranta, zanyi miki duk abun da kike so amma kada ki zama shamaki tsakanina da....”

Wani banzan bugu Baba AMARYA ta kaiwa Zahrah tare da tura ta gefe, tuni ta faɗi ƙasa tana kuka, har ta wuce ɗaki ta dawo gaban Zahrah tace “shegiya mayya kuma tashi yanzu ki girka min abinci duk kin bar Ni da yunwa” Babu yadda ta iya ta tashi da ƙyar ta kaɗe ƙasar jikin ta sannan ta fara ƙoƙarin haɗa wuta. Bayan ta gama kamar da safe Baba AMARYA bata bata abincin ba, hakan yasa ta koma ta kwanta kan gadon Mamah tana kuka.

“haba Mamah, MEH yasa? MEH yasa? MEH yasa zaki bar Zahrahn ki a wurin mugwagen nan?, Gashi yanzu ko makaranta an dakatar da Ni ammah wallahi ko meh zata yi sai naje” cikin zuciyar ta ta faɗi hakan daga nan ta miƙe tunawa da kayan abincin su da ba sosai suka yi amfani da shi ba coz tun da aka fara kawo abinci daga gidan Ammi Mamah ta daina girki sosai. Cikin ranta tace “Allah sarki yaya Ishaq ɗi na mai tausayi na! Kaima ka tafi kaƙi dawowa balle na ganka na faɗa maka halin Baba AMARYA da hukuncin da ta yanke game da karatu na!” Goge hawayen da ya zubo mata tayi ta wuce ta zaro ledar taliya ɗaya, a hankali ta fito ta girka ta, thank God baba AMARYA bata fito ba har ta gama ta tattare komai.

Sai a lokacin ta samu ta juye abincin a cooler ta ɗiba taci da mai da yajin da ya rage musu. Wanka ta ƙara yi tayi shirin islamiyya duk da cewa lokacin ta ya wuce, ta ƙara fiye da hour guda. Still Bata tambaye Baba AMARYA ba ta kama hanyar ta ta fita. Gidan Ammi da ta shiga ta tarar Badi'a kwance babu lafiya. Bata jima ba ta miƙe ta wuce islamiyya.

Bayan ta dawo gida ta wuce kai tsaye, sabon Bala'i ko kaya bata cire ba ta jiyomuryar Baba AMARYA. Bata san ita da waye ba ammah taji ana cewa “sai ta dawo zata ci ubanta, ban san ina ta tafi ba shegiya wata ƙila wurin maza ta tafi kin san yaƴan yanzu haka suke. Yarinya ƙarama sai kiga ta san bin maza balle wannan da jikin ta ya kai na wata ƴar shekara 18yrs.” Bata ji me ɗayar ta ce ba Baba AMARYA ta cafke “bar shegiya tunda na wulaƙanta uwar ta har ta bar gidan saura ita, shegiya mai fuskar aljanu.”

Duk da cewa Zahrah ba babba bace ammah ai ta sanbata kula maza ita dai, kuma kenan Baba AMARYA ce ta kora Mamah?, Lallai kuwa zan sanar da Abba ya taimaka wajen nemo ta kuma a nema mata haƙƙin ta wurin baba AMARYA. Ganin babu inda tunanin zai kai ta yasa ta fito don ta lallaɓa ta je gidan Ammi kwatsam suka haɗa ido da Baba AMARYA ta rako baƙuwar ta.

Cike da fargaba ta juya zata koma ɗaki sai dai bata kai ga ƙarara shiga ɗakin ba baƙuwar ta dakatar da ita. “ke mai siffar Mayu baki iya gaisuwa bane ko Saudatu baki koya mata ba” A sanyaye ta juyo tace “ina wuni” Ko amsa wa batayi ba suka wuce abun su, sai can Baba AMARYA ta dawo. “ke mayyatu fito” A guje Zahrah ta fito tace gani

Jawo ta Baba AMARYA tayi ta ɗurma mata dundu ta ja ta....har sai da suka je wajen bulalar ta ta janyo ta rinƙa tsulawa zahrah har sai da Muryar ta ta dishe ta tsaya. Allah Sarki Zahrah abun tausayi. “tashi ki je kiyi girki kuma mai daɗi zaki yi saboda yau ƴata zata zo, daga nan kuma in kin gama akwai wanki na da zaki yi min kinji ko?”

A hankali ta miƙa ta ɗaura musu girki har sai da ta gama Baba AMARYA tazo ta kwashe tas bata bar mata ba. Haka ta jibgo kayan ta Zahrah ta wanke. Sai 8:45pmta kammala komai daga nan ta shiga ɗakin mamah ta ci taliyar da ta dafa. Ɓigirewa tayi ta fara bacci babu tsammani taji an watsa mata ruwa. A gigice ta miƙe tsaya. Wata ƴarinya ce da bata girmi Zahrah ɗin ba, da wani ƙaton hancin ta da ƙananun idanuwan ta.

“ke don buraubanki ki tashi ba ke babu bacci tunda na dawo” Kan Zahrah ɗaure take kallon Bibalo da ke zaro mata ido.

A zuciye ta janyo ta ta fara dukan ta tana ramawa daga ƙarshe Zahrah ta naushe Bibalo a ciki. Cike da munafurci ta ƙwalla ƙara. Da gudu Baba AMARYA ta fito tana zuwa, ta hau Zahrah da duka.

Bayan nan taja hannun Bibalo suka wuce, ita kuma Zahrah awurin bacci ya ɗauke ta.

Bayan Baba AMARYA ta shiga ɗaki ita da Bibalo, ta busawa Bibalo huɗubar irin azabar da zasu ganawa Zahrah.

★★★★★★

Some month later, Zahrah ta azabtu iya azabtuwa wurin Baba AMARYA da Bibalo, sun mayar da ita jakar su, wanki girki duk ita ce abun takaici in tayi girkin ma ba za'a bata ta ci ba and gidan Ammi yanzu ba zuwa take yi ba, duk ranar da ta saka ƙafa ta je gidan kuwa har Baba AMARYA ta fahimta to kashin ta ya bushe,Kawunzu ba abun da yake yi sai da izinin Baba AMARYA. Ashe ba banza ba su Ammi suka cire damuwar Zahrah a ran su ba sai dai ashe aikin Bulebule ne da baba AMARYA ta kai mishi.

Zahrah ta samu sauyi cikin rayuwar ta, duk hasken fata irin na Zahrah sai da ta disashe, ga kuma wata shegiyar rama da tayi, wuyan nan kamar mariƙar lema ƙasusuwa sun fito kamar wata skeleton, Abu ɗaya da bai sauyu ba jikin Zahrah shine tsantsan kyau da Ubangiji ya bata wanda wahala bata sa ya tafi ba. Y'an abubuwa kuwa sai dai in zahrah ta samu shiga school ƙawaye su tarkata su bata Ana cikin haka kuwa school ya gagari Zahrah, da ƙyar ta kammala ss1 nata daga nan ita ma ta cire rabon ci gaba da karatu.

Sannu sannu babu wuya a wurin Allah Zahrah ta kai shekaru goma sha biyar, ta fara menses sai dai babu wani mai kula da al'amarin ta, don ma bata manta wasu karatukan ta na islamiyya ba tana applying wurin tafiyar da rayuwar ta. duk irin ranar da ke jikin ta bai hana ainihin ƙirar jikin ta bayyana ba, tana da ƙirji ga kuma hips nata so Masha Allah kamar na wata babbar mace.

TEAM ZAHRAH WAI KUNA INA NE JARUMAR KU TA ZAMA ASARA A HANNUN BIBALO DA BABA AMARYA? WHEN ZASU DAINA AZABTAR DA ITA? KO INA RAI MAMAH TAKE? TA MUTU KO TANA RAYE? All theses na a cikin littafin babban gida wanda yanzu ake dab da fara wasan IN ALLAH YA KAI MU GOBE ZAN CI GABA kunga kwana biyu bana post saboda baku yi comments ne, at least in ma ba za'a yi comments ba ayi reacting hakan zai sa naji ƙarfin guiwa. DIAMOND LADY CE [07/10, 7:16 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing   *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 8

Dedicated to mah sister Shaheedah, I love u endlessly ƙanwa am.

Masu Neman labarin daga farko, kuyi following channel ɗin nan zaku samu https://whatsapp.com/channel/0029VanUFkw5kg7G2ci16o2X

WhatsApp group https://chat.whatsapp.com/IWQW3ytbVc611XLon2sn66

SHARE AND COMMENT PLEASE _____★★★_____

AFTER FEW MONTHS....

Abakin wani makeken hotel motar tayi parking, na cikin basu fito ba for more than 10minutes, can wanda ke driving motar ya buɗe ya fito, wani ƙatoton shiregegen mutum ne wanda ya kai shekaru 45years a duniya. Maimakon ya shiga ciki ya zagaya ɗaya sure ɗin ya buɗe, a hankali ya miƙa ma na cikin hannu yayin da shima na cikin ya miko nasa sai naga hannun kamar mace.

Soyayyanovels

Ɗago ta yayi ta miƙe still dai hannun shi riƙe da nata. Wata fitinanniyar shiga ce da ko a ƙasar Turai ban jin ana yin ta. Wata lalatacciyar maroon gown ce a jikin ta wacce bata ɓoye komai nata ba. A haka suka shiga hotel ɗin har suka kai ɗaki room 48, ba tare da ta juyo ba suka shige ciki. Hour uku cikakku suka kwashe kafin suka fito kayan jikin mutumin duk sun yaƙushe..

Sau al lokacin na ƙarewa budurwar kallo Bibalon Baba AMARYA ce. Tun daga nan na ja ƙafafuwa na na gudu kada Baba AMARYA tace ina sakawa ƴar ta ido.

On the other hand

Ɗan gaba da majalisar su Kawu a nan ta kafa murhun da take soyawa Baba AMARYA awarar sayarwa. Hijabin jikin ta da yaji jiki ka ɗigo ɗigon maiƙo nasha nasha. Wani saurayi da ake kira da Bubby ya zo ya tsaya kan ta ce “yah Zahrah zubo min ta ɗari biyu gobe zan baki”

Saurayin da kana kallon shi kaga ɗan duniya ta ƙura wa big eyes nata, cikin ranta kuma tsoro take saboda har yanzu bata manta su waye maza ba musamman yadda Kawu ya wulaƙanta rayuwar ta. “kaga Bubby in na baka Baba AMARYA ta ga babu ko ta biyar ne sai ta jibge ni, don Allah kayi haƙuri..” Cikin kallo na baki isa ba yace “zahrah yau ko uba amarya ne ba Baba amarya ba kwarangwatsa sai kin bani.” Yana faɗa yaja matsamin da take zubawa ya fara ci...

Hawaye ne suka fara zubowa Zahrah don babu yadda ta iya gashi bata don Baba AMARYA ta yi ta bugun ta akan awarar nan ga kuma dukan Bibalo da zata ƙara mata wai ta yi wa uwar ta asara. Sai da yaci kusan ta ɗari biyar ya tura abun gaban ta kafin ya miƙe yana cewa “shegiya ba dai kin ƙi ki zo ɗaki na ba saboda tsantsar wayon ki?, Toh wallahi kullum sai naci iya ci na asawanyar taki ta kashe ki ƴar ɓakin ciki kawai" Yana faɗar haka ya ja ƙafafuwan shi ya wuce, sunkuyar da kai Zahrah tayi ta fara kuka tun ma kafin ta isa gida.

Tana cikin wannan yanayin ne motar da na gani a hotel ɗin nan tayi parking, tare da mamakin motar Bibalo ta fito suna jerawa ammah kayan jikin ta yanzu atamfa ce. Sun tafe suna hira tamkar couples ɗin nan har suka zo gun awara....sai da ta tsaya ta yi tsaki tana tofa yawu a daidai jikin Zahrah. Zahrah da hankalin ta baya kan su jin sauƙar abu ruwa ruwa hannunta yasa ta juyo don ganin wa ya watso ruwa.....maida kanta ƙasa tayi ganin Bibalo ce.

Mutumin da suka zo da Bibalo, Alhaji Yunusa Budawa kenan, mutum ne mai kuɗi ba laifi amma ba can ba kuma yana da mata huɗu har da yaran shi kusan takwas ammah duk da haka basu ishe shi ba, bin matan banza kuwa kamar wanda aka saka shi. Yau ina kin ganshi da wannan gobe kuma wata zaki ganshi da ita. Ya maida mata tamkar motar hawar sa amma yana kashe musu kuɗi in suna tare.

Sun haɗu da Bibalo ne a wajen wani Dije da aka yi bayan layin su, da yake Bibalo ƴar duma-dumar nan ne tuni ya ƙyaso ta...ita kuma don abin duniya da ya rufe mata ido gashi dama ita da bin maza kamar wata karya tun bata kai haka ba ta san maza.

Ɗan kaɗa kan sa yayi ya matso saitin kunnen Bibalo yace “darling wannan kyakkyawar yarinyar fa?” ɗan haɗe fuska tayi haɗi da yamutsa ta kamar wata tsohuwa tace “bebi mai aikin gidan mu ce, sam na tsane ta don Allah mu bar gurin warin jikin ta ya dame ni” “toh kawai yace saboda shi ya riga ya hango abu kuma ko zasu rabu da Bibalo toh sai ya san yadda ya samu fine babe ɗin nan duk da cewa iya fuskar ta ya gani ammah har ya hasaso yadda yarinyar zata kasance.

Ganin bashi da niyyar tafiya gashi ya tsira wa Zahrah ido yasa Bibalo hasala, a lokacin ta cire takalmin ta ta buga wa Zahrah a ka “shegiya mayya wai ke duk wanda ya kalle ki sai ya tsaya ne...toh wallahi ki sake shi don kuwa auren shi zanyi” Ƙasa hana ta yayi saboda ya riga ya faɗa fa shikam. Dukan da ta kai mishi a ƙeya ya dawo da shi hankalin shi nan da nan ya fara kame kame. Babu kunya a bainan nasi Bibalo ta fizgo hannun shi, kamar wani raƙumi kuwa ya bi ta har sai da ta kai shi mota ta zaunar da shi ita ma ta shiga tayi ta surfa mishi Bala'i daga ƙarshe ta bar shi ya tafi. Yana tafiya ta yi kan Zahrah da ke zuba wa wani awara a leda ta wanka mata mari har sau biyu left an right kafin tace “zaki shigo ki same Ni mayya kawai” tana huci ta shige gidan. Saurayin da take sallama ne ya bata haƙuri Saboda tun ba yau ba suka fuskanci yarinyar na cikin damuwa ga irin cin kashin da matar baban ta da ƴar ta suke gabza mata koda kuwa a wurin

tallan awarar ta ne. Ita sam ba damuwar ta dukan da Bibalo tayi mata bane sai dai uban Bala'in da zata tarar, ga Bibalo ga Baba AMARYA ma kuɗin da Bubby bai biya ba. Daga ƙarshe dai Zahrah yanke shawarar ƙin shiga da wuri tayi har sai sun kwanta.

Ɗangaren Bibalo tunda ta shiga ta fara kututtuma ashar wai ita ala dole mai kishi...mutumin da ko zata mutu bashi da niyyar auren irin ta ma infact Bata kai ba kawai dai yana rage zafi da hutawa da ita ne.

Baba AMARYA ce ta dakatar da ita da faɗin "ke kuma fa Bibalo, ke da kika fita neman abun arziƙi kuma ya zaki dawo kina masifa? Ko dai bai biya ki ba ne?" Hararar Baba AMARYA Bibalo tayi tace "rabu da Ni kema, wannan yar abu ta kazar ubance mai ƙirar mayu...." Nan ta kwashe komai ta faɗa wa Baba AMARYA "shegiyar yarinya kinga irin kallon ta da yake yi?" ta faɗa tana ƙara banka harara kamar Zahrah na gaban ta.

Salallami Baba AMARYA ta fara "innalillahi, Ni Saudatu ina ganin bariki yanzu duk irin rayuwar bariki da nayi yau sai da nayi mamaki, shegiyar yarinya bari ta shigo" "si kuwa nimah cin uban ta zanyi Saudatu " ta faɗi sunan gatsau babu ko girmamawa.

Shiru shiru Zahrah ta ƙi shigowa har wajen 10:00pm tana waje gaban murhun ta da already ta gama sayar da awarar tsoro ne ya hana ta shiga. Ba ita ta shiga ba sai around 12:00am lokacin har sun yi bacci, a hankali ta lallaɓa ta shige ɗaki bata ƙara fitowa ba coz lokacin da take shigowa da kayayyakin aikin ta taji motsi kuma ta san ba Kawu bane tunda Baba AMARYA ta riga ta haramta masa kwanan gida.

A ƙasa ta kwanta saboda Baba AMARYA ta sa an sayar da komai na ɗakin Mamah a cewar ta ai ba dawowa zata yi ba kayan gado ne. Kuɗin kuwa a cike aka bata dubu uku wai ta fara awarar a ƙofar gida kuma kullum ita take dafa awarar, ta yanka tun a gida a lissafa in ta kawo kuɗin da bai kai ba kuma taci uban ta da duka gashi ba wani isasshen abinci take ci ba shiyasa ta zama wata solo-solo kamar raƙuma.

Da yake kullum da asussuba take tashi in Bata tashi ba ma za'a zo a kwara mata ruwa. Tana cikin bacci taji ruwa a jikin ta....ba shiri ta miƙe, ko sallah ba'a barta tayi ba taji duka ta ko ina Suna dukan ta suna tsine mata. "shegiya karuwa jiya har da ƙin shigowa wato kin bi kwarton naki Koh!" Tana jhu suna ƙara bugun ta sai da taji jiki suka barta. A wurin ta sume baba AMARYA ta lalume ta ta kwashe kuɗinta.

Ta kwashe kusan awa guda tana kwance babu wanda ya damu da sumar ta ballantana su watsa mata ruwa. Sai da lokacin ɗaura girki yayi Baba amarya ta watso mata ruwa. Ajiyar zuciya Zahrah ta sauƙe yayin datake buɗe idanuwan ta da suka yi mata nauyi, gashi kuma bata jin ƙarfin jikin ta. Ganin ta farfaɗo yasa Baba AMARYA taka ƙafafuwan ta, babu shiri ta saki ƙara. "don ubanki waye zai yi girkin mayya kawai ki fito ki mana abinci" Cikin rawar murya Zahrah tace "ki....yi....haƙu...ƙi....ri...ba...nida.....lafiya...."

Wani sabon bugu baba AMARYA ta ke yiwa Zahrah ita kuwa bata da ko ƙarfin ihu daga ƙarshe ta ce lallai lallai ta fito tayi musu girki. Sai can da ƙyar Zahrah ta miƙa ta fito, ga wani irin jiri da take ji a haka tayi musu abincin.

Ko ɗanɗan ba'a bata ba wai tayi laifi kuma ta cinye kuɗin awara. Haka suka lamushe abun su. A daddafe Zahrah ta koma ɗakin ta tunawa da awarar jiya da ta ɓoye kamar ta san ba zata samu abinci ba tayi. Ɗauko ta tayi taci ko ruwa bata iya sha ba ta kwanta ...sallah kuwa yau ko asuba bata yi ba gashi la'asar ta kusa.

Bayan la'asar haka ta fita tayi musu girki tayi awara wanda kawai ƙarfin hali ne ammah sun riga da sun nakasa ta.

Bayan tayi wanka da ƙyar ta iya ɗauko ƙanzon da ta kankare na awara ta cinye shi gaya kamar mayya. Tana kuka tana hawaye har ta ɗan ɓigire tana bacci, Baba AMARYA ce ta zo ta canke ta da ƙafa a zabure Zahrah ta miƙe "don ubanki assrar waken zki min, ki fito ki fice da awarar" tana faɗin haka ta fice.

Zahrah bata samu fitowa ba don kuwa kanta wani irin juyawa yake....sai da ya ƙara wajen 40minutesa wajen, Baba AMARYA kuwa tunanin ta Zahrah ta fice da awarar don kuwa ta san bata mata magana biyu.

Lokaci ɗaya taji kanta ya yi wasai saboda haka ta fito sannan ta kwashi kayan suya.... Alhamdulillah yau da wuri ta sayar

ta dawo gida tana bawa Baba AMARYA kuɗin zata juya taji tace “akwai wankin kayan mu Ni da Bibalo yanzu ki zo ki wanke” Marairaice fuska tayi ko Baba AMARYA zata ji tausayin ta tace “don Allah Baba ki bari sai gobe da safe kinji, wallahi bani da lafiya” A hasale Baba AMARYA tace “mayya yau in asibiti ne kan ki sai kin yi wankin nan, shegiyar mai siffar aljanu.

Babu yadda ta iya ta juyo ga cikin ga sai ƙugi yake mata, yunwa kamar ta hallaka ta. Bayan Baba AMARYA ta shiga ciki Zahrah ta faki idon ta ta je wurin tukunyar da suka yi abinci. A hankali ta buɗe ta tsoma hannun ta, jin taliya ce yasa ta wawusa a baki kamar mayya, ta ƙara ciko hannun ta ta kai baki, sai da tacinye tass ta rufe a hankali ta zo ta haɗa ruwan wanki.

Tana cikin wanki Bibalo ta shigo, hara ta banka wa Zahrah yayin da ita kuma ta sunkuyar da kan ta ƙasa. Wankin ta take hankali kwance duk da kayan sun ci uban datti. Bibalo ce ta fito ta wullo mata pants ɗin ta wai ta wanke, a lokacin kuwa Zahrah bata san MEH ya faru da ita ba tace “in na wanke miki shegiya nake” ta faɗa babu alamar tsoro a fuskar ta.

Bibalo ta jima tana mamaki saboda iya sanin ta Bulebule yace ba zata taɓa yi musu musu ba ya mallaka musu zuciyar ta sai yadda suka yi da ita. A tsorace ta koma ta sanar da baba AMARYA, babu shiri su biyu suka fito a ɗan tsorace, saboda kuwa Bulebule yace ina dai asirin kan Zahrah ya warke to uwar ta ma zata warke, kuma aikin ba zai ƙara yiyuwa ba sai Bibalo ta aure shi. Abun da baba AMARYA ba zata taɓa yarda ba.

Hankali tashe suka nufi ɗakin mamah coz Zahrah ta bar wankin ta koma ɗaki abun ta. Wani haushi kanta take ji ta yaya aka yi har suke dukan ta suke azabtar da ita haka.... Toh wallahi sai tayi maganin su. Cikin ƙarfin hali da saddaƙarwa Baba AMARYA ta ce “ke fito ki ƙarasa wankin nan” Kallon da Zahrah ta aiko mata yasa ta zaro idanuwa ba shiri. Wani tsoron Zahrah ne ya ɗarsu cikin zuciyar ta. Babu shiri ta kamo hannun Bibalo suka taho ɗaki. Ita kanta Bibalo a tsorace take.

Ɓangaren Zahrah kuwa kuka ta saka bayan fitar su “kun cuce ni iyakar cuta....kun azabtar da ni, kun ɓatar da mahaifiya ta yayin da kuka kulle min baki har na kasa faɗa wa masu ɗaukar min mataki.....kun shiga tsakani na da karatu na....tun hana Ni cikar buri na....billahil Azeem bazan zauna da ku ba, zan tafi na barku da halin ku daga ku har Kawu bazan yafe muku ba.....yau ba gobe ba zan tafi kun ƙuntata rayuwa ta na tsawon shekaru biyu....kun bautar da ni kooooooooo. Tunda knce Mamah ta ta mutu bazata dawo ba yasa kika sayar da kayayyakin ta shikenan, Allah mafi sani in da gaske ne bazan yafe ba in kuma tana nan zan ci gaba da addu'ar Allah ya haɗa Ni da ita.

Haka Zahrah tayi ta surutai daga ƙarshe ta tashi tayi wanka ta rama sallolin ta ta kwanta. Safiya mai albarka Zahrah.

MUNA GAB DA SHIGA TAKUN ƘARSHE WANDA CIKIN SA NE LABARIN ZAI FARA, WANNAN DUK PROLOGUE NE! SHAFI BASU FI BIYU BANE SUKA RAGE, IN KIN SAN KINA BIBIYAR ALƘALAMIN DIAMOND LADY TOH KI ƘARA HIMMA DA COMMENTS, IN BAKI BI TOH KI FARA KADA AYI BABBAN GIDA BABU KE... COMMENTS SECTION GROUP DUK WACCE BATA CIKI TA SHIGA IN NAGA BA A COMMENTS BA ZAN YI POSTING PART TWO BA KUMA ZAN MAYAR DA SHI NA KUƊI....What I need is ur comments saboda ƙarfafa guiwa. DIAMOND LADY CE BHATOOL ADERM. [08/10, 11:58 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing   *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

PAGE 1 9

Dedicated to mah sister Shaheedah, I love u endlessly ƙanwa am.

Masu Neman labarin daga farko, ku danna wannan link ɗin sannan kuyi following

SHARE AND COMMENT PLEASE _____★★★_____

Ɓangaren Baba AMARYA da kuma Bibalo abun babu kanta kwana suka yi a zaune suna nemarwa kan su maslaha daga ƙarshe suka yanke tafiya gidan mata su bi ta kan Asabe ta raka su wurin wani bokan tunda Bulebule yace ina aikin ya ɓaci ba zai gyaru ba.

Asubar fari Bibalo ta ciro yan kuɗaɗen da take yafuta daga wurin Alhajin ta da sauran mazan da take mu'amala, daga nan basu tsaya ko ina sai gidan mata. Ko da suka SANARWA Asabe batun su bata Musa ba tace akwai boka na kan dutse, zata raka su kuma za'a dace sai a lokacin Baba AMARYA ta samu nutsuwa da sawaba.

★★★★★★

Ɗauke da addu'ar bacci a bakin ta ta farka, miƙa tayi kafin tayi ƙoƙarin tashi, tuno da abun da ya faru yasa Zahrah ta miƙe tare da goge hawayen da yake zuba a fuskar ta, alwala tayi sannan tayi sallah, kayan ta da yanzu suke a zube a tsakar ɗakin ta fara dubawa, gaba ɗaya babu nata wanda ta sani, “kenan sun daɗe suna mulka ta” ta faɗa cikin ranta. Ɓarin zuciyar ta ne ta Musa mata hakan tace A'ah Zahrah a haka bane, can ta yamutsa fuska tace “toh in ba haka bane yaya ne? Gashi duk kayan da Ammi ta bani duk da cewa sun daɗe ai ban kyautar su ba, toh ina suke?” ta ƙarasa tana birkito kayan.

Ganin hakan ba zai fisshe ta ba gashi har gari ya waye sai hargitsa kaya take yasa ta miƙe ta fito don nemar wa kanta abinci coz wata shegiyar yunwa take ji duk da cewa ta ci abinci ma jiya. Jin shiru a tsakar gidan yasa ta ɗan leƙa taga MEH shegun nan suke yi, zuwa dai-dai ɗakij Baba AMARYA tayi sai ta leƙa ammah bata ji motsi ba kuma babu alamun mutum, a hankali ta yi Bismillah tana takawa zuwa ɗakin....dube-dube ta fara can ta hango buhu da kuma waken suya, murmushi tayi tace “shegiya Baba AMARYA wallahi bazan bar miki shi ba gwanda ayi asarar shi da na baki” Barar da taji almajiri nayi yasa ta ƙwalla ƙiran “ya ka” Bayan Almajiri ya shigo taga kuma da girman shi yasa ta marairaice fuska tace “don Allah ka taimake Ni ka taimaki rayuwar ummah na tana kwance babu lafiya bamu da halin kai ta asibiti saboda Baba na ya rasu kuma ita je ɗawainiya damu. Fuskar almajirin ta nuna tsantsar rashin fahimta ganin hakan yasa Zahrah tace “ina so ka taimake Ni ne akwai waken suyar Umma mu siyar sai na kaita”

Yanda take marairaice fuska yasa tausayin ta ɗarsuwa cikin zuciyar sa, ba musu ya amince ya kwashi fiye da rabin buhu ita ma ta kwashe sauran suka fita, da yake lokacin awara na tashe yasa aka saye shi tas....kuɗin ya damƙa mata yace shi zai wuce ta shiga maƙwabta tasa su raka ummar tata kitso. Ɗari biyar ta bashi daga nan yayi mata sallama ta dawo. A lokacin da zata shiga gida ta tuna da jakar da Mamah ta bata ta barta gidan su Badi'a, gashi kuma ta riga ta yanke shawarar su ma ba zasu ƙara sanya ta cikin idanuwan su ba har sai ta nemo Mamah, coz in SUKA ganta duka da cewa an raba tsakanin su ba zasu bar ta ta tafi Abuja ba. Tana tunawa da cewa irin lokacin nan Ammi bacci take, Badi'a na school yasa ta dumfari gidan.

A hankali take takawa tamkar wata ɓarauniya har ta iso bakin part ɗin Ammi jin babu alamun motsi yasa ta ƙara lallaɓawa ta sanya kan ta ciki, tana shiga siɗif suɗif kamar ƙadangare haka take bin bango har ta isa ɗakin Badi'a.

Maimakon ta shiga ɗakin ta ɗauki abun da take so sai ta tsaya tana kallon curtains ɗin dake cikin ƙofar. “Allah sarki Aminiya ta masoyiya ta, yanzu shikenan daga, duk rayuwar mu ta baya ta zama tarihi, ga Abba da ya kula da rayuwa ta na wani dogon lokaci ba tare da ya banbanta Ni da yar cikin sa ba, yayi wa rayuwa ta da ta mahaifiya ta hidima shima haka ya zama tarihi, Ammi, Allah sarki Ammi na...kin so ni fiye da yadda kika so yar cikin ki, ki kan bani zaɓi a kowanne lokaci kafin ki bawa ɗiyar ki.

Dole zan bar rayuwar ku bari na wani dogon lokaci har zuwa lokacin da Mamah ta zata bayyana, oh! Har zuwa lokacin da zan cika buri na. Fata na da addu'a ta gare ku Allah ya saka muku da gidan aljanna, ya kula da ku fiye da yadda kuka kulani” Shesshekar kukan da Ammi taji yasa ta farka daga bacci, ƙoƙarin tashi ta fara yi coz ba lafiya gare ta ba kwanan nan, a hankali ta dumfaro parlour saboda tana son ta ɗan haɗa tea.

Motsin da Zahrah taji ne yasa tayi gaggawar ƙulewa ɗakin wanda yayi daidai da fitowar Ammi kuma taga wulgawar abu. A tsorace ta biyo direction na wurin da taga wulgawar abu. Zahrah kuwa tuni ta faɗa toilet ta, Bata yi ƙoƙarin locking ba ta maƙale can bayan ƙafa. Har ɗakin sau da Ammi ta shiga Bara fata kowa ba hakan yasa tayi la'akari da cewa idanuwan

ta ke yi mata zato.

Jin ta fita yasa Zahrah sauƙe wata wawuyar ajiyar zuciya ta sauƙe kafin tafito daga toilet, a hankali ta ɗauko sidedrawer ta ajiye sannan ta ɗale dogon wardrobe ɗin dake ɗakin, bata sha wahala ba ta janyo jakar.... hawayen fuskar ta ta goge sannan ta diro dummmmm kake ji. Jin sauti ya fito yasa tayi saurin miƙewa ta mayar da drawer tana ajiyewa ta koma toilet jin takun ƙafar da ta tabbatar Ammi ce kuma ƙarar nan ne ya sa tazo dubawa, stilll irin duban ɗazu tayi daga nan ta koma bedroom ɗin ta.

Sai da Zahrah ta tabbatar Ammi ta shiga room ɗin ta yasa ta fito a hankali tana leƙen Ammi ta jikin curtains, ganin Ammi Bara parlourn yasa Zahrah fitowa a hankali ta bar part ɗin, haka ta lallaɓa da sauri ta fice a gidan. Wata ajiyar zuciya ta sauƙe ganin ta haye wannan siraɗin.

Da sauri ta koma gida still su Baba AMARYA basa nan, ɗakin ta ta ƙara shiga tana bincike, ganin jakar ƴan gayu (Trolley) yasa ta juye kayan ciki a ƙasa taje ta jera nata, ta ƙara dawowa tana bincika wa har ta samu wasu kuɗaɗen ta kwashe tasss duk da ba masu yawa bane, har zata fita tayi tozali da kular abinci. A wurin ta zauna ta cinye shi tass daga nan ta fita. Ko wanka bata yi ba ta ɗauki wani Coffee brown hijab ɗin ta wanda ya amshi kyakkyawar farar fuskar ta. Janyo Trolleyn tayi yayin da gaban ta ke dukan tara-tara. Bata ɓata lokaci ba ta tari mai adaidaita har tasha ya kai ta daga nan ta shiga ta zauna, mutum biyun da suka rage suma shuka shiga daga nan na juyo dan ɗauko report kan su Baba AMARYA..

Sai da suka yi tafiya mai ɗan karen nisa cikin wannan dajin kafin su fara hango wani ɗan ginin ƙasa, kasancewar duk ƙwarin guiwar su a halin yanzu ya ta'allaka ne ƙara shirya wani tuggun yasa suka saki dariyar cin nasara a tare. Suna isa wurin ginin suka ƙule, kwane-kwane suka yi kafin su miƙe wata doguwar siririyar hanya. Sai da suka yi tafiya mai ɗan nisa suka dakata bisa umarnin da suka ji ba tare da ganin kowa ba. “ku dakata da tafiya!” Muryar ta faɗa a kausashe. Kafin daga bisani suji ance “kowacce ta rufe idanuwan ta!” da sauri kuwa suka rufe. Suna rufewa basu ƙara sanin inda suke ba saboda wata fitinanniyar guguwa mai ɗan banzan duhu da hargagi ta mamaye wurin. “ku buɗe idanun ku!” wata murya apart from waccan ta faɗa. Suna buɗe ido suka yi arba da wanni mummunan mutum wanda bashi da daɗin gani kana ganin shi ka ga typical boka, ga wasu zungura-zunguran ƙahon shi guda biyu.

Dariya bakan ya kece da ita yana faɗin “Tun da sassafe aka nuna min tahowar ku waje na ammah baku iso ba sai yanzu hhhhhhh.....hhhhh" zazzare idanuwa suka yi cike da tsoro, suna mamaki ashe duk hatsabibancin Bulebule bai kai na kan dutse ba Katse musu tunanin yayi da faɗin “ku daina mamaki, ke Saudatu kin zo ne saboda ɗiyar mijin ki wacce a halin yanzu shirin barin gidan take yi, na duba madubin tsafi ammah bai nuna min ainihin inda zata je ba ammah a halin yanzu asiri ba zai yi tasiri a jikin ta ba saboda shaiɗanun da ke kanta sun hasala ba zasu bari a cutar da ita ba”

Shiru Baba AMARYA tayi tana zaro idanuwa cikin ranta tace “shikenan ta faru ta ƙare, yanzu mayyar yarinyar nan sai da ta ɓata aikin nan” Asabe ce ta katse shirun da cewa “toh mai girma na kan dutse ya batun uwar yarinyar kumah?” “hhhh....hhhhhhh.....wai Madinah kuke nufi?” Kai suka gyaɗa, ƙara duba madubin tsafin shi yayi kafin ya ɗago ya kalle su yace “hh...hhhhhhh.....hhhhh Madina,” juyo da madubin tsafin yayi gaban su. Ido suka zuba kai tare da waro idon

Mamah ce zaune a wani hamshaƙin parlour ga kuma wata babbar mace a gefen ta dai wani dattijo a kujerar dake facing ɗin tasu. Fuskar ta a marairaice tana jijjiga kai alamun bata don abun da ake yi.

Ɗauke madubin tsafin yayi ya fuskance su, in a serious tone yace “kuna ji koh, abun da kuka gani gaskiya ne...yanzu haka Madina tana can Kaduna gidan wasu mutane wanda suka kaɗe ta wata rana kan titi, da suka fahimci ba tada hankali yasa suka tafi da ita suna mata magani, sai dai babban sihiri aka yi mata, kuma makarin sa ɗaya” Ƙara maida hankalinsu gare suka yi alamar suna son sani “makarin ba komai bane face ƴar ta, tana haɗuwa da ita asirin zai karye ya rage naku ku san abun yi”

Yana faɗan haka ya murtuƙe fuska. Baba AMARYA ta marairaice fuska yana haɗa hannayen ta biyu “ranka shi daɗe ka taimake ni bana don sihirin ya lalace ko dan saboda mijin da na aura, boka Bulebule yace da zarar asirin da aka yi wa matar ya karye to na jikin sa ma zai karye gashi dama can asiri nayi masa ya aure ni idan ya dawo hankalin sa yaga ba

Madina na shiga uku...” Tsawa boka ya daka mata nan da nan jikin ta ya hau ɓariiii “abu ɗaya zan miki ya rage naki ko ki biya ko a'a, in kin amince toh” Cikin rawar murya Baba AMARYA tace “eh” “zan hana haɗuwar yɑr da uwar ta hanyar tura mata aljanun da zasu ƙara mantar da ita uwar, ladan aiki na shine....” ya faɗa yana pointing Bibalo da yatsa, fara rarraba ido tayi tana jiran taji meh baba AMARYA zata yanke kwatsam taji Baba AMARYA tace “shi....shi....shi...shike...nan na amince” ta faɗa a rarrabe tana mai kallon Bibalo da fuskar roƙo.

Nan Bibalo fah taƙi Amincewa, a rasa wa zai sadu da ita sai wannan mummunan ƙazamij mutum ɗin toh wallahi da wannan ya kasance ta gwara kare ya kasance ta. Tab.

Tasawar da boka ya daka ne yasa suka nutsu “keeeeee.... Har kin isa nace ina son jikik ki ki ƙi, kin ma ci Sa'a sai da na tambaya, toh ko kina so baki so sai nayi abun da nayi niyya dake” yana kai haka ya miƙe zai yi kanta, da gudu Bibalo ta arta a na kare ko taku biyar bata yi ba taji an cafke ta. Boka ne da kan shi ya cafke ta, kai tsaye ya nufi wani ɗaki da ita.

Tunda ya kaita ya ajiye ta daga nan ya zare abun da ya naɗe jikin sa da shi take ainihin suffar shi ta bayyana Abu dai babu daɗin gani a take duk ta bi ta firgice.

4Hours ya shafe yana aiki kan ta har sai da yaji shi zam yayi wani irin gurnanin a lokacin wata guguwa ta tashi da farko guguwar mugun duhu gare ta, kafin wani lokaci ta fara raguwa har haske ya bayyana.

Ɓangaren su Baba AMARYA tunda suka ga boka ya shiga da ita suka tabbatar sai yayi, saboda haka suka dawo baƙin ƙofar ɗakin suka tsaya. Ganin tsayuwar ba inda zata kai su yasa suka nemi wuri suka zauna.....hour 4 nan a wurin tayi musu har aka fara guguwa wacce tunda ta tashi suka rasa hankalin su. Bayan komai ya sarara hankalin su ya dawo ammah abun mamaki sai suka gansu a bakin titi.

Jimamin da suka tsaya yi ne har sai da suka waiwyo ta bayan su, a take Baba AMARYA ta cilla ihu ta faɗi ƙasa sume.....

Ba komai bane sai Bibalo da suka gani yashe tana numfashi sama sama ga uban jinin da yake malale a wurin da take kwance. Asabe kuwa duk ta ruɗe ta rasa wa zata fara ceto wa. Nufar wurin da Bibalo take tayi, idanuwan ta ta zare tare da sakin ajiyar zuciya. Irin wannan cin mutuncin ƙamar wanda maza 100 ɗari ne suka yi aiki a kan ta! Murmushi tayi tace “ko ba komai na fara cin nasara a kan su, shegu miyagu” Daga haka ta juyo wurin da Baba AMARYA take ta fara danna ƙirjij ta, a hankali ta saki ajiyar zuciya sannan ta buɗe munafikan idanuwan ta.

“saude bamu da lokaci ki tashi mu ɗauki Bibalo mu yi asibiti tunda akwai kuɗi a gun ki Jada mu rasa ta.” Da ƙyar Baba AMARYA ta miƙe suka nufi wurin da Bibalo take a kwance suka cicciɓo ta, jinin jikin ta duk ya ɓata musu kaya, a haka suka tafi har suka fara isa cikin jama'ah, duk wanda yasan su sai ya sa ta kare, kowa suka yi wa magana kafin ya gama ji in ya kalli abun da ke hannun su sai ya cika wandon shi da iska, tunanin mutane ko kashe matar suka yi.

__Kuyi min comments yɑn albarka gobe sai mu ci gaba.__ YA KUKE TUNANI ZA AYI? ALLAH SARKI BIBALO YAU AN WAHALA KO MUTUW TAYI DA GASKE? AIKIN BOKA A TUNANIN KU ZAI CI? TEAM ZAHRA KO ZAKU YI MATA RAKIYA NE? Duk cikin littafin babban gida (PROLOGUE) saura post ɗaya mu shiga book two Wanda shine ainihin labarin...kada ayi babu ku. [10/10, 5:51 a.m.] Diamond Bhatool : _____★★★_____ Typing *A BABBAN GIDA* _(All in a big family)_ ★TAKUN FARKO★ _[Labari/Rubutawa]_ *©Fadimatu Adamu Hassan* *A.K.A DIAMOND BHATOOL* _____★★★_____

PROLOGUE

*PAGE 20 (LAST PAGE)

I dedicated this page to u Boɗɗi Autar Ammi, the writer of _MAYU NE_, Allah ya ƙaro hazaƙa yɑr uwah.

Masu Neman labarin daga farko, kuyi following channel ɗin nan zaku samu:

SHARE AND COMMENT PLEASE _____★★★_____

Har bayan la'sar babu wanda ya kula su in fact kowa ta kan shi yake yi in ya can su. Can dai har suka isa wani asibiti bayan sun ci uwar tafiya. Babq amarya kuka Asabe kuka, Da ƙyar aka amshi Bibalo saboda case ɗin ta yayi muni da yawa. Hour uku suka share kafin a samu ta farfaɗo. Tun da ta farfaɗo take ta uban sunbatu kamar mahaukaciya

“aah boka, ka rabu da Ni don Allah wallahi iya Alhaji na nake alaƙa da shi kada ka ɓata tsakanin mu, wayyoh wayyoh Baba ta duk ke kika jawo min, ka ƙyale Ni haka babu daɗi wallahi ka barni zan mutu. Wayyoooh”

Nurses ne suka yi kanta ganin irin yadda take jijjiga kamar wata psychiatric patient. Da ƙyar suka maka mata pentazocine injection bayan danne ta da aka yi. Nan bacci yayi awun gaba da ita.

★★★★★★★★

Tunda ta shiga motar ta kifa kanta bisa cinyar ta tana kuka, tun iya hawaye ke zuba har ta fara kuka mai sauti. Babu abunda ke tashi sai shesshekar kukan ta. Cikin motar kuwa babu wanda yayi mata magana sai ma wata dake seat ɗin baya da ke jera uban tsaki alamun kukan na damun ta. Matar da ke gefen Zahrah wadda ba zata wuce sa'ar Mamah ba ta ƙare mata duba kafin ta ɗaura hannun ta a bayan ta tana ɗan bugawa alamar rarrashin tace “yan mata kiyi haƙuri ki daina kukan nan ko ma meyeh aka yi miki ki fauwala wa Ubangiji al'amarin ki shi zai yaye miki ba kuka ba”

Haka matar tayi ta bawa Zahrah baki har tayi shiru tana sauƙe ajiyar zuciya.. Bayan tayi shiru matar take tambayar ta ina zata je tace mata Abuja, murmushi tayi tace “nimah can zan je ammah wace unguwar zaki je?” Jimm Zahrah tayi kafin tace “nimah ban san yadda na dosa ba tukun na” Cike da tausayawa matar ta ke kallon Zahrah coz tunda suka shigo taji tana ƙaunar ta uwa uba kuma fahimtar akwai damuwa a tattare da ita yasa ta ƙara jin Zahrah a jikin ta.

“yaya sunan ki?” matar ta tambayi Zahrah “zahrah” kawai tace Murmushi matar tayi ta ce “in babu damuwa ki ƙira Ni Mamah, naga kina cikin damuwa sosai, kada ki damu in munje sai ki sauƙa gida na kin yadda” Gyaɗa kan ta tayi tana jin farin ciki ganin yadda matar ta nuna kulawar ta a kan ta.

Har suka isa Kaduna matar ke siya musu abu idan sun tsaya shan mai. A haka har bacci ya ɗauke ta.

Tana farkawa lokacin suka shigo Abuja, sannu matar tayi wa Zahrah. Bayan an sauƙewa kowa kayan sa suka tari taxi har gidan matar dake a Gwagwalada. Ba laifi gidan da kyan shi, bayan sun shiga Zahrah tayi wanka umma (Aunty) Kamar yadda Zahrah ta ƙira sunan ta girka musu abinci bayan sun ci ta raka Zahrah guest room daga nan baccin gajiya ya ɗauke ta.

★★★★★★ Washegari aka sallamo su Bibalo suka samu motar da zata kawo su gida, bayan sun dawo a nan aka fara yiwa Bibalo sabuwar jinya ɗin kuwa ƙarfi da yaji ta zama mahaukaciyar dole, Baba AMARYA kuwa hankalin ta ya koma kan Bibalo yada bata damu da ɗauko zancen bokan ba.

Ɓangaren Zahrah da safe tayi sallah tayi wanka sannan ta ɗauki ɗaya daga cikin kodaɗɗun atamfofin ta ta saka, fuskar ta fayau ta fito parlourn, a lokacin Aunty har ta gama breakfast, bayan sun yi breakfast Aunty ta tambayi Zahrah meyeh damuwar ta, bata ɓoye mata komai ba saboda tana buƙatar mai tallafa mata. Aunty ta yi kuka da jin irin rayuwar da Zahrah tayi daga nan ta yi addu'a Allah ya bayyana Mamah. Kuma tayi alƙawarin zata taimaka mata har ta isa zuwa ABATCHA FAMILY tunda ta san ESTATE ɗin sai dai burin ta Allah ya sa a bar su su shiga.

LA'ASAR sakaliya suka fita bayan sun tari taxi suka nufi ABATCHA ESTATE. Tun daga round out ɗin da zai sada ka da ESTATE ɗin Zahrah dake ɗauki zuwa zuciyar ta ta fara bugawa coz Bata yi tunanin sanuwar dangin Mamah haka ba.

Daidai makeken gate ɗin ABATCHA ESTATE Wanda gefen shi ke ɗauke da wani signboard Mai ƙyalƙyali an rubuta “WELCOME TO ABATCHA ESTATE”. Bayan sun sauƙa Aunty ta have hannun Zahrah zuwa bakin gate ɗin, a hankali ta bita yayin da zuciyar ta karye tana wani irin bugu, ji take yi kamar ta koma coz wannan mansion bai dace da rayuwar ta ba.

Suna dumfaro gate ɗin Guards suka yi kansu suna tambayar lafiya. Aunty tace “lafiya munzo wurin masu gidan ne” Kallon baki da hankali suka yi musu kafin wani baƙi daga cikin su ya ce “kai dallah ku bar wurin nan bana son iskanci in

kun ƙi kuma toh yanzu zan harbe ku.

A tsorace Zahrah ta ja hannun Aunty zasu juya Aunty ta jijjiga mats Kai alamun A'ah kada ta sare tun yanzu. Juyawar su yayi daidai da fitowar wani tsoho wanda shima da gani ma'aikaci ne a ESTATE ɗin, duk da alamun tsufa da suka bayyana a tare da shi bai hana shi ƙura ma Zahrah ido ba, cikin ransa kuwa cewa yake “madina?, Aah ita ai ance ta mutu to in ma ita ce sai yanzu sai dai ace ta haifi ya wannan” Juyawa yayi ganin irin hararar da Zahrah ke aiko mishi coz ta gaji da kallon da yake banko nata.

Sunyi sunyi Guards ɗin su bar su su shiga ammah inaaaah sun ƙi, daga ƙarshe suka fafaro su da gudu, babu arziki Zahrah da Aunty suka koma.

Washegari suka ƙara komawa but jiya iyau, har sai da suka bugi Zahrah coz ta fara yi musu rashin kunya, har mamaki suke ga ta ƙazama yar ƙauye ammah ta san salon iskanci. Haƙuri Zahrah ta bawa Aunty tace mata ba sai ta ƙara rako ta ba har zuwa ranar da zasu bar ta ta shiga.

Sati guda Zahrah tayi tana zuwa ABATCHA ESTATE ammah ba a barin ta har Guards sun fara tunanin mayya ce.

Ranar da tayi zuwan ta na sati ne ta ɓarke musu da hauka kan lallai su barta ta shiga in ba haka ba wallahi sai ta hukunta su. Duk abun da ake yi a kunnen wannan tsohon shi dai ya kasa daina mamaki yarinya sak Madina da ta bar gida yanzu kusan tsawon shekaru goma sha takwas. Ana cikin wannan drama wata arniyar mota ta dumfaro gare ɗin Babban gida. Tun kafin ta ƙaraso wani guard ya jawo Zahrah da ke tsaye tsakiyar titi yana mai cilla ta gefe. A harzuƙe ta tashi tana faɗin “Allah ya isa na Mugu kawai, wallahi duk ranar da aka barni na shiga gidan nan sai kayo da na sanin abun da kuka yi min” Caraf a kunnen Dattijon dake cikin motar wanda tun lokacin da yarinyar ta faɗi ƙasa yaji zuciyar sa ta buga, hakan yasa yayi wa driver umarni kan yayi parking bayan ya sauƙe glass ɗin motar ne yaji abun da tace. Cike da izza mutumin ya fito bayan driver ya buɗe mishi ƙofa, bai kuka Guards ɗin ba ya kamo hannun Zahrah wacce ta kusa mutuwa saboda mamakin yadda Dattijon ke kama da Mamahn ta. Katse mata tunani yayi da faɗin “yan mata wurin wa kika zo ne, ko kin zo neman aiki ne?” Jijjiga kan ta tayi tace “aah nazo wurin Hajjaty ne sati guda yau i a zuwa sun hana Ni shiga don Allah kayi musu magana uncle”

Uncle ɗin da ta ambata yada zuciyar shi bugawa, ba tare da ya kalli fuskar ta ba ta ce ta shiga motar, nan jikin Guards yayi sanyi suna tsoron kada yar nan tayi musu gwaiba. Tafiya mai tsawo suka yi yayin da hankalin Zahrah yake kan manya manyan Mansions dake cikin babban guda, cikin zuciyar ta kuwa tunani take

“anya zan samu matsuguni a wannan aljannar kuwa?, Dubi gidaje kamar ba za'a mutu ba! Lallai Mamah tayi sakacin barin ahalin ta in dai kuwa ta tabbata nan ɗin ne”

Goge hawayen fuskar ta tayi yayin da Dattijon hankalin shi baya kan ta gabaɗaya ya sauƙe ajiyar zuciya.

Lallai duniya tana yadda take, duk yadda kake tunanin guda na alfarma toh kazo ESTATE ɗin nan sai kaji tsoro, gashi Mansions sun kai Ashirin a cikin ESTATE ɗin, parking lots baa magana kuma kowanne danƙare yake da mitoci, motocin ma waɗanda ido ba lallai ya taɓa gani ba.

Wani ƙarin mosque suka wuce wanda shima ginin shi ya tafi da zuciyar Zahrah daga nan suka yanki titin da zai sada ka da Babban Mansion. Bayan driver yayi parking PA ɗin Dattijon ya buɗe mishi ƙofa, a hankali ta fito yana yiwa Zahrah alamar ta fito, gyara riƙon bag ɗin ta tayi tana fitowa.

Dattijon ne ya ƙara kama hannun ta suka nufi cikin wannan daula, Zahrah dai baki kawai ta sake, lallai duk wayewar ka ina ka zo nan sai kayi ƙauyanci. Faɗin haɗuwar wannan parlour ma ɓata lokaci ne but kuyi assuming a ranku yadda zai kasance, bayan haɗawa irin ta parlourn, wani sihirtaccen ƙamshi ne da kuma sanyin AC ke tashi, nan da nan jikin Zahrah ma yayi sanyi.

Zaunar da ita yayi a parlourn ganin Hajjaty bata nan yasa shima ya zauna ɗin jiran fitowar ta, don kuwa ƙa'idar su ce haka in dai Hajjaty bata parlour sai dai ka tafi ko kuma ka jira ta, ko kaɗan ba sa so a takura wa tsohuwar.

Fitowar Laraba daga kitchen ne yasa ya miƙa kallon shi ga hanyar kitchen ɗin, sunkuyar da kai Laraba tayi saboda girmamawa, gashi dai gulma na cin ta ganin wannan dirty creature ɗin gefen Alhaji Umar kuma wai a parlourn Hajjaty tunani take wai dama Hajjaty suna da dangi talakawa ne?

Katse mata tunani yayi yace “Ki kawo mata refreshments, Babu musu Laraba ta juya ta kwaso snacks da drinks a kan tray, gaban Zahrah ta ajiye har zata wuce taji Muryar sa “ki ƙira Hajjaty in ba bacci take yi ba” Kai ta gyaɗa sannan ta wuce wata hanya wacce zata sada ka da bedroom ɗin Hajjaty. Ita kuwa Zahrah mamaki ne ya cika ta ganin har yanzu mutumin ko kyakkyawan kallo bai yi mata ba balle ya gano ita ɗin jinin sa ne ga kuma uban refreshments dake gaban ta wai duk ɗin ita aka kawo.

A hankali ta ɗauki cake da hannu bata ko bi takan spoon.s da knives ɗin da ke gaban ta ba. Ta gutsiri na farko taji wani daɗi ya ziyarce ta, tana kai na biyu taji takun mutum hakan yasa ta dakata da cin cake ɗin.

Hajjaty ce sai kuma Laraba a bayan ta, kyakkyawar tsohuwa ce fara sol da ita, tana da mulmulallen jiki irin na tsofin da ake ƙira *bakwa tsufa*, sanye take cikin shigar ta ta alfarma, riga da zani ne ɗas a jikin ta, tunda ta fito idon Zahrah ke akan ta! Abun mamaki kana ganin ta kaga Mamah zaka tabbatar daga jikin ta ta fito, kamar su ɗaya sak, tsufar ce kawai banbanci sai kuma Hajjaty da a yanzu ta fi Mamah hasken fata.

Sai da ta kusa ƙarasowa idon ta ya sauƙa akan ɣar matashiyar da ke gefen yaron ta Umar, ɗagowar Zahrah da ta sunkuyar da kai yasa suka haɗa ido da Hajjaty, lokaci ɗaya zukstsn su suka buga dummmmm, Hajjaty ce tayi ƙarfin halin zaro idanuwan ta tana furta

“Maaa..ma...dii...diiiiiiiiii...diiiina...ceeee” Daga haka ta faɗi sume.

ALHAMDULILLAH, NAN NA KAWO ƘARSHEN TAKUN FARKO NA LITTAFIN A BABBAN GIDA Takun farko, ina riƙon Allah ya bamu ikon amfana da abubuwa masu muhimmanci daga ciki ya kuma yafe mana kurakurai da na tafka ciki. In Sha Allahu nan ba da jimawa ba zan sake muku littafi na biyu wanda shine ainihin cikin labarin. Ku ci gaba da kasancewa da ni don jin yadda littafin zai kasance. Na gode muku sosai Allah ya bar ƙauna. FADIMATU ADAM HASSAN DIAMOND BHATOOL DIAMOND LADY OUM ZAINAB duk nice.....ki ci gaba da BIBIYAR ALƘALAMIN DIAMOND LADY, na gode. ASSALAMU ALAIKUM WARAHMATULLAH WABARAKATOUH

Soyayyanovels